[9/27, 09:36] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD* ✍🏻

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Dasunan Allah me rahama me jin k'ai , tsira da aminci su k'ara tabbata ga Shagaba Annabi Muhammad S.A.W ,_

_Wannan littafin nawa k'agaggene banyishi dan cin zarafin wata ko wani ba , duk wanda yayi dai dai da rayuwarsa to yazo ne a kasi , banyadda wani ko wata ya juyamin labarina ba batare da izinina ba , Yin hakan doka ce Akiyaye_🤝🏻🤝🏻

_Wannan littafin sadaukarwa ne gareki Masoyiya🥰 Hafsat Abdurrahman_ *Allah yabar k'auna* 🙏🏻🙏🏻🤝🏻

Chapter 1.

A garin Abuja yau antashi da ruwan sama kamar da bakin k'warya , hakan yasa garin yayi tsit kowa yana cikin gidan sa , wani katafaren gida nagani ana wangale k'ofar gate d'insa , wata motar ce ta danno kai da gudun tsiya tamkar zata tashi sama saboda gudu .....
baka hango wanda ke cikin motar saboda bak'in glass d'in dake jikinta , amman kasan duk wanda ke cikin motar basai anfad'a maka irin rashin jin shiba , saboda irin gudun dayake sharawa ga kuma wani kid'a na tashi tamkar dodon kunnen mutane zai tsage , a k'ofar wani katafaren gida motar ta tsaya ta danna hon. Da gudu megadi yazo ya bud'e dan yasan waye ko ba'afad'a masa ba , da gudu motar ta kuma shiga cikin wannan gidan kuma har a lokacin ba adaina ruwa ba , anfi minty biyar ba'a fito daga ciki ba sannan aka bud'e murfi aka fara zuro k'afa , wata had'addiyar Budurwace wacce tagaji da had'uwa ta fito daga cikin motar sanye da glass a idonta , ga wasu matsatstsun kaya datasa duk ilahirin jikinta a matse yake , takalmin

dake k'afarta irin hill d'in nan ne ,  tana fitowa me gadi ya k'araso da gudunsa yana zubewa gabanta yana fad'in " sannunki da zuwa ranki shi dad'e  Hajjaju mutan makka da madina , ko kallon arzik'i batayi masa ba ta wurga masa lemar data d'auko bayan motar ta , da sauri ya mik'e yana bud'e lemar tare da rik'e mata dai dai kanta  gudun kar ruwa yatab'ata ,  shigewa tayi tana wani irin taku tamkar wahainiya har suka k'araso k'ofar wani had'add'en falor ,  shigewa tayi ciki shikuma me gadi ya tsaya a wajen saboda bin umarninta......

Tana shiga cikin falor tasamu 'Yan aikin gidan sai faman gyare gyare suke a falor , suna ganinta dukansu suka zube k'asa suna gaidata , kallo basu isheta ba bare ta amsa musu ,  step tafara hawa alamun sama zata hau , saida ta haye saman sannan dukan su suka mik'e suna girgiza kai kafin suci gaba da aikin gabansu......

Wani d'aki naga tashiga ko sallama batayi ba ,  wani Magidancin mutum ne a zaune yana danna cumputer lapton akan wani katafaren gado , sai kuma wata mata wacce ke had'a masa cofee a gefensa , kana ganinta kasan matar sace saboda yadda suke hirarsu cikin farin ciki da raha  , jin anshigo yasa dukansu suka dubi k'ofah dan ganin waye ?  koda suka ganta Mutum yafara fara'a yana fad'in oyoyo My luv , zonan naji waya tab'amin ke naga sai had'e rai kike ?  Hajiya Maimuna tadubeshi tace " Alhaji nagama aikina zan'iya tafiya ?  dubanta yayi tare da canza fuska yace " Haba Maimuna wai meyasa duk lokacin da *SANAM* zatazo sai kin bar wajen ?  Hajiya Maimuna tace " kafi kowa sanin halin 'yarka batason kowa ya rab'eka mutuk'ar ba ita bace , dan haka duk lokacin data tafi zaka iya kirana inyi maka duk abinda kakeso , bata jira cewar saba tayi hanyar fita tafice abinta.......

Sanam ta rakata da Hara sannan tayi tsaki taci gaba da taunar cingum d'in ta , Alhaji Abba yadubi tilon 'yartasa wacce yake mutuk'ar k'auna a duniya kuma akanta zai iya yin komai mutuk'ar za'atab'a masa ita yace " Sorry my luv k'yaleta kar ranki ya b'aci akanta , Sanam tayi wani k'wai da cingum d'inta har saida yatab'o hancinta tace " Daddy nazo ne akan maganar canzamin motar , kasan cikin account d'ina kwata kwata bakai adadin kud'in dana ke buk'ata ba , duk wannan maganar da Sanam takeyi a Shagwab'e takeyinta tamkar K'aramar yarinya , dubanta yayi yace " My luv ina ganin fa motar nan taki kwata kwata batafi kwana goma ba , kuma ace har ank'ara siyan wata , da bari kikayi wannan ta kwana biyu sai insa ayi miki order wata daga Jamus ,  had'e rai tayi sannan tace " Daddy yanzu kana so muyi anko motar da Zahra ne ? itama fa daga ganin wannan tawa tasa Daddyn ta yasiya mata irinta , nikuma gaskiya bazan dunga hawa motar iri d'aya da wata ba saboda banson Ajina ya zube , Murmushi yayi yana dubanta sannan yace " to shikenan nawa ne kud'in waccen motar d'in ?  wani murmushi tayi wanda har sai da dimple d'inta ya lotsa tace " 50.Million ce kawai Daddyna , murmushi yayi yace " indai akwai ta sama da haka ni ita nakeso nasiya miki My luv , tashi tayi da sauri ta fad'a jikinsa ta rungumesa tana murna , ganin ta a farin ciki yafi masa komai a duniya , shima samun kansa yayi da farin ciki sannan ya sumbaci goshinta , Nan yatura mata 80.Million a accaunt d'inta yana fad'in " sai munzo celebrition my luv ,  ta shagwab'e fuska tare da manna masa kiss a kunci tace " thanks my special papa proud of U My Daddy , da sauri ta d'auki jakarta tajuya ta fice daga cikin d'akin ,..

Lokacin da ta sauko sukayi karo da Hajiya Maimuna , Sanam wani dogon tsaki taja tare da tsartar da miyau tana bin gefe harta fice daga falor , wannan Abun datayi wa Hajiya Maimuna ba k'aramin harzuk'ata yayi ba , taya yarinya k'arama zata dunga yi mata wannan abu ? tabbas wannan hali na Sanam yafara damunta zata iya ci gaba da zama da Alhaji Abba kuwa ? Sama ta nufa wajen sa ranta a mutuk'ar b'ace , tana shiga d'akin nasa ko sallama batayi ba tafara fad'in " a gaskiya Alhaji nagaji sosai da halin wannan 'Yar taka , a koda yaushe tazo gidan nan saita yimin abinda zuciyata zatayi min rashin dad'i , yau saboda iskancinta har miyau ta tsartamin dashi haba Alhaji , idan anyi magana sai kace ana takura mata ansa mata ido , a gaskiya indai zamu ci gaba da tafiya akan haka tabbas zanbar maka gidan ka dan hak'urina yafara kaiwa k'arshe , a fusace Alhaji Abba ya mik'e yana kallon Hajiya Maimuna yace " nasan dama dole sai kinzomin da wata sabuwar magana akan zuwan Sanam gidan nan , Maimuna ina d'aga miki k'afa sosai aka Sanam saboda wani Abu , amman duk randa kika isheni wallahi zaki gane waye ni , tsaki yaja tare da d'aukar mukullin motar sa yafito ......

Hajiya Maimuna tuni hawaye ya wanke mata idanuwa , fad'awa kan gado tayi tana kuka tare da fad'in " yaushe ne matsala ta zata kawo k'arshe a kan wannan yarinya ? yaushe ne zanyi zaman farin ciki a gidana koda yaushe indai zata kawo ziyara to tabbas sai tabar mata tabo , lallai hausawa sunyi gaskiya da suke cewa *'Yar kishiya rik'on me hak'uri* Allah yabasu ikon cinye jarrabawar nan......

Koda Sanam ta fito har a lokacin megadi na tsaye ruwa yayi masa duka , ga lema a hannunsa amman yasan indai yasake yashiga cikinta to tabbas yagamu da jaraba , tana fitowa yayi saurin bud'e lemar yana rufa mata aka suka wuce har gun motar ta , tana shiga ya nad'e lemar yasa mata ita a bayan motar tare da kwasa da gudu yayi wajen gate. Bud'e wa yayi tazo ta fice da mahaukacin gudunta tamkar zata tashi sama , gudu take sosai titi ko wanne me motar matsawa yakeyi inyaganta , tana shiga estet d'in Airea 11 dai dai wani k'ofar gida wani matsahin saurayi ya fito a k'afa sanye da jallabiya jikinsa , kana ganinsa kasan sauri yake yasamu sallar Azzahar ta wanke sa da ruwan cab'i dukansa , kuma ta fiki motar ta tamkar batasan abinda tayi ba..............

*Comment* *d'inku* *shine* *zai tabbatar min da karb'uwar da littafin zaiyi*

*Dafatan wannan salon shima zai k'ayatar daku*

Kardai kumanta Alk'alimin *'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ ✍🏻😍🌹

[9/27, 09:36] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*

_Rik'on_ _Me_ _Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 2.

Bin motar yayi da kallo har ta k'ure sannan yadubi jikinsa , duk jikinsa a b'ace da cab'i , wani takaici yaji ya kamashi sosai tabbas duk wanda yake cikin wannan motar ba k'aramin mara mutunci bane , amman tabbas saiya gano ko waye a cikin motar tunda acikin Estet d'insu yake , juyawa yayi ya nufi cikin gidan su ransa a b'ace ga takaicin rasa jam'i dazaiyi....

Wani mahaukacin Hon Sanam ke dannawa a k'ofar gate , lokacin megadin su yatada sallah , babu shiri ya sallame daga sallar saboda sanin hali , da gudu ya bud'e k'ofar gate d'in yana fad'in "sannu da zuwa hajjaju , dawani mugun gudu ta shigo tamkar zata bi takansa , da sauri ya buga wani tsalle yana jan baya tare da dafe k'irji saboda razanar dayayi , tafi minty goma kafin tafito daga cikin motar ta dubesa a wulak'ance tace " mekakeyi da har yafi hon d'in motar ta muhimmanci ? da sauri ya zube yana fad'in " tuba nake ranki shi dad'e wallahi sallah na tayar shiyasa , wani tsaki tayi sannan tajuya ta nufi cikin gida......

Hajiya Nafeesa tana cikin kitchen tana ta k'ok'arin had'a Abincin dare taji shigowar Sanam , k'wala mata kira taji tanayi tamkar k'aramar yarinya , da sauri tafita daga kitchen d'in ta nufi Falor , Sanam naganinta ta taho da gudu tana fad'in " Mumy Kitayani murna Daddy yabani kud'in yace in canza motar , Hajiya Nafeesa tace " shiyasa nafad'a miki kije kisamesa kinsan komai kikeso yana faranta miki , Sanam tayi murmushi sannan tace " Mumy nasan Daddyna yana sona fiye da komai a duniya , Hajiya Nafeesa wani abu taji ya tokare mata a k'irji na takaici amman saboda bariki irin tata sai cewa tayi " in bai soki ba Baby wazaiso ? ke kad'ai Allah ya mallaka mana a duniya kinga kuwa dole musu farin cikin ki , k'ara shiga jikinta Sanam tayi tamkar wata k'aramar yarinya tana jin dad'i , Hajiya Nafeesa cikin ranta take fad'in " duk yadda zanyi na raba wannan soyayyar taki da Mahaifinki sainayi , a koda yaushe na bud'e ido naga yadda yake sonki yake kulawa dake wani takaici ne yake min yawa , a fili kuma tace " bari nakoma kitchen dan kinsan yau girkin da kikeso shinake miki , Sanam ta d'ago tana fad'in "

shiyasa nake sonki Mumyna kina sakani farin ciki sosai , ba kamar waccen matar Daddyn ba yauma danaje saida ta b'atamin rai ,  da sauri Hajiya Nafeesa ta dubi Sanam tace " me Hajiya Maimunar tamiki haka ?  Nan Sanam tafad'a mata yadda sukayi da Hajiya Maimuna , wata dariya suka saka tare da tafawa  Hajiya Nafeesa tace " kin kyautamin walllahi dakika tofah mata miyau ,   nan Sanam ta haye sama d'akinta tana fad'in " ai ko gobe naje gidan nan saina kuma mata kalar wani rashin mutunci mutuk'ar zata shiga gonata .....

Hajiya Nafeesa kitchen ta nufa tana fad'in " banza wawiya wacce bata san ciwon kanta ba , Wai har dad'i takeji dan tayiwa Uwar ta rashin kunya , yarinya zakiyi bayani ne sannan gaba , duk wannan soyayyar danake nuna miki badan Allah bane kawai saboda dukiyar Ubanki  nake lallab'aki , dasannu zaki gane cewa duk inda kishiyar uwa take to tabbas kishiyar ce , tun zuwanki duniya nakeshan wuyarki  kawai ina dannewa ne saboda lokacin baki wuya baiyiba , saina sa kinsan cewa rik'on danake miki shine wanda hausawa suke cewa *'Yar kishiya rik'on me hak'uri* zanci gaba da hak'uri dake tare da nuna muku tawa kalar siyasar......

Wani had'ad'd'en d'aki Sanam tashiga sai k'amshine ke tashi , komai na cikin d'akin kalar pinky ne har fentin d'akin , toilet d'in dake manne jikin bed d'inta tashige , bayan minty 15 tafito daga toilet d'in d'aure da tawul iya guwa sai k'amshin turaren wanka take ,  zama tayi gaban mirror tana goge jikin nata tare da janyi mansha fawa tafara shafawa ,  Sanam nada kyau sosai kana ganinta kaga zallar shuwa arab , tana da kyau na nunawa sa'a ga dirin jiki tamkar itace tazab'i ayita hakan ,  farace sol fatar jikinta har shek'i takeyi saboda hutu da gyara , wayar tace tashiga ruru amman ko kallo wayar bata isheta ba har kiran ya katse....

Shiryawa tayi cikin wasu matsatstsun kaya riga da wando , duk wata sura ta jikinta sai data baiyana , ta d'auki wani tsadadden turare ta fesa ajikinta , tuni k'amshi ya gauraye ko inah na jikinta abinka da 'yar gayu ,  wani filet d'in shoe d'inta ta d'auka tasaka tarae da d'aukar jakarta swuga tarik'e tafice daga d'akin....

Lokacin data sauko k'asa dai dai lokacin Hajiya Nafeesa take jera abinci  a daining , k'arasowa tayi taja kujera  ta zauna tana fad'in " Mumy  yunwa nakeji plss kiyi seving d'ina , Hajiya Nafeesa tace " to my Babyna bari nagama d'akko sauran Kayan sai na zuba miki ,  turo baki tayi sannan tashiga dannan wayarta , sai a lokacin taga me kiran nata k'awarta ce Diyana , da sauri ta dannah calling d'in number , bugu d'aya aka d'aga ana cewa " Baby Sanam wai ina kika shigane yau kwata kwata bakizo an had'u ba ? kinsan fa  yau Zahra take celebrition d'in siyamata sabuwar motar da Daddyn ta yayi , kuma kinsan da gayya takeyin hakan saboda ke , tab'e baki Sanam tayi sannan tace " k'yaleta kawai Diyana banda lokacinta amman ko saboda kar ace ina mata bak'in ciki anjima zanshigo ,  katse wayar tayi batare da tajira me Diyana zatace mata ba ,  lokacin Hajiya Nafeesa ta k'araso tana ajiye kayan hannunta sannan tafara zubawa Sanam Abincin , Faten doya ne wanda yaji Naman kaji  sai k'amshine ke tashi , Sanam tuni tafara zubawa cikinta tana wani danna waya ,  Saida takusa cinyewa sannan ta ture wai ta k'oshi , lemo ta tsiya tasha sannan ta mik'e tana duban Hajiya Nafeesa tace " Mumy nidai zanfita kibani mukullin motar ki da ita zanfita ,  Hajiya Nafeesa tace " yana kan dirowar mirror d'ina kije ki d'auko , sannan karki dad'e dan kinsan anjima Kad'an Daddyn ki zaizo , Sanam tace " to Mumy kikulamin da kanki bye bye ,  Hajiya Nafeesa ta raka ta da harara tana fad'in "

shegiyar yarinya tamkar Aljana dan kyau..

Sanam tana fitowa tashiga motar Hajiya Nafeesa , da sauri megadi yaje ya bud'e mata gate yana fad'in adawo lafiya Hajjaju , ko kallonsa batayiba tasaka kai ta wuce abinta.....

tunda Huneed ya shiga gida canza kaya yake cika yana batsewa , dubansa Hisham yayi yace " wai mutumina ya akayi naganka haka naga jallabiyar ka ta b'aci da cakwali saikace k'aramin yaro , gashi kuma naga sai faman had'e rai kakeyi ? Huneed yace " wallahi nafita sallar Azzahar d'azu kawai wani wawa yazo wucewa a motar ya feshe ni da cakwali , murmushi Hisham yayi sannan yace " duk cikin Estete d'in nan bawanda yake irin wannan gudu sai wata yarinya me suna Sanam , itace take gudu da motar tamkar zata tashi sama , kowa yasanta kaima dan dai baka dad'e da dawowa ba shiyasa bakasanta ba , Huneed ya dubi Hisham yace " wai kana nufin kace wannan gudun da akeyi da motar mace ce haka ? murmushi Hisham yakumayi yana cewa " Allah ya taimakeka ma daba ta taka kaba , dan kusan duk Estate d'in wallahi kowa yasan wannan mugun halin nata , shiyasa duk lokacin dazata wuce kowa yake killace kansa saboda sanin halinta , Huneed jiyayi ransa yakuma b'aci tabbas saiya yi maganinta kuwa , dan tunda tashiga gonarsa wallahi saita raina kanta , mik'ewa yayi yace " inaso kafad'amin da wanne lokacin take wucewa dan tabbas saina saita mata hankalinta , Hisham yace " anjima ma zaka iya jinta sannan wajen sha biyun dare ma tana zuwa wucewa , amman inaso kabar wannan maganar ka shareta , dan wallahi bata da mutunci ko kad'an gashi Daddynta ko k'ararta bayaso ana kai masa , Huneed yace " wallahi daga ita har Daddyn nata dai dai nake dasu kuma tunda har ta tsokanoni wallahi saina koya mata hankali , yatasa tsaki yasa kai yafice daga d'akin nasu .......

Gudu Sanam take tamkar zata tashi sama har ta k'araso gidan gonar Daddyn su Zahra , tunda Diyana tagaya mata anan take Partyn nata , tana shigowa aka fara ihu ana fad'in " Oyoyo *'Yar kishiya rik'on me hak'uri* wannan sunan Sanam tana mugun sonshi , dan haka kawai hannu tasaka cikin jakar ta tafara zuba musu ruwan dollars , dan kwata kwata bata amfani da kud'in Nigeria mutuk'ar zasuyi wani party da k'awayenta , take gayu suka saka wawa suna ihun murna tare da zuba mata kirari , kanta ne yake k'ara fashewa tanajinta bakamar ta , Zahra tuni ranta yafara b'aci da abida gayun sukeyiwa Sanam , taya ita data shirya Party amman koda tazo basuyi mata kirari haka ba , daman tsakanin Sanam da Zahra akwai dabi sosai , kuma kowacce jitake da kanta tare da tak'ama da kud'i , sai dai duk kud'in Daddyn Zahra bai kai Daddyn Sanam ba , tuni Zahra ta d'auki speaker tayi wata tsawa tana fad'in "ya isheku haka malamai , in itace ta taraku zan iya tafiya inbaku guri , nan suka shiga bata hak'uri suna mata nata kirarin , Sanam ta tab'e baki tare da hawa step d'in da Zahra take , tana zuwa ta mik'awa Zahra hannu tana fad'in " Congrat k'awata rai yakashe , bandir d'in Dollars ta saka mata a hannu tare da cewa " gashi kyasha mai , tana gama fad'in hakan tayi sauri ta sauko tare da watsa kud'i sama sannan ta bar gun.....

Huneed tunda akayi sallar isha'i yaja ya zauna a k'ofar gate d'in Estate , dan yace yau bazai

shiga gidaba har sai Yarinyar nan tazo tasamesa , kulle k'ofar gate d'in yayi yacewa megadi yaje ya huta zuwa anjima zai jire masa , wajen k'arfe goma na dare saiga Sanam ta nufo Estate da mugun gudunta data saba , koda Huneed yaji tahowar ta sai ya mik'e tare da nufar k'ofar gate d'in , aikuwa tuni Sanam tafara mahaukacin Hon d'in ta , cikin ransa yace zakiyi bayani wallahi nan ba k'ofar gate d'in gidan ku bane da kika saba iko , ganin ba'azo an bud'e mata ba yasa tafito a fusace , k'ofar ta nufo tana fad'in " wane mara mutuncinne wajen daya ruf'e gate d'in kuma yanaji ana hon bazai zo yabud'e ba ? buga k'ofar tafarayi amman taji shuru ba wanda yayi magana , ranta tuni ya k'ara b'aci sosai lallai masu gadin nan basu san ta bane shiyasa , tuni Huneed ya nemo ruwan sanyin s bokiti guda harda k'ank'ara sannan ya nufo k'ofar gate d'in , dama gashi anyi ruwan sama garin ya d'au wani sanyi me ratsa jiki , sakatun dayasa yashiga zarewa yana murmushin mugunta , lokacin Sanam ta kira wayar Mumy amman ba'ad'agaba , ranta yagama b'aci mutuk'a , tanajin anfara zare sakata ta dubi k'ofar tana k'issima irin rashin mutuncin dazatayiwa wanda ya bud'e .....

Bata ankara ba sai saukar ruwan sanyi taji ajikinta , tuni ta tsorata tana ja da baya jikinta yana tsuma , gashi ko kad'an Sanam bata shiri da ruwan sanyi , Huneed ya hasketa da touthlith yana fad'in " jiki wata k'azama dake sai rashin kunya da iya shege , inaso kisani ba'ayimin batare da na rama ba , kuma daga yau mun k'ullah nida ke , dan saina gyaraki a wannan Estate d'in namu , maza kizo ki wuce kibawa mutane guri mara kunyar banza , Sanam data daskare tamkar gunki a wajen ko motsi batayi saboda tsabar takaici.........

*Comment* plss

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_ 🌹😍
[9/27, 09:37] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on_ _Me_ _Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 3.

Tanaji tana gani Huneed ya juya yashige cikin Estate d'in , da kallo Sanam tabi bayan sa tare da mamakin irin Zarrarsa dayayi mata wannan wulak'ancin , komawa tayi cikin motar ta taja ta da gudu tashiga Estate d'in itama........

Sanam tana zuwa tayi wani mahaukacin Hon. Da gudu megadinsu yatafi tamkar zai kifa ya bud'e gate d'in , da gudu ta shigo tayi parking ta fita kana ganinta kasan a fusace take , tana shiga cikin Falor ko kallon kowa batayi ba tahaye sama da gudu.....

Hajiya Nafeesa lokacin suna zaune ita da Alhaji Abba suna hira , yana ganin wucewar Sanam a haka ya mik'e yana cewa " Anya lafiya kuwa naga My luv tashigo gida a haka ? Hajiya Nafeesa cike da kissa tace " nima naga kamar ranta a b'ace inajin dai akwai abinda akayi mata , da sauri Alhaji Abba ya nufi sama d'akin Sanam , Hajiya Nafeesa tabishi da wata uwar Harara tana fad'in " aikin banza yarinya ta dunga garaka kamar wani k'wallo , wannan soyayya taku gab nake da datseta , tsaki taja tare da nufar saman itama ........

Sanam tana shiga d'akinta tanufi toilet tasakarwa kanta ruwan d'umi , tanayin wanka tana tunanin irin rashin mutuncin da guy d'innan yayi mata , tabbas tunda aka haifeta batajin akwai wanda yatab'a yimata irin wannan wulak'ancin ba ,

Shigowar Daddyn ta taji cikin d'akin nata yana kiran sunan ta , dasauri tayi maza ta fito daga toilet d'in d'aure da tawul, Daddyn ta yace " meyafaru dake kika shigo a wani yanayi ? murmushi tayi sannan tace " babu komai Daddy wlh gajiya nayi kuma gashi inajin fitsari shiyasa , wata ajiyar zuciya yayi tare da cewa " kin tsoratani My luvly Dauther , dai dai nan Hajiya Nafeesa tashigo tana fad'in " meye yafaru my Happiness duk kin tsorata mu , murmushi tayi tace " babu komai fa Mumy kawai fitsari nakeji shiyasa , nan Hajiya Nafeesa ta rik'e mata kunne cikin wasa tana fad'in " zanyi maganinki agidan nan , naga kullum sabuwar rigima kike k'arayi , dariya suka saka dukansu sannan Daddy yace " in kinshirya kifito zamuyi magana , Sanam tace " to Daddy bari nasa kaya ganinan zuwa.......

Huneed baki har kunne saboda Abinda yayiwa Sanam ko banza zata shiga taitayinta , duk dayaji da gudu ta wuce amman zai gyara mata zama kwanan nan ,

Tunowa yayi lokacin daya watsa mata ruwan tayi tsamo tsamo da ita , dariya ya tuntsire da ita yana cewa " ni ko fuskar ta ban tsaya gani ba saboda wulak'ancinta , cikin zuciyar sa yace " amman gaskiya tana kama da Aljanu , dan yaga farinta har yaso yayi yawa duk da bawani tsayawa yayi ya k'are mata kallo ba ......

Sanam cikin kayan bacci ta fito Falor tasamu guri kusa da Daddyn ta ta zauna , cike da

Shagwab'a tace " Daddy gani mezaka gayamin ne ? murmushi yayi yadubi Hajiya Nafeesa yace " ki gaya mata da kanki , murmushi Hajiya Nafeesa tayi tace " kagaya mata da kanka kaidai , Sanam tafara turo baki tana cewa " wai Daddy mene dan Allah kugayamin plss ,  Daddy cike da murna yace " zaki samu k'anwa ko k'ani kwanan nan , wani tsalle ta daka tana rungume Hajiya Nafeesa tace " Mumy da gaske cikine dake  wayyo dad'i zansamu k'ani , murmushin yak'e Hajiya Nafeesa tayi tare da cewa "  banice nake da cikiba my Baby , Mumy Maimuna itace take da ciki ,  tsayawa tayi cak murnar ta ta koma ciki tana fad'in " toni ina ruwana da cikinta tunda ba Mumyna bace ,  Daddy ya dubeta yace " haba My luv yakamata kitayani da murna koda bazakiyi murna saboda itaba , karki manta inaso naga kinsamu k'anne wanda zakina wasa dasu ,  shuru tayi nawasu mintyna sanna tace " Daddy kayi addu'ar Allah yabawa Mumyna sainayi duk yadda nakeso dasu , amman a yanzu bana murna dan nasan soyayyar dakakemin ce zata ragu ,  murmushi yayi yace "haba my luv kinsan duk yawan Yaran da zansamu a duniya babu abinda zai ragu game da soyayyarki ,  ked'in kece wacce Allah yafara bani a duniya kinga kuwa dole zansoki tamkar raina ,  Hajiya Nafeesa dauriya kawai takeyi saboda wani abu dake tokare da k'irjinta ,  mik'ewa Sanam tayi sannan tace  " saida safe Daddy nagaji bacci nakejin  , to my luv Allah yatashemu lafiya kiyi bacci me dad'i , matsawa tayi ta sumbaceshi a kunci , shima ya sunbace ta a goshi sannan ta juya wajen Mumy itama hakan tayi mata Ta juya tahaye sama d'akinta.....

Zahra tunda Sanam tabata  wannan kud'in takejin haushi , ita Sanam zatazo har wajen Party d'in ta ta tozar tata , tabbas saita rama ai lokacin Birthday d'in Sanam yakusa anan zata rama abinda tayi mata ...

.

Washe gari Sanam sai sha d'aya ta farka tayi wanka ta shirya cikin wata doguwar rigar atamfa ,  d'inkin sosai yakamata ko ina najikinta a d'ame ,  sakkowa k'asa tayi  sai faman zabga k'amshi take tamkar wata sabuwar Amarya ,  zama tayi kan dinnig tafara had'a break fast , Soyayyiyar plantain ta xuba tare da had'a tea , sai da tagama zubawa cikinta sannan ta mik'e tafita........

Harabar gidan tafito tafara tunani wanne mataki zata d'auka akan wanda yayi mata wanka da ruwan sanyi , tabbas saita nemosa ta nuna masa da banbanci tsakanin matsiyaci dakuma me kud'i ,  dan daga ganinsa talaka fak'iri dan tasan duk cikin estate d'in su babu wanda yakai Daddyn ta kud'i , ita kuwa duk wanda bai kai Daddynta ba to tabbas ba me kud'i bane a wajenta ,  a hankali take tafiya har ta k'araso k'ofar gate , da gudu me gadi yataho yanayi mata kirari tare da cewa " hajjaju aikene kikawo ayi miki ? bud'emin gate kawai tace tana kuma d'aure fuska , da sauri ya bud'e mata tare dayi mata fatan dawowa lafiya.......

*Kuyi hak'uri da wannan*

*Comment plss*

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_🌹😍
[9/27, 09:37] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on_ _Me_ _Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 4.

Tunda Sanam ta fito daga cikin gidan su tafara zagaye a Estate d'insu duk akan idon Huneed , dan shima tunda gari ya waye yafito yake gadin wucewar ta , dan yanaso ya tabbatar da cewa taji kashedinsa ko kuwa , tana tafe tana duba k'ofofin gidajen dan sotake ta tabbatar da a wanne gida yake , kamar daga sama taji muryar sa yana fad'in " sokike kiganni ko ? da sauri taja da baya tana dubansa cikin zuciyar ta take fad'in " anya wannan mutumin mutum ne kuwa ? zarrarsa da kuma yadda yake nuna wata izza dajin kansa , katseta yayi da cewa " kind'auka ni Aljanine ko ? k'iris yarage Sanam bata zura da gudu ba , wata zufa ce ta tsatstsafo daga jikinta duk irin sanyin da akeyi , amman ta dake ta dubesa tace " Hmm nasan kai mutum ne kamar kowa , sannan ba kowa bane kai face talaka fak'iri wanda bai wuce kazo a meyimin wankin takalmi ba , Wani Shu'umin murmushi Huneed yayi yana dubanta sannan ya matso gab da ita Numfashin su na dukan juna yace " inaso kisani duk wani d'agawarki da ji da kanki da kuma dukiyar dakike tak'ama da ita duk abanza suke a wajena , kuma kamar yadda kikace ni bakowa bane yes ni bakowa bane kuma ba d'an kowa bane , amman inaso kisani ni ba k'ask'astance bane bakuma mara zuciya bane , ni d'in da kike gani Namiji acikin mazaje me zuciyar Nema , kuma mutuk'ar muna numfashi dani dake a duniya to watarana sai kin gogemin takalmin da zansa , kuma kin wankemin kayan jikina tare da gogemin motar dazan hau , yana gama gaya mata hakan yajuya zai tafi tuni tayi saurin shan gabansa tare da rik'e k'ugu tace "

wai kai dame kake tak'ama da har kakemin irin wannan maganganu ? Huneed ya dubeta yace " bana tak'ama da komai sai dai innuna miki Namiji Namijine a ko'inah kuma duk irin girman kan mace to tabbas Namiji ne gatan ta , nasan duk wanna d'agawar taki da jin kan naki dole watarana gidan wani zakije kuma dole ya juyaki mutuk'ar ba maza yarako duniya ba , kuma ina fatan kina sane da sharud'an da na gindaya miki akan gudu da motar , in kunne yaji to jiki ya tsira yashige yafara tafiya abinsa , a fusace Sanam tace waye kai d'in kuma acikin Estate d'in inaso isan waye Mahaifinka da har kake kafamin doka haka ? batare da Huneed ya juyoba yace " Sunana Huneed Abdallah Kiyi tambaya cikin Estate d'in zakiji tarihina in kina buk'ata , Nabarki lafiya Bera a cikin Mata.........

Sanam tsayawa tayi tana kallon sa har ya k'ulewa ganinta , Sunan daya kirata dashi tashiga maimaitawa Bera a cikin Mata , tabbas wannan yaraina mata hankali wato yana nufin ita ba mace bace ba , lallai zata nuna masa kalar halinta sai yagane lallai ita ba Bera bace mace ce data amsa sunan ta , a fusace ta juya ta nufi Hanyar gida.......

Huneed yana dawowa yasamu kira a wajen ogan su , tuni aka turasu aiki wani gari a jihar Calaba dan ko 'Yan ta'adda , had'a kayansa yayi kafin yafito har anzo d'aukar sa , yana fito wa yaron sa ya fito ya sara masa tare da bud'e masa murfin mota , Hisham yadubi Huneed yace " Soja wuta soja harbi Soja gatan daji inbaku gari baza ya kwana k'alau ba , inayi maka fatan samun Nasara a wannan fitar taku Allah yadawo mana dakai lafiya , Murmushi Huneed yayi tare da duban Hisham yace " Ameen d'an uwa ka kulamin da Hajiyar mu kadunga bata magungunan ta akan lokaci , sannan inaso kasa idonka akan Berar yarinyar nan kaga zata gyara halin nata ko saina fito mata a kalar ta , tuni Hisham yasa dariya yace " Anya wannan yarinyar zata canza kuwa ? amman zandunga saka ido naga yadda wasan naku zai k'are , Huneed yayi Murmushi yace " ai haryanzu yarinya ce batasan komai na duniya ba , gata da kud'i shine tasani amman da sannu saina saita ta tadawo dai dai , tarbiyar da iyayenta sukayi mata saina gogeta na d'ora mata tawa , Hisham yace " Allah yasa hakan dan gaskiya basu d'orata adai dai ba , Huneed yace " zata dawo dai dai tunda har ta shiga gonata , juyawa yayi ya shiga motar tare dacewa Hisham sai sunyi waya....

Koda Sanam tadawo gida Sama tahaye cikin d'akinta , wayar ta ta d'auko tare da kiran Number Diyana , bugu d'aya tayi ta d'aga tare da fara yiwa Sanam kirari " Babbar Yarinya gidan kud'i sarauniyar kyauta , duk wanda yaga kiranki to yafara washe baki dan yasan Alkairine , Sanam cike da jin kai da wata Izza tace " Diyana kina inah yanzu ? Diyana tace " ina gida a zaune inah zaman banza ko da aikine inzo ? Sanam tace " tabbas akwai Aiki akan wani Mutum dayake neman zama matsala arayuwa ta , Diyana tace " waye shi dazai shiga sabgar Uwar d'akina baya goya marayu ? Sanam tace " shine nakeso kizo yanzu kiyimin bincike cikin Estate d'in nan namu akan labarin sa kaf , Diyana tace " karki damu *Rik'on Me Hak'uri* ganina zuwa kibani minty 10 kacal , Sanam ta kashe wayar tare dayin jifa da ita kan gado tana rik'e kai .......

Minty Goma na cika sai ga Diyana a gidan su Sanam tamkar Aljana , tana zuwa Sanam tafara bata labarin tun daga farkon Abinda Huneed yayi mata har izuwa yau d'in nan daya kafa mata wannan sharud'an , Diyana tace " inason sanin sunansa dakuma Number gidan su , Sanam tace " Sunansa Wai Huneed Abdallah number gidan su kuma wallahi bansan taba , sai

dai inaganin in kika rik'e iya sunan ma yayi zaki samo min komai nasa , Diyana tace kibani 50 min. Zanfita induba miki cikin Estate d'in nan naku harda wajen sa , Sanam tace " hakan yayi dan sonake nayi shiri sosai akansa dan bazan k'yalesa ba tunda ya tab'oni , Diyana tuni ta mik'e dan fita nemo labari akan Huneed.......

Diyana na fitowa tafara duba cikin Estate d'in , duk k'ofar gidan dataga da megadi sai taje ta tambayesa ko yasan Wani Huneed Abdallah , sai da taje gidaje wajen guda hud'u kowanne yana baisan shiba , tana shirin buga gida na biyar sukayi karo da Hisham yafito daga k'ofar gate d'in gidansu , yana ganinta suka dubi juna Diyana tasakar masa wani shu'umin murmushi , k'arasowa tayi tana wani yauk'i sannan ta dubesa tace " dan Allah tambaya nakeyi ko Allah zaisa nadace ? Hisham yace " yi tambayarki ko Allah zaisa nasani , Diyana tace " ina neman wani Guy ne me suna Huneed Abdallah , dubanta Hisham yayi sosai sannan yace " Saurayin kine Kenan ? murmushi Diyana tayi sannan tace " ko d'aya wlh saurayin k'awatane shine ta aikoni gunsa kuma ni bansan gidan suba , nadai san a cikin Estate d'in yake shiyasa nake cigitashi ko Allah zaisa nagansa , Hisham yayi murmushi yace " ni ma bak'one a nan Unguwar sai dai kibari anjima zansamu me gadin gate d'in Estate d'in gaba d'aya na tambayesa ko zai san shi , Diyan cike dajin dad'i tace " yauwa nagode sosai kaga ka hutar dani , yanzu bari nabaka Number na inkasamu Labarin inda yake saika kirani , tuni Diyana tabawa Hisham number ta , dan ita kam tana ganinsa taji ya burgeta dan guy d'in yahad'u sosai , nan sukayi salama ta wuce tatafi Abinta , Hisham na tsaye har saida yaga b'acewar ta sannan ya juya yashiga gida.......

Diyana na dawowa tabawa Sanam labari duk yadda sukayi da Hisham , sai dai kwata kwata ta manata bata amshi number sa ba itace tabashi tata , gashi ko Sunan sa bata sani ba , dan haka suka zauna suna jiran kiran wayar Hisham ........

Koda Hisham ya shigo cikin gida tuni yakira Huneed , yana d'agawa ya sheda masa anzo nemansa kuma budurwa ce wai k'awar tace ta turota , Huneed yayi murmushi yace " kai me kake tunani akan haka ? Hisham yace " nidai bankawo komai ba nayi tunanin kodai ita wacce tazo nemanka d'in itace take sonka ? Murmushi Huneed yakumayi sannan yace " aikota akayi amman ba itace ba , kuma Bera ce ta saka ta tayi bincike akaina dan haka kabasu duk Abinda suke buk'ata indai basu wuce gona da iri ba , sai munsake waya kit yakashe wayar yabar Hisham rik'e da waya baki asake , yana bala'in mamakin Huneed da wannan halin nasa , tabbas zai iya cewa Huneed d'in d'an baiwane sosai acikin mutane.......

*Bana ganin Comment*🤕

*Zantafi yajin aiki*
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on_ _Me_ _Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 5.

Har aka kira Magriba Sanam da Diyana basu ga kiran Hisham ba , k'arshe dai Diyana tayiwa Sanam sallama akan gobe zata dawo lallai sai ta nemo mata labarinsa......

Sanam sosai takeson sake ganin Huneed , dan ita komai nasa ya tsaya mata aranta , tabbas bata tab'a ganin mutum da bashi da tsoro ko kad'an ba irinsa , dan haka tanaso ko sau d'ayane ta bashi tsoro ta kuma nuna masa wacece ita......

Duk wani motsi na Sanam tuni Huneed yasa asaka masa ido akanta , dan haka ma yasan shirin su akan sanin waye shi ita da Diyana..

Washe gari Hisham ya kira wayar Diyana yace mata inta shirya a inah zasu had'u yabata labarin Huneed d'in , aikuwa tamkar anyi mata albishir da gidan Aljannah haka takira Sanam ta sheda mata , Sanam tace " kawai ki kawosa gidan mu cikin Garden sai muzauna anan yagaya mana , da wannan shawarar Diyana ta kira Hisham ta fad'a masa inda takeso su had'u , nan suka tsaida lokaci sannan sukayi sallama.......

Tuni Diyana ta iso gidan su Sanam dan bataso yazo bai sameta ba , suna zaune suna hira saiga kiran wayar Hisham akan ya k'araso , sawa sukayi aka shigo dashi tare da kai masa kayan motsa baki , yafi minty 10 dazama sannan yagansu sunjero sun taho suna hira abinsu , suna zuwa suka gaisa da Diyana , ita kuwa gogar sai wani shan k'amshi take ita ala dole tanajin kanta , Hisham ya dubeta yace " barka da hutawa Hajjaju dafatan kina lafiya , ata k'aice ta amsa masa da cewa lafiya , daga haka taja kujera ta zauna tare d fara danna wayar ta tamkar batasan damutane a wajen ba , murmushi Hisham yayi cikin zuciyar sa yana fad'in " tabbas wannan yarinyar bamai saita ki sai Yaya Huneed shine zai iya saita ki , a fili kuwa yace " to

Malama Diyana nasamo miki labarin Wannan guy d'in da kika sani ,   Diyana tace " ina godiya sosai dan haka ina sauraren ka ......

Da farko dai Sunan sa Huneed Abdallah Ma'aji , Haifaffen garin Borno state ne  acan yayi karatunsa tunda ga matakin primary har yakai ga kammala Digree d'insa , Mahaifinsa ya kasance Babban Soja a Barrack d'in Borno , su biyu iyayensu suka haifa dagashi sai d'an uwansa ,  Mahaifinsa Canal Abdallah Ma'aji yarasu a wajen wani yak'i da akayi  lokacin a garin Barno ,  tunda nan Huneed yayi shirin maye gurbin Mahaifinsa , tashi farko dayatafi training yadawo da babban resure akan and'aukesa aikin soja , kuma yafito da babban matsayi yanzu haka Shima babban Canal ne ,  aiki ne yadawo dasu Abuja shiyasa yataho da Mahaifiyar sa dakuma d'an uwan sa ,   Huneed mutum ne me rik'o da Addini  gashi da son zumumci , sai dai Akwai abubuwan da baya shiri dasu  sune  baya shiri da mutum me girman kai , baya shiri da mutum me wulak'anta Al'uma , sannan bayason mutumin da girmama na gaba dashi , miskili ne sosai inkinga dariyar sa to yana cikin 'yan uwansa ko kuma yana tare da mahaifiyar sa , bayason yawan tambaya ko kuma a dunga yi masa dariya , hakan na harzuk'asa sosai kuma yana son  wasa da k'ananan yara  , a b'angaren cima kuma mutum ne me son tuwon biski miyar taushe ,  yana son saka kaya k'ananu sannan duk Juma'a yana saka jallabiya ,  yanason k'amshi sosai yana shiri da dukkan mutum me tsafta da kuma k'amshi , wannan shine cikakken labarin Huneed Abdallah Ma'aji ,  sai dai kuma abinda ba'a rasa ba wanda bansani ba .....

Ajiyar Zuciya Diyana tayi tare da cewa " mungode sosai Hisham , Sanam tuni ta mik'e tabar wajen tamkar batasan da wasu mutane ba abinta , binta Hisham yayi da kallo yana fad'in tabbas akwai babban aiki atare da Yaya Huneed ,  Diyana ta dubesa tace " magana kakeyine ? yayi sauri ya mik'e yace " ni zan zo na wuce dan nasan lokacin da Hajiyar mu zata sha magani yayi , nan sukayi sallama da Diyana ya wuce yatafi abinsa ........

*Kuyi maneji*

*'Yar* *Mutan* *Kanawa* _Ce_ 🌹😍
[9/27, 09:37] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on_ _Me_ _Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪

https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}* ✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 6.

Diyana na shiga cikin gida tasamu Sanam a falor tana zagaye , tana ganin Diyana tace " tabbas dole asameshi da wannan halin ashe soja ne , to tabbas saina janyo masa ansallameshi daga wajen aikin dayake tak'ama dashi , tunda harya shigo rayuwata sai yagane bashi da wayo , nagode Diyana nasa miki dubu d'ari biyar a account d'inki kasha ice cream , tana gama fad'ar haka ta haye sama abinta , Diyana cike da murna ta fice abinta tana murnar samun kud'i........

Tundaga nan Sanam tayi sercing d'in Huneed a Social media , duk wani posting d'in dayayi sai data bi ta duba , tab'e baki tayi cikin Zuciyar ta tana yaba kyan halittar Huneed , samun kanta tayi da kafe shi da ido tana kallo saita ke ganin tamkar murmushi yakeyi mata , Wurgi tayi da wayar sannan a hankali ta furta Huneed zakasan nice nashiga rayuwar ka bakaine kashiga tawa ba....

Washe gari tuni motar Sanam data canza ta iso , nan tasha wanka tashiga tafara zagaya gari , ranar gudun datakeyi ya wuce ko wanne irin gudu datake , duk inda tayi saikaga kowa na neman hanyar tsira da ransa , a haka ta k'araso gidan su Diyana dan nuna mata motar ta , tana shigowa lokacin Diyana na fitowa daga cikin gidan su , sakin baki Diyana tayi tana kallon had'uwar motar da Sanam ke ciki , cikin ranta tace " arzik'i yayi arayuwa , Allah yabamu rabon mu mu inba dan muna shiri da Sanam ba banga dalilin da zai hanani auran Daddyn taba , dai dai lokacin Sanam ta fito cikin wasu d'amammun riga da wando tana sanye da glass a idonta , mukullin motar ta na hannunta sai karka d'ashi take tana taunar cingum , da gudu Diyana ta k'araso tana fad'in " wow congrat my k'awa kice motar ta iso , Sanam tayi murmushi tana duban Diyana tace " Zahra meyin gasa dani to wlh wannan motar ko Babanta baitab'a hawan irinta ba , Diyana tace " wace ita taja da me *'Yar kishiya rik'on me hak'uri* ai duk kud'in Baban ta bai isa ya siyamata irin wannan ba , Sanam tace "kinshirya hawan ta ko ba yau ba ? da Sauri Diyana ta zagaya tana fad'in " wanne ba yauba yanzu ma haka dama ice cream zani sha , nan Sanam ta shiga taja motar dawani mugun gudu.......

Alhaji Abba yana zaune a falor sa yana cike wasu takaddu , Hajiya Maimuna ta sakko daga sama tana zabga k'amshi tamkar sabuwar Amarya , tana k'arasowa tace " sannu da aiki My Husbee , murmushi Alhaji Abba yayi yana duban Hajiya Maimuna yace " yauwa tauraruwar mata , samun waje tayi ta zauna tana duban sa sannan tace " inason magana dakai amman

ina fatan kayimin kyakkyawar fahimta , Alhaji Abba yace " ina sauraranki ki fad'i duk abinda kikeson fad'a , Hajiya Maimuna tace " inaso dan Allah ka nemawa Sanam makarantar islamiyya kasata a ciki , yadda take tafiyar da rayuwar ta yakamata ace tana da ilimin addini ko Allah zaisa ta rage wasu abubuwan , Alhaji Abba yayi shuru yana nazarin maganganun Hajiya Maimuna , can ya nisa yace " kinsan a yanzu My Baby ta girmi zuwa makarantar islamiya , sai dai zanyi magana da ita muji yadda zatace , inta amince sai asamar mata akaita , dan kinsan tunda tadawo daga k'asar turkey tace hutu take buk'ata , amman zanyi mata magana duk yadda tace haka za'ayi , dubansa Hajiya Maimuna tayi sannan tace " Haba Husbee taya zakace sai yadda tace haka zakayi wai kaine ka haifi Sanam ko kuma itace ta haifeka ? Murmushi Alhaji Abba yayi sannan yace " bazaki gane irin son danakeyi wa Sanam ba , karki manta itace kad'ai 'Yar danake da ita a duk duniya sai kuma abinda yake cikinki , kinga kuwa wanda yake ciki bani da tabbacin samunsa ita kuwa tana doron duniya dole insota fiye da komai , Hajiya Maimuna tace " ban hanaka kaso Sanam ba amman inaso kasani yakamata kasan cewa ita fa mace ce kuma gidan wani zataje , mutuk'ar tana tafiyar da halayyar ta yadda takeso to tabbas bazata iya zaman aure ba , da sauri Alhaji Abba yadubi Hajiya Maimuna yace " dole saitayi auren ? inaso kisani mutuk'ar mijin da Sanam zata aura bazai k'yaleta tayi yadda takeso ba to wallahi sai dai ta zauna haka dan bana son ace antakurawa Rayuwa ta , wallahi Maimuna badan kece kika tsugunna kika haifi Sanam ba to wallahi zance kinq kishi da ita , kuma da yanzu kindad'e da barmin gida , wani tsaki yaja tare da d'ebe takardunsa dukansu ya nufi sama......

Hajiya Maimuna binsa tayi da kallo tana mamakin irin halin Alhajin , kwata kwata indai akan Sanam ne bashi da mutunci , zai iya rabuwa da kowa akanta ita kanta tasheda , saboda Sanam yarabu da ' Yan uwansa da dama a hankali ta furta Allah kasa sugane shi da 'yar tasa.......

Sanam da Diyana sunshiga gari sai faman wasa suke da motar , duk inda suka wuce sai anyi Allah wadai dasu , gidan su Zahra suka nufo dan nuna mata motar , lokacin Zahra na zance da saurayin ta Najeeb , ji sukayi anayin wani shegen hon. Me gigita mutane , da gudu megadi ya bud'e gate d'in aikuwa Sanam ta figo motar a guje tashigo cikin gidan , Zahra da Najeeb tuni suka mik'e tsaye ganin yadda aka shigo da motar da gudu tamkar za'a yo kansu , bin motar Zahra tayi da kallo dan tasan bata tab'a ganinta ba , kuma sannan Daddyn ta yana gida bare tace shine yayi sabuwar motar , kid'an dataji yana tashi tamkar anje club yasa tagane Sanam ce aciki , tuni taji ranta yayi mugun b'aci , bata gama tunani ba taga anbud'e murfin motar Sanam ce ta fito tana taunar cingum tamkar wata karuwa , d'aya gefe kuma Diyana nace tafito itama , dukansu bawacce tayi shigar mutunci ko wacce surar ta a bayyane take , wani kishine ya ziyarci Zahra dan tasan halin Najeeb sarai da son mata , musamman had'add'un mata irin su Sanam , Diyana ce tace " barka da hutawa Zahra dafatan munsameku lafiya , daman zuwa mukai mu nuna miki sabuwar motar da Sanam tayi , itama idan kinga zakisa Daddyn ki yasai miki to mukuma zamu kuma canza wata , dan kinsan *'Yar kishiya* anriga da antara mata ba Albashi suke d'auka ba , Zahra sosai taji zafin maganganun Diyana amman sai ta dake tace " *'Yar* *Kishiya* ina tayaki murna Allah yasanya Alkairi , ke kuma Diyana ai

wanda ni ansan muna dashi kefa dakike binta kike maula , murmushi Diyana tayi sannan tace " dad'in abin nice nake maular ba Ubana ba , kuma inayin maular ne a inda nasan akwai abin bayarwa , Zahra zatayi magana Najeeb yace " sorry Baby ba girmanki bane , kishare kawai karki biyewa 'yar yaga riga , wani mugun kallo Sanam tayi masa sannan tace " waye 'Yar yaga rigar ?  Najeeb yace " wacce take take miki baya mana , Sanam tace " ka gyara lafazinka tunkafin mu kunyata ka a gaban budurwar taka , tana gama fad'ar haka tashige cikin motar suka bata wuta sannan suka fice daga cikin gidan.......

*Zantafi yajin aiki tunda ba'ayin Comment😒*
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Nagode sosai Mutanena da tarin addu'oinku , Allah yabar k'auna_

Chapter 7.

Bayan kwana biyu  Sanam kwata kwata bata canza ba ,  gudu a motar sai abunda yayi gaba  dan so uku tana jiwa mutane ciwo ,   Duk abinda takeyi Huneed nasane da ita  kawai jira yakeyi yagama abinda yakeyi yadawo , dan ya fuskanci lallai saiya koya mata hankali sannan za'asamu sauk'in ta .......

Yau Alhaji Abba na gidan Hajiya Nafeesa  suna zaune suna hira sai ga Sanam , tana

shigowa ta dubesu tace " Hi Daddy Hi Mumy , Alhaji Abba yace " Hy my luv your wel come , K'arasowa tayi tana taunar cingum ta zauna sannan ta dubi Daddyn nata tace " Daddy inason zuwa Turkey za'ayi bikin wata k'awata da mukayi karatu tare kuma acan suke , murmushi Alhaji Abba yayi sannan yace " bakomai My luv zantura miki kud'i ta Account d'inki saikiyi yadda kikeso , wani tsalle Sanam tayi tana rungume Daddyn nata sannan tace " thanks my sweetheart Allah yakare mana kai , Ameen my luv Allah yayi miki albarka , Da sauri Sanam ta mik'e tayi sama tana murna , dan kwata kwata bata zata Daddyn ta zai barta taje Turkey ba........

Hajiya Nafeesa wani kishine ya turnik'e ta ko magana ta kasayi , cikin ranta take fad'in " wannan farin cikin naku da kukeyi duk lokacin da kuka kasance da juna kun kusa dainashi , dan saina saka muguwar k'iyayya a tsakanin ku ta yadda in d'aya yaga d'aya sai yabar guri , Alhaji Abba ne ya katse ta da cewa " lafiya kuwa Matar kirki ? murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " jinayi banason Sanam tayi tafiyar nan , dan kasan banajin dad'in na wayi gari bansata a idanuna ba , wani dad'i Alhaji Abba yaji murmushi yayi yana janyo Hajiya Nafeesa cikin jikinsa sannan yace " kiyi hak'uri kibarta taje ai nasan baza ta dad'e ba zata dawo , wannan soyayyar da kike nunawa My luv itace tasa nake k'ara sonki , ina Alfahari dasamunki a matsayin mata , kin d'auki Sanam tamkar kece kika haifeta kin nuna mata gata da soyayya wacce ko wacce ta haifeta batayi mata ita , nagode sosai matar Kirki kema Allah ya nuna min randa zanga d'anki a duniya , Hajiya Nafeesa cike da kissa tace " inbanso Jininka ba Alhaji wazanso ? Sanam kuma 'Yace a guna na raineta tuntana tsumma inbanso ta ba wazan so , inajin kewar ranar da zatazo wacce Sanam zatayi min nisa , Alhaji Abba yace " ai babu wanna ranar da My luv satayi miki nisa , Hajiya Nafeesa tace " Akwai mana Alhaji ko kamanta da ranar aurenta , kasan nan gaba kad'an gidan wani zataje dole zamu rabu , Alhaji Abba yace " duk wanda zai kasance miji a wajen Sanam tabbas zai kasance a k'arkashina yake , dan nafison ta auri wanda zandunga bashi umarni yana bi wanda yarinya ta zatayi yadda takeso , wani murmushi Hajiya Nafeesa tayi cikin ranta tace " lokaci yafara , zansa Fahad yashigo rayuwar Sanam yadda zamu tafiyar da komai a dai dai , a fili kuwa tace " Allah dai yabata miji nagari wanda zai dunga yi mata duk abinda takeso , Alhaji Abba yace Ameen......

Huneed yau ya dira garin Abuja da tarin Nasarorin da suka samu , sosai Hajiyar sa tayi murna da ganinsa ita da Hisham , wanka kawai yayi yaci abinci yafito daga gidan , dan yanaso yau sai Sanam tashiga tai tayinta , bai mi minty 15 da zama ba saiga motar ta nan ta taho da mugun gudu , aikuwa shima ya shiga cikin tasa ya take mata baya , kwata kwata Sanam bata kula dashi ba dan cikin murna take sosai sai faman jin kid'a take abinta , sai da yabari tashiga wani layi mara yalwar Jama'a yayi sauri yasha gabanta , wani wawan birki taja har tana bige bakinta a jikin sitiyari , cike da masifa ta fito tana fad'in " wanne mahaukaci ne wannan d'in haka ? motar Huneed ta nufo sai zage zage takeyi tana fad'in " banza talakan wofi kawai , taya zaka zo kasa mutane su kusa jin ciwo taja wani tsaki mtsss, Huneed tuni yasa bak'in glass ya rufe k'wayar idanunsa , sannan yasa face mark ya rufe bakinsa da hancinsa , tuni ya bud'e murfin motar ya fito , baiyi wata wata ba yajanyota ya wurga ta cikin motar tare da zagaya wa ya shige wajen tuk'i ya figi motar da mugun gudu , tuni yayi waya da Hisham akan yazo ya d'auke motar Sanam d'in ya maida mata da ita gidan su.......

Ihu Sanam take tana nan agaji tare da k'ok'arin bud'e motar ta fice , sai dai ko 'inah a rufe yake gam takasa bud'e komai , shikuwa ko kallonta baiyi ba kawai gudu yakeyi sosai tamkar zasu tashi sama ........

*Kuyi maneji*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪🏻
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 8.

Dai dai k'ofar wani gida Huneed ya tsayar da motar sa , fitowa yayi daga ciki yana huci tamkar zaki , zaga yawa yayi b'an garen da Sanam take ya bud'e ta , janyo ta yayi waje da k'arfin tsiya tamkar zai b'alla ta , k'ofar gidan ya nufa rik'e da hannun ta , yana zuwa ya saka mukulli ya bud'e gidan yashiga da ita , sosai Sanam ke ihu amman babu mejin ta saboda unguwar babu gidaje.......

Huneed maida k'ofar yayi ya rufe kuma har lokacin yana rik'e da hannun Sanam , sai da ya tura wata k'ofar falor sannan ya tura ta ciki ya janyo k'ofar , Sanam ihu tasaka tana fad'in " menayi maka ne bawan Allah ? plss dan Allah kazo kafitar dani kabarni natafi gida , Huneed

yana jinta ya fito daga gidan yana huci , cikin motar ya koma ya zauna ya fara tunanin yadda zai hora Sanam ,......

Hisham tunda Huneed yamasa waya akan yazo ya d'auki motar Sanam , yana zuwa daya d'auketa gidan su ya nufa yaje ya ajiyeta wajen parking space , yana fitowa ya shiga cikin gida abinsa yana dariyar koya hankalin da Hauneed zai wa Sanam d'in ......

Diyana ce tashiga kiran wayar Sanam , lokacin Huneed yayi nisa a tunanin yadda zai fara horata yaji ring d'in waya , dubawa yayi yaga ansa My D katse wayar yayi sannan ya kashe ta gaba d'aya yayi jifa da ita bayan motar , fitowa yayi daga cikin motar yana nufar cikin gidan......
Yana shiga gidan ya bud'e k'ofar falon yashiga , lokacin ya cire face mark d'in sa da kuma glass d'in , Sanam ta zauna a k'asan cafet ta had'e kanta da gwiwa lokacin tana shan kukan ta , a lokacin taji shigowar sa da sauri ta d'ago kanta , aikuwa ido biyu tayi da Huneed ya had'e girar sama da k'asa yana tsaye yana kallon ta , da sauri ta mik'e tana dubansa kafin ta fara magana " me na tare maka a cikin rayuwa daka takura min haka ? menayi maka kake shiga cikin Rayuwa ta , kuka ne ya k'wace mata tana yi tana fad'in " wallahi bazan tab'a k'yaleka ba azzalumi kawai , wata tsawa Huneed ya daka mata wacce tasa Sanam yin shuru jikinta har rawa yake , Huneed ya k'araso gaban ta yace " keda kike mara kunya wacce bata san darajar mutane ba , sau nawa ina fad'a miki kigyara halinki amman kika yi min kunnar uwar shegu ? saboda kin samu sake har taka mutane kikeyi batare da and'au mataki akan ki ba , to kisani nine zan d'auki mataki yau akanki dan saina gyaraki tunda iyayenki sun kasa baki tarbiya , wani tsaki yaja tare da dubanta yace " Komai kikeyi aganinki dai dai ne ko ? shuru tayi batare da tabashi amsa ba , tsawa ya daka mata sannan yace " ina tambayarki kinyi min shuru wallahi yanzu jikinki zai gaya miki , kuka take k'asa k'asa yaci gaba da fad'in " meyasa bakyajin magana ? nan ma shuru Sanam tayi ba tare da ta Bashi amsa ba , fusata yayi yayi kanta ya d'agota da gashin kanta da ya baje a bayanta , wata k'ara ta saki tare da sakin fitsari .......

*Dan Allah kuyi hak'uri an hanani kallon hasken waya zuwa lokacin da zanji sauk'i sosai*
[9/27, 09:40] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association*💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 9.

Huneed ko ajikin sa yace " za kiyi magana ko ba zakiyi ba ? da sauri Sanam tace " zanyi wallahi zanyi , sakin ta yayi sannan yace " to ina jinki meyasa ba kyajin magana kuma Alhalin ke ba yarin ya bace ? Sanam tana kuka tana fad'in " kayi hak'uri duk abinda kake so nayi wallahi zanyi , dan Allah ka maidani gida plss , Huneed ya kalle ta fuskar ta jage jage da hawaye tamkar ba itace Sanam 'Yar gayun nan ba , jiyayi dariya na neman kamashi amman sai ya maze yace " daga yau inaso inga shedar kin fara jin magana ta , a ko yaushe ki kasan ce kina jan Motar cikin Nutsuwa , sannan ki girma ma duk wanda yakasan ce ya girmeki , sannan inaso ki daina irin wannan shigar mutuk'ar zaki fito yawan ki na gari , kuma inaso duk wad'an da kika buge su da Motar kije kine mesu ki basu hak'uri , nabaki nan da kwana biyu zanga in kinji magana ta , sosai Sanam take kuka har Huneed yaga ma magan ganunsa , jiyawa yayi ya kwaso mata wasu uniform d'in sa na Sojoji yace ta shiga toilet maza ta wanke masa sannan tazo ya maida ta gida , Sanam ba musu ta anshi kayan ta nufi cikin toilet tana share hawayen ta , tunda take a duniya bata tab'a wanki ba ko sau d'aya , komai sai dai tasa ayi mata amman yanzu lokaci d'aya ace wani yasa ta wanki , tana shiga toilet d'in tasa ka wani kukan tare da zuba kayan a cikin wani bawool na wanki , saka kayan tayi a gaba tana kallo tare da tunanin taya zata fara , gashi intace masa bata iya ba nan ma zaiyi mata wani rashin mituncinne , sabulu tagani a gefe a ajiye nan ta d'auka tafara wankin tana kuka.......

Tuni Hajiya Nafeesa ta kira K'anin ta a waya wato Fahad , suna waye take sheda masa duk abinda yake yabaro k'asar Cameroon yadawo gidan ta , tanaso tasaka shi aiki akan Sanam , tuni Fahad yafara shirin tahowa dan dama babu abinda yake sai bin mata kamar bunsuru , kud'i ta tura masa ya hawo jirgi ya sauka a garin Abuja......

Yana isowa ta tareshi da murna tare da nuna masa masaukin da zai dunga kwana , bayan Fahad yayi wanka ya shirya ya fito dan cin abinci , Hajiya Nafeesa tana zaune ta kame tasha wanka da kwalliya tamkar zataje gidan biki , zama Fahad yayi yana duban ta yace " gaskiya Aunty kin samu duniya sosai , dubi yadda kika koma tamkar wata shuwa arab , murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan ta dubesa tace " zaka fara rashin mutuncin naka ko ? yanzu dai kaci abinci sai muyi magana , Fahad yace " inacin abinci kina gayamin abinda duk kiso ayi miki , Hajiya Nafeesa ta gyara zama tace " inaso ka bud'e kunnen ka kaji sosai , kasan dai duk duniya banida kamarka ko ? to inaso kasan cewa duk wannan daular danake ciki da zarar Alhaji Abba ya rasu bani da wani kaso me yawa aciki , kasan ba haihuwa nayi dashi ba dan ni likita

ya tabbatar min da bazan haihuba saboda yawan zubar da cikin dana ringa yi ina budurwa , duk wannan dukiyar ta Alhaji a yanzu inya mutu duk rabinta ta zama ta Sanam , sai kuma uwar ta wacce take da wani cikin a yanzu , kaga ni zan tashi a tutar babu kenan , abinda yasa na kira ka dan ka tainaka min nima insamu kaso na me tsoka acikin dukiyar Alhaji , gashi tun yanzu babu abinda nake k'aruwa dashi , wannan shegiyar 'Yar tasa itace komai akan dukiyar yanzu , komai na dukiyar sa sunan tane ajiki kuma duk abinda takeso to tabbas sai ya mallaka mata shi duk tsadar sa , inaso kashiga jikinta ka k'ullah soyayya da ita yadda zaka dunga kwaso mana rabon mu , ta wannan hanyar kawai zamu samu kud'i yadda mukeso , wani murmushi Fahad yayi sannan yace " ina yinki Auntyna tabbas kin yi kyan kai , nikuma bazan baki kunya ba duk yadda zanyi nashiga rayuwar Sanam sai nayi , daman ina masifar sha'awar yarinyar , dan naga tana da Albarkatun ruwa atare da ita , wata harara Hajiya Nafeesa ta watsa masa tana fad'in " kana nan da halin naka kenan ? sosa k'eya yayi yana fad'in " to mezan fasa Aunty ai mata duniya ce dole sai dasu rayuwar zata tafi.......

Sanam sosai tasha wuya a wajen wankin sannan ta fito tace ta gama , duban ta Huneed yayi sannan ya kauda kai yana fad'in " kishiga kiyi wanka sai nazo na maidaki dan bazaki shigar min motar a haka ba , wani takaici ne ya kuma kama Sanam batare da tace komai ba ta juya cikin toilet d'in.....

Tana fitowa tasame sa a tsaye yace " taho mu wuce , yana fad'in haka ya juya ya fita daga cikin falor , binsa tayi a baya har ta fito daga gidan tasame sa a k'ofar gidan yana tsaye jikin motar , tana zuwa ta bud'e baya zata shiga Huneed yace " ni direban ki ne da zaki zauna min abayan motar ? maza ki dawo gaba ko ranki ya b'aci , da sauri Sanam ta dawo gidan gaba ta zauna shikuma ya zagaya yaja su suka tafi....

tunda suka fara tafiya yake waya yana musayar kalmomin soyayya shida budur warsa , wani ta kaici ne ya kama Sanam wato ita yagama horata shikuma gashi nan sai wani farin ciki yake abinsa , wani murmushi yasaki yana fad'in " kinsan Allah na matsu sosai na ganki , gaskiya kiyi ki tattaro ki dawo Nageria , ko mai akace masa daga can b'angaren yace " habawa ai ba wacce ta isa ta kwace miki ni , kinsan matan Abujan yawancin su duk garorine , gasu da rashin tarbiya uwa uba kuma akwai su da iya bin saurayi , Sanam ji tayi tamkar ta rufesa da duka dan tasan wannan magan ganun da ita yake , haka ta k'yalesa tanaji yana ta zubawa Budurwar sa luv , har wata shagwab'a yake yi mata tamkar k'aramin yaro , a haka har suka k'araso cikin Estate d'in su , lokacin har ankira sallar magriba haka ya ajiye Sanam tare da cewa " daga yau nake so naga kinfara aiki da abinda nace miki , rashin hakan zai tabbatar min da cewa bakiji magana ta ba , rashin jin magana ta kuma tamkar kin k'ara ansar hukunci na ne , kuma inaso kisani in ma kin fad'awa Iyayenki babu abinda aka isa ai min sai dai ma ki saka kanki a wata babbar matsalar , in kunne yaji to jiki ya tsira zaki iya fita sai wani lokacin , A hankali Sanam ta bud'e motar ta fice batare da tayi magana ba , tana fita ya ja motar sa da gudu ya nufi gidan su dan sauri yake yaje yayi sallah tunda ankira........

Lokacin da Sanam ta zo k'ofar gate bugawa tayi da hannun ta , megadi yana sallah lokacin

haka ta ci gaba da bugu har ya idar yazo ya bud'e mata , yana ganinta ya zube yana fad'in " kiyimin rai hajjaju wallahi sallah nake shiyasa banzo na bud'e ba , kuma banji k'arar motar ki ba shiyasa tuba nake , wuce wa tayi batare da tace masa kanzil ba har ta shige k'ofar falor su , binta yayi da kallo yana mamakin yanayin ta , cikin ransa yana addu'ar Allah yasa dai lafiya .......

Sanam na shiga cikin falor sukayi ido biyu da Fahad , da sauri ya mik'e yana fad'in " Oyoyo my Special ina kikaje haka ? tunda nazo nake cigiyar ki banji kiba , daurewa kawai Sanam take dan kanta ne yake ciwo sosai , murmushi tayi sannan a hankali ta furta " na d'an je gidan su k'awata ne dafatan kazo lafiya , Fahad ya rik'o hannun ta yana fad'in " lafiya lau nazo My Special me yasa me kine naganki haka ? Sanam ta zame hannun ta a hankali tana fad'in kaina namin ciwo bari na hau sama , bata jira amsar da zai bata ba ta haye sama abinta......

Da ido Fahad yabi bayan ta ana had'iyar wani mugun miyau , cikin ransa yake yaba tsarin halittar da Allah yayi wa Sanam , dan duk iya yawon dayayi k'asa she baiga mace me dirin jikin Sanam ba , dan haka ko tak'i ko taso dole yasha romonta .......

Huneed yana shiga gida ya fad'a toilet yayi wanka tare da d'auro arwala , yana fitowa ya nufi masallaci lokacin har sun tada sallah , bayan an idar yayi lazimin sa da yasa ba sannan ya taso ya shigo cikin gida abinsa , samun Hajiyar su yayi ita da Hisham suna hira abinsu cike da so da k'auna , shima zama yayi suka ci gaba da hirar abinsu , sai bayan sallar isha'i sannan suka ci abinci ya fito , Hisham ne ya biyosa yana cewa " wai Ya Huneed yaya ta kasance kai da Sanam ? murmushi Huneed yayi sannan yace " nakuma saka mata doka ta biyu inaso naga yadda zata kuma karya ta , murmushi Hisham yayi yana fad'in " Wannan yarinyar kuwa zata iya bin doka ? amman bari dai mugani nan da gobe ko zata iya , Huneed yace " inaso ka d'auki motar ta ka kaimata gidan su ga wayar ta nan ka had'a mata da ita , Hisham yace " to shikenan bari na kai mata na dawo , Huneed ya shiga motar ya fice dan akwai wasu aiki da xaije dubawa........

Koda Hisham yakai motar gidan me gadi yabawa yace ya shigar mata dasu , me gadi ya ansa da mukullin da wayar ya nufi cikin gidan dasu .......

Tunda Sanam ta hau sama wanka taje tayi ko sallah batayi ba ta haye gado ta kwanta , sai dai me tana rufe idon ta hoton Huneed ne ke yawa a cikin idanun ta lokacin da ya ke fincikar ta yana shiga da ita cikin gidan , hawaye ne taji yana bin kuncin ta tabbas Huneed ya karya mata record d'in ta , itace harda yin fitsari itace har dayin wanki , ga uwa uba kukan data sha tamkar ranta zai fita , tabbas batason dame zata rama abinda Huneed yayi mata ba , tunani tatafi akan yadda zata rama abinda yayi mata har bacci yayi gaba da ita......

Fahad ne ya hawo sama dan kawo mata wayar ta da mukullin motar , yana shigowa d'akin

nata yaganta tana bacci duk ilahirin cinyoyin ta a waje , gashi saman k'irjin ta ya bayyana duk da gashin kanta ya rufe wani wajen ,  wani miyau ya had'iya tare da nufo gadon yana jin D d'insa na mik'ewa ,  Hawowa yayi cikin sand'a tare da nufar ta dan yadda yakejin kansa bazai iya rik'e sha'awar saba , turo k'ofaf da akayi shine ya dakatar dashi yana wai wayen yaga waye wanda yashigo..........

*Bana ganin Comment fa*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR  KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter    10.

Hajiya Nafeesa yagani tsaye a bakin k'ofa , sauko wa yayi daga gadon yana sosa k'eya , duban sa tayi tace " me zakayi mata ? k'asa yayi da kansa yana fad'in " sorry My Aunty babu komai kawai yarinyar ce tahad'u sosai ,  Hajiya Nafeesa tace " amman karka manta yau fa kazo kabari aikin da zamuyi yafara tafiya , yanzu in ka haike mata sai ka b'ata komai na shirin

namu , Fahad yace Shikenan za'a kiyaye hakan insha Allah , fitowa sukayi daga d'akin tare da janyo mata k'ofah suka sakko.....

Washe gari .
Sai wajen k'arfe sha d'aya Sanam ta sauko cikin kwalliya tare da trolly ta matafiya , lokacin Hajiya Nafeesa da Fahad suna zaune a falor suna hira , suna ganin ta suka tsaya suna kallon ta , dan iya had'uwa Sanam ta had'u tamkar itace ta tsara kanta , sai da ta k'araso sannan suka d'auke kansu da ga kallon ta , Sanam ta k'araso jikin Hajiya Nafeesa ta rungume ta sannan tace " Mumy yau zanbar k'asar nan inaso tafiya Turkey saboda zuwa na da wuri yana da amfani , Hajiya Nafeesa jitayi kamar ta shak'e Sanam d'in kowa ya huta , a fili kuma tace " haba My Dauther kibari mana bikin yataho basai ki tafi ba , kodai wani abun akayi miki da kikeson guduwa kibar mu ? Sanam a cikin ranta take fad'in " tabbas ina buk'atar yin tafiyar kwana biyu ko dan wannan azzalumin mutumin , mutuk'ar tana gari to tabbas zata biya ko nawa ne aje a kashe mata shi , tunda take a rayuwa ba'a tab'a yi mata abinda yayi mata ba , shurun da tayi ne yasa Hajiya Nafeesa fad'uwar gaba , cikin ranta take ayyana kodai Sanam tajisu jiya da daddare ne ? da sauri ta dubi Fahad tayi masa wata inkiya da idanu , shima hakan yayi mata sannan Hajiya Nafeesar ta katse shurun da cewa " Haba My Dauther na d'auka ina da muhimman cin da zansan dukkan damuwar ki ? ashe ba haka bane ! idan wani ne ya shigar miki rayuwa yana da kyau ki fad'amin mud'au mataki akansa , Sanam tace " babu komai fa Mumy kawai inaso in tafi da wuri dan Rauda tace sainaje zatayi komai , wata a jiyar zuciya tayi sannan tace " to shikenan hakan ma yayi kyau , yanzu yadda za'ayi ki kira Daddyn ki ki sheda masa kin janyo tafiyar yau kikeso , in kina buk'atar rakiya ga Uncle d'in kinan sai yaraka ki , Murmushi Sanam tayi sannan tace " munyi waya da Daddy tunda asuba kuma ya amince intafi yau , Fahad yace " to bari na had'o kayana mutafi tare nima naga gari , murmushi Sanam tayi sannan tace " Uncle ai dama kayi zamanka tunda nima ba wani dad'ewa zanyi ba , kuma kai daka zo hutawa ai baka kuma shan tafiya ba , Sanam kwata kwata jininta bai had'u da Fahad ba , tun tana k'arama in yazo gidan bashi da aiki sai rungumar ta da yi mata wasanni wad'an da bata so , dan haka bata shiri dashi ko yaushe ta gansa sai ta tsiri fita kullum.....

Ganin Sanam bata son tafiya da Fahad yasa Hajiya Nafeesa tace " to shikenan amman yana da kyau kije gidan Hajiya Maimuna kiyi mata sallama , Sanam tace " sauri nake Mumy kuma yanxu haka saura minty sha biyar jirgin mu yatashi , tana fad'ar hakan ta mik'e daga jikin Hajiya Nafeesa tana fad'in " Miss u so much my Mumyna , bye sai munyi waya ki kula min da kanki Mumyna , Hajiya Nafeesa cike da kissa tace " Miss u so much my luvly Allah yatsare min ke , Fahad ya mik'e yana fad'in " kawo trolly d'in naki na rakaki airpot d'in tunda ba'ason nayi rakiyar can d'in , murmushi Sanam tayi sannan tace " haba Uncle kana Abbana zan baka rik'on Trolly ? kabar shi kawai ai ina fita zansa a bayan mota , haka suka fito dukan su har jikin mota sannan Fahad ya shiga wajen direba ya zauna tare da cewa ta shigo ya kaita airpot d'in , sake rungume ta Hajiya Nafeesa tayi sanna tayi mata adawo lafiya ta shiga motar Fahad yaja suka tafi.......

Huneed koda yaje bacci kasa bacci yayi saboda tunanin Sanam , tabbas yarinyar tafara

shiga ransa , sai dai gaskiya yanayin tarbiyar ta baya burgesa ko kad'an , inda zai ga iyayen ta tabbas sai yayi musu gyara sosai a cikin rayuwar su , dan yakamata ace sun bata tarbiyar da za'ayi alfahari da ita a matsayin ta na 'Ya mace , a haka bacci yayi awon gaba da shi me cike da mafarkin Sanam kala kala......

Washe gari wajen sha d'aya na safe ya fito waje yana zaga Estete d'in nasu , can ya hango motar Sanam tataho a hankali batare da wannan gudun na hauka ba , mamaki ne ya kamashi na ganin tabbas ta fara d'aukar horonsa , bai gama tunani ba motar tazo giftawa ta kusa dashi , anan ya hangi wanda yake tuk'in ashe ba Sanam d'in bace , sai dai itama ya hango ta tana cikin motar tana danna wayar ta , cikin ransa yake fad'in " wannan d'in shikuma waye ? take wani kishi ya ziyarce shi wanda bai tab'a jinsa ba ko akan Fateema wacce zai aura , da sauri ya nufi cikin gidan su dan d'auko motar yabi bayan su dan kwata kwata bai yadda da guy d'in ba .......

Fahad suna tafe yanajin music ya dubi Sanam yace " Baby yanzu kuma sai yau she zaki dawo ? Batare da ta dube sa ba tace " inason inyi 2 weeks kawai , in kuma na zarta to babu laifi dan can ma gidane , Fahad yace " gaskiya bazan iya jure rashinki har 2 weeks ba , ki taimaka min kiyi 1 weeks kidawo kinji Baby , murmushi Sanam tayi tare da mamakin maganar Fahad d'in , a cikin ranta tace kaji mun Uncle sai kace wata budurwar sa wai zai yi missing d'ina , a fili kuma tace " kamar yaune ai Uncle kuma ai zamuyi waya , Fahad yawani shagwab'e baki tamkar yaro yana fad'in " My BBy ki kulamin da kanki karki kula kowa kinji , Sanam tace " zan kula . Daga haka tayi shuru bata sake magana ba har suka k'araso air pot......

suna zuwa dai lokacin aka fara kiran sunayen matafiya , Daddyn ta ta hango yana murmushi ya nufo ta bayan sa body quart suna biye dashi , da sauri ta nufi wajen daya ke itama tana murmushi , tana zuwa ta fad'a jikin sa ya rungume ta sanna yace " bazan iya zama banzo munyi sallama da My One and Only d'ina ba , Murmushi Sanam tayi tana fad'in " nasan hakan Daddyna Abin k'auna ta , jin ankira sunan ta yasa ta saki Daddy tana fad'in " Miss u my Daddy so much , ta sumbace shi a kunci sannan ta nufi hanyar wajen hawa jirgin , tanayi tana wai wayen su tana d'aga musu hannu har ta k'ule......

Duk abinda akeyi Huneed na tsaye yana kallon Sanam har ta k'ule , cikin ransa ya furta " wato zaki bar k'asar kenan kije ki k'ara koyo wasu banzayen halayyar , duban wajen dasu Daddyn nata suke yayi suna tsaye har lokacin suna magana da Fahad , takawa Huneed yayi har wajen da suke yayi musu sallama tare da gaisar da Daddy , amsawa yayi cike da kulawa yana fad'in " kamar Canal Huneed Abdallah ko ? Huneed yayi murmushi sannan yace " nine , Daddy yace " masha Allah ya fama da gwagwar maya ? kuna k'ok'ari sosai Allah yabiya ku , Huneed yace " Ameen ya Allah nagode da addu'a , nan suka wuce shikuma ya tsaya yana dube dube , Huneed ya tsaya ne yana son sanin wacce k'asa Sanam tatafi ? yanaso yasan k'asar da zataje da kuma dalilin ta na tafiya , cikin wajen ya shiga ya nufi office d'in ma'aikatan jirgin , yana zuwa dayake dayawa sun san shi bai sha wata wahala ba suka sanar dashi garin da jirgin ya nufa , take Huneed yasamu kansa da biyan kud'in visar k'asar Turkey shima

zaije......

*Tofah Sanam kinsamu cingum*

Tunda Sanam ta isa garin Turkey takejin wani nishad'i na ratsa ta , ba komai take tunawa ba sai rayuwar datayi a garin , tuni Rauda sunzo airpot d'aukar Sanam dan ta sanar mata da zuwan ta , ai suna ganin juna Sanam suka fara murna tare da tahowa da gudu suka rungumi junan su ......

*Comment plss*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/27, 09:42] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 11.

Rauda ta dubi Sanam tace " kinga yadda kika koma kuwa ? murmushi Sanam tayi sannan tace " haba my R ke bakiga yadda kika koma ba saini , Rauda ta rik'e mata hannu tana fad'in " aini dole na canza tunda nasha gyara haryanzu ina shan gyaran , haka suka k'arasa wajen motar cike da so da k'auna suna tafe suna hirar yaushe gamo .......

Rauda k'awar Sanam ce tare sukayi karatu tun datazo turkey , sun shak'u sosai har takai

iyayen su sun san da wannan shak'uwa tasu , Iyayen Rauda 'yan asalin Nageria ne amman suna zaune a Turkey anan suke aikin su , da Ammin ta da Abeeh duk likitocine shiyasa suke zaune a Turkey suna aiki , Yaran su biyu suka haifa Asuk' da Rauda suna bala'in k'aunar 'yayansu...

Suna k'arasawa gidan su Rauda aka fara murna da zuwan Sanam , duk wanda yake Family d'in su Rauda sai yasan Sanam saboda shak'uwar su , Ammi tana murmushi tace " oyoyo my dauther , Sanam tafad'a jikin Ammi tana fad'in " nayi kewarki Ammi dakuma kewar daddad'an girkin ki , dariya suka saka baki d'aya Ammi " tana fad'in " kwantar da hankalin ki indai girki nane gashi can a dinning yana jiranki tund'azu , da sauri Sanam ta nufi dinning tana fad'in "dama yunwa nakeji banci komai a cikin jirgi , tana zuwa ta janyo kujera ta zauna tana cewa Rauda " zokiyi serving d'ina yunwa nakeji , Rauda ta nufo wajen tana fad'in " girman kine ai dole nazo nayi .......

Huneed yana zuwa gida yafara shirin tafiya , Hajiyar su yaje yiwa sallama yana fad'in " tafiya ce tazomi zuwa k'asar Turkey amman ba jimawa zanyi ba , Hajiya tayi masa addu'ar Allah yatsare shi yayi mata sallama ya fito , wayar Hisham ya shiga kira yana sheda masa tafiya tazo masa zai tafi Turkey amman ba jimawa zaiyi ba , zai saka masa kud'i a Account saboda ko zasu buk'ata shi da Hajiya , Hisham yayi masa fatan Allah yatsareshi sannan sukayi sallama , Huneed yashiga motar sa yabata wuta ya nufu airpot , yana zuwa visar sa na fitowa aka ce masa zuwa yamma jirgin su zai iya tashi ..........

Bayan Sanam taci abinci tanufi d'akin Rauda ta fad'a toilet tayi wanka , tana fitowa Rauda ta shigo tana fad'in " kinsan mungama shiryawa ke kad'ai muke jira , Ammi cewa tayi wai mutafi mubarki ki huta tunda yanzu kika zo ya kikagani , Sanam tana shafa mai tadubi Rauda tace " ai babu gajiya atare dani kawai kujirani insa kaya sai nafito mu wuce dan inaso inzaga gari tunda nadad'e banga garin ba , Rauda tajuya tanufi fita tana fad'in " muna jiranki cikin motar sai kin fito , Sanam tana gama shafa mai tasa kwalli daman bawata kwalliya tacika yiba , kayan ta ta bud'e ta d'auko wasu riga da wando bata tab'a sasu tasaka abinta , ta d'auko filet shoe da hand bag d'in ta iri d'aya , sai wani k'aramin gyale ta yafa ta fesa turare me tsadar gaske , agogon gold d'in ta ta d'aura a tsintsiyar hannun ta ta fito ....

Tana zuwa falor sukayi karo da Asuk' yayan Rauda , da kallo yabi Sanam tamkar tsohon maye har wani kashe ido yake , tana k'arasowa tayi tamkar bata gansa ba dan dama tuntuni haka suke kowa naji da miskilan cin sa , wanda ma yanzu Asuk' shi ya sauko bakamar da ba , har ta gifta yace " manyan mata saukar yaushe ? Sanam batare da ta juyowa ba tace " saukar d'azu dafatan kana lafiya , daga haka bata jira cewar saba ta fice abinta , da kallo Asuk' yabi k'ugunta cikin ransa yana kiyasta yadda zai sarrafa ta mutuk'ar tashigo hannun sa , wani murmushi yayi tare da shigewa cikin d'akin sa....

Sanam tana fitowa k'awayen Rauda suka bita da kallo suna fad'in " wow so beautifull lady ,

wani murmushi Sanam tayi tana wani jin kanta , dan dama burin Sanam arayuwa ayabi kyanta sannan a girma mata , tana k'arasowa tace " My R nice fa zanyi drivernig dan inaso asan Sanam tazo garin Turkey yau , Rauda tayi murmushi sannan tace " wato haryanzu wannan halin naki yana nan nasan gudu sosai a motar ? Sanam tana ansar mukullin motar tana cewa " mezan fasa haryanzu yana nan kuwa , dukansu suka shiga mota Sanam taja da wani mugun gudu suka fita .......

Huneed sai hud'u sannan jirgin su yataso zuwa Turkey , yana cikin jirgi yafara tunanin ko a inah Sanam ta sauka ? tabbas zaiyi bincike sosai har sai yagano inda tasauka , sai wajen k'arfe goma suka sauka a airpot d'in k'asar Turkey , suna isowa yasauka a wani Babban Hotel dake cikin garin , sai da yagama kintsawa sannan yafito ganin gari , dan yasan sai dare ake fitowa yawo a k'asar Turkey , kuma yana da tabbacin lallai Sanam zata fito ganin gari itama , yana fitowa ya nufi shopping d'in k'asar wanda akeji dashi sosai , yana zuwa wajen shiga yaji k'amshin turaren Sanam , tabbas wannan turaren yasan Sanam ce take sakashi kuma yana da tabbacin tana wajen , bai gama tunani ba yagan su sunfito ita da k'awayen ta suna wata mahaukaciyar dariya , da sauri ya b'oye a jikin bishiya dan bayason tasan yazo garin yanzu har sai ta saki jiki zai bayyana mata kansa yazo , yana hangosu suka shige motar kuma itace ta zauna a b'angaren tuk'i , da sauri ya tsaida motar ya hau yana fad'in " kabi mun wannan motar dake gaban mu duk inda tayi , da turanci yayi maganar direban yafara bin motar su Sanam , wani gudu tashiga yi tamkar zasu tashi sama , shima direban binsu yashiga yi da gudu yana fad'in " wannan gudun yayi yawa sosai , Sanam tuni tashiga wana motar tamkar wacce ta sha k'waya take tangad'i , Huneed wani takaici ne ya rufe sa cikin ransa yake fad'in " wato wannan yarinyar bazata gyaru ba kenan ? a k'asar da bata ta ba ma saita yi musu wannan iskancin nata , tabbas zata gane shayi ruwa ne dan sai ya koya mata hankali wannan lokacin .........

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪

https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 12.

Allah ne kawai yakai su Rauda gida lafiya , dan dukansu sai da suka jigata da tuk'in da Sanam takeyi , suna fitowa kowannen su ya fara tari na wuya , ita kuwa dariya ta dunga yi musu tamkar wata zararriya , bayan sun lafa da tarin da sukeyi wata daga cikin k'awayen Rauda tace " a gaskiya kina da matsala bazan k'ara shiga motar ba mutuk'ar kece zakiti driver , Rauda tace " wai dama har yanzu Sanam baki daina wannan gangancin naki ba kenan ?  wallahi sanake in kika k'ara girma zaki dai na ashe ba haka bane abun ,  Allah ya shirya ki wallahi nan k'asar ba kamar Nageria bace kidaina kar aka maki ,  murmushi Sanam tayi tare dayin tsalle ta haye saman motar ta dube su tace " babu ruwana da nan Nageria ce ko ba Nageria ba dole nayi yadda nake so a duk inda naje , matsora ta kawai duk kun wani firgice wlh kunbani dariya , haushi bai sa sun k'ara mata magana ba suka shige sukayi tafiyar su cikin gida......

Sanam na zaune a samon motar wayar ta ta soma ruri , d'auko wa tayi tana duba screen d'in wayar dan ganin waye yakira ta , Daddyn tane  da sauri ta d'aga wayar tana fad'in " Miss u my luvly Daddy , shima cike da k'auna yace " My Dauther dafatan kin sauka lafiya ? lafiya lau Daddyna ina Mumy na take ? Alhaji Abba yace " ina gidan d'aya Mumyn naki gata ku gaisa , daman baki mata sallama ba kika taho , dan danan Sanam ta turo baki tamkar tana ganin su tace " Daddy nifa bance kabata wayar ba kasan ba sona takeyi ba ,  Hajiya Maimuna da wayar take a kunnen ta tuntuni ji tayi maganar ta doke ta , cikin ranta tace " duk wanda zai soki a duniya bayana yake , nice wacce na d'auki cikin ki har na haifeki kika girma kika zama hakan , Maganar Sanam d'in ce ta katse ta daga tunanin datake tace " ba Daddyn naki bane nice , Sanam cike da jin haushi tace " kinyini lafiya ? Hajiya Maimuna tayi murmushin takaici wai 'Yar da ta haifa ce keyi mata irin wannan gaisuwar , kashe wayar tayi batare da ta ce uffan ba ta mik'awa Alhaji Abba wayar sa tamik'e tabar gurin .......

Sanam najin Hajiya Maimuna ta kashe wayar ta tab'e baki tare da fad'in " huta roro , saukowa tayi daga kan motar ta nufi cikin gidan Itama ......

Duk abinda Sanam keyi Huneed na tsaye yana kallon ta , har ta shige cikin gidan sannan yasa me taxi ya maida shi hotel d'in daya sauka ,   koda ya koma hotel d'in band'aki ya shiga yayi wanka sannan ya fito ya anso abinda zai iya ci yadawo ,  yana cin abincin yana tunanin yadda zai gyara Sanam tunda ya fahimci batajin magana sosai ,  haka ya gama batare da ya

yanke me zaiyi mata ba ya kwanta dan ya huta......

Washe gari..

Yau akeyin Bridel Shower dan haka tunda suka tashi suka fara shirye shirye , Sanam na zaune sai faman chat take da Diyana suna labarin k'awayen su , sai wajen k'arfe biyu ta tashi tayi wanka sannan ta fito ta shirya cikin wata riga wacce suka d'inka duk iri d'aya , sosai kayan sukayi mata kyau dan dama Sanam akwai kyau na tamkar itace ta k'era kanta , gashin ta dayake a baje a gadon bayan ta ta kamo tasa masa ribon kalar rigar data saka , sannan ta saka wani hils d'in takalmi me tsinin gaske , kwalliya bata dami Sanam ba sai dai tana saka kwalli wanda ke k'ara fito da kyawun idanunta masu kama da madara , fitowa tayi palor tuni mutanen dake zaune cikin falor suka saki bakin kallon ta , Ammin Rauda tana duban ta tace " wow my Beautifull queen , murmushi Sanan tayi wanda siririyar wushiryar ta ta fito tare da dimple d'inta ya lotsa , ai take suka rud'e sai cewa suke " wow so beautifull nice , aikuwa Sanam tasamu abinda takeso wato a fasa mata kai ace tana da kyau , wani yauk'i tashiga yi har ta fito harabar gidan , lokacin Abokan Ango sunfara zuwa d'aukar su dan kaisu wajen Party , suna ganin Sanam kowanne ya kafeta da ido suna k'arewa k'ugunta kallo da k'irjin ta , wanina ciki yace " wannan Babyn ta had'u sosai dama zata yarda tabani dare d'aya dana mallaka mata duk abinda takeso , dukan su suka shiga yabon halittar Sanam wacce ta tsaya gefe d'aya tana danna waya da alamar kiran wani zatayi .......

Huneed tunda gari ya waye ya shirya ya shiga gari , sai wajen biyu da rabi yasamu kansa da son zuwa gidan da Sanam ta sauka , dai dai lokacin dayazo a dai dai lokacin Sanam ta fito da wannan shiga , bayan wata bishiya ya lab'e ya saka face mark d'in sa da glass yana lek'owa , ganin yadda maza ke kallon Sanam hakan ya kuma b'ata masa rai over , cikin ransa yace " wai wannan yarinyar anya mutum ce kuwa ? sai kace shaid'aniya zatayi irin wannan shigar , tamkar ma ba musulma ba dubi jikinta ko d'ankwali bata saka ba , Asuk' ne ya fito daga motar ya nufo wajen Sanam , tana zuwa yayi hugging d'in ta batare da ta kula dashi ba , tuni mutanen dake gurin suka fara yin tafi suna jinjina masa yadda yayi hakan , Huneed nadaga bayan bishiya jiyayi juwa na neman kamashi , wani abu yaji ya tokare masa a k'irjin sa tamkar numfashin sa zai tsaya haka yaji , Sanam jin yadda Asuk' ya rungume ta yasa ranta yayi mugun b'aci , k'arfin ta ta had'a guri guda ta hankad'ashi gefe , tana yin hakan tayi saurin komawa cikin gidan dan yagama b'ata mata rai over , Asuk' sosai yaji haushin abinda tayi masa dan har bige kansa yayi jikin motar , dan haka shima cikin gidan yabita.......

Huneed take ya yanke shawarar mutuk'ar Sanam tafito to sai ya d'auke ta , dan ya fuskan ci wannan guy d'in zai iya yimata komai yadda ya fusata , kuma shima bazai so ace ko d'an yatsan ta wani banza yasake rik'ewa ba , haka ya zauna zaman jiran fitowar ta , yana zaune motoci suka fara wucewa dan tafiya gurin Kamu , kwata kwata bai ga Sanam ta fito ba har ya tashi yafara nufar cikin gidan dan ganin me takeyi , lokacin kowa yatafi wajen party har Ammin su Rauda da k'awayen ta itama , ita kuwa Rauda dama tuni suna can ana shirya ta daga can za'a wuce sa ita , yana tsaye yana kai kawo a harabar cikin gidan sai ga Sanam da gudu ta fito

tana kuka rigar ta duk ta yage ana ganin jikinta , bayan ta Asuk' ne daga shi sai gaje ran wando ya biyota da gudu shima , wajen Huneed ta nufo tana fad'in " dan Allah ka taimaka min wallahi d'an iska ne , wani mari Huneed ya tsinka mata sannan ya janyo hannun ta ya kawo ta wajen Asuk' dake tsaye yana kallon su yace " gatanan kayi mata duk abinda kakeso kayi , mamaki ne yaka ma Sanam tafara Nazarin a inah tasan wannan muryar ? Asuk' ya rik'e hannun ta tare da cewa " Huneed thank u Yana k'ok'arin janta ya shigar da ita cikin gidan , kwata kwata Sanam bata ceton kanta take ba so take ta tuna muryar waye wannan dan tabbas tasan muryar kuma taji ta ba sau d'aya ba , juyawa Huneed yayi yana dafe kansa yayin da Asuk' yake jan hannun Sanam zai shiga da ita cikin gidan , ita kuma tana wai wayen Huneed tana son sanin waye shi ? gab da zasu shiga k'ofar falor Huneed yace " Stop dawata murya wacce tasa dukan su suka firgita , tuni Asuk' yasaki Hannun Sanam yana duban Huneed wanda ya nufo su gadan gadan tamkar zaki , yana zuwa yashiga duka Asuk' yana fad'in " rungumar da kayi mata baiyi ba sai ka ai ga keta mata haddi , mara tarbiya kawai wawa jaki , sai dukan sa yake tamkar zautacce haka yakoma , tuni ya sumar da Asuk' sannan ya waiwayo kan Sanam wacce tagama tsurewa jikin ta sai rawa yake , yana zuwa yajanyo hannun ta batare dayayi magana ba har suka fita daga gidan suka nufi titi , tunda ya rik'e mata hannu ta tuno da ko waye , Huneed bai saki hannun Sanam ba har sai da suka isa Hotel d'in dayake suka shiga har cikin d'akin daya kama ...........

*Comment plss*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/27, 09:44] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 12.

Allah ne kawai yakai su Rauda gida lafiya , dan dukansu sai da suka jigata da tuk'in da Sanam takeyi , suna fitowa kowannen su ya fara tari na wuya , ita kuwa dariya ta dunga yi musu tamkar wata zararriya , bayan sun lafa da tarin da sukeyi wata daga cikin k'awayen Rauda tace " a gaskiya kina da matsala bazan k'ara shiga motar ba mutuk'ar kece zakiti driver , Rauda tace " wai dama har yanzu Sanam baki daina wannan gangancin naki ba kenan ? wallahi sanake in kika k'ara girma zaki dai na ashe ba haka bane abun , Allah ya shirya ki wallahi nan k'asar ba kamar Nageria bace kidaina kar aka maki , murmushi Sanam tayi tare dayin tsalle ta haye saman motar ta dube su tace " babu ruwana da nan Nageria ce ko ba Nageria ba dole nayi yadda nake so a duk inda naje , matsora ta kawai duk kun wani firgice wlh kunbani dariya , haushi bai sa sun k'ara mata magana ba suka shige sukayi tafiyar su cikin gida......

Sanam na zaune a samon motar wayar ta ta soma ruri , d'auko wa tayi tana duba screen d'in wayar dan ganin waye yakira ta , Daddyn tane da sauri ta d'aga wayar tana fad'in " Miss u my luvly Daddy , shima cike da k'auna yace " My Dauther dafatan kin sauka lafiya ? lafiya lau Daddyna ina Mumy na take ? Alhaji Abba yace " ina gidan d'aya Mumyn naki gata ku gaisa , daman baki mata sallama ba kika taho , dan danan Sanam ta turo baki tamkar tana ganin su tace " Daddy nifa bance kabata wayar ba kasan ba sona takeyi ba , Hajiya Maimuna da wayar take a kunnen ta tuntuni ji tayi maganar ta doke ta , cikin ranta tace " duk wanda zai soki a duniya bayana yake , nice wacce na d'auki cikin ki har na haifeki kika girma kika zama hakan , Maganar Sanam d'in ce ta katse ta daga tunanin datake tace " ba Daddyn naki bane nice , Sanam cike da jin haushi tace " kinyini lafiya ? Hajiya Maimuna tayi murmushin takaici wai 'Yar da ta haifa ce keyi mata irin wannan gaisuwar , kashe wayar tayi batare da ta ce uffan ba ta mik'awa Alhaji Abba wayar sa tamik'e tabar gurin .......

Sanam najin Hajiya Maimuna ta kashe wayar ta tab'e baki tare da fad'in " huta roro , saukowa tayi daga kan motar ta nufi cikin gidan Itama ......

Duk abinda Sanam keyi Huneed na tsaye yana kallon ta , har ta shige cikin gidan sannan yasa me taxi ya maida shi hotel d'in daya sauka , koda ya koma hotel d'in band'aki ya shiga yayi wanka sannan ya fito ya anso abinda zai iya ci yadawo , yana cin abincin yana tunanin yadda zai gyara Sanam tunda ya fahimci batajin magana sosai , haka ya gama batare da ya yanke me zaiyi mata ba ya kwanta dan ya huta......

Washe gari..

Yau akeyin Bridel Shower dan haka tunda suka tashi suka fara shirye shirye , Sanam na

zaune sai faman chat take da Diyana suna labarin k'awayen su , sai wajen k'arfe biyu ta tashi tayi wanka sannan ta fito ta shirya cikin wata riga wacce suka d'inka duk iri d'aya , sosai kayan sukayi mata kyau dan dama Sanam akwai kyau na tamkar itace ta k'era kanta , gashin ta dayake a baje a gadon bayan ta ta kamo tasa masa ribon kalar rigar data saka , sannan ta saka wani hils d'in takalmi me tsinin gaske , kwalliya bata dami Sanam ba sai dai tana saka kwalli wanda ke k'ara fito da kyawun idanunta masu kama da madara , fitowa tayi palor tuni mutanen dake zaune cikin falor suka saki bakin kallon ta , Ammin Rauda tana duban ta tace " wow my Beautifull queen , murmushi Sanan tayi wanda siririyar wushiryar ta ta fito tare da dimple d'inta ya lotsa , ai take suka rud'e sai cewa suke " wow so beautifull nice , aikuwa Sanam tasamu abinda takeso wato a fasa mata kai ace tana da kyau , wani yauk'i tashiga yi har ta fito harabar gidan , lokacin Abokan Ango sunfara zuwa d'aukar su dan kaisu wajen Party , suna ganin Sanam kowanne ya kafeta da ido suna k'arewa k'ugunta kallo da k'irjin ta , wanina ciki yace " wannan Babyn ta had'u sosai dama zata yarda tabani dare d'aya dana mallaka mata duk abinda takeso , dukan su suka shiga yabon halittar Sanam wacce ta tsaya gefe d'aya tana danna waya da alamar kiran wani zatayi .......

Huneed tunda gari ya waye ya shirya ya shiga gari , sai wajen biyu da rabi yasamu kansa da son zuwa gidan da Sanam ta sauka , dai dai lokacin dayazo a dai dai lokacin Sanam ta fito da wannan shiga , bayan wata bishiya ya lab'e ya saka face mark d'in sa da glass yana lek'owa , ganin yadda maza ke kallon Sanam hakan ya kuma b'ata masa rai over , cikin ransa yace " wai wannan yarinyar anya mutum ce kuwa ? sai kace shaid'aniya zatayi irin wannan shigar , tamkar ma ba musulma ba dubi jikinta ko d'ankwali bata saka ba , Asuk' ne ya fito daga motar ya nufo wajen Sanam , tana zuwa yayi hugging d'in ta batare da ta kula dashi ba , tuni mutanen dake gurin suka fara yin tafi suna jinjina masa yadda yayi hakan , Huneed nadaga bayan bishiya jiyayi juwa na neman kamashi , wani abu yaji ya tokare masa a k'irjin sa tamkar numfashin sa zai tsaya haka yaji , Sanam jin yadda Asuk' ya rungume ta yasa ranta yayi mugun b'aci , k'arfin ta ta had'a guri guda ta hankad'ashi gefe , tana yin hakan tayi saurin komawa cikin gidan dan yagama b'ata mata rai over , Asuk' sosai yaji haushin abinda tayi masa dan har bige kansa yayi jikin motar , dan haka shima cikin gidan yabita.......

Huneed take ya yanke shawarar mutuk'ar Sanam tafito to sai ya d'auke ta , dan ya fuskan ci wannan guy d'in zai iya yimata komai yadda ya fusata , kuma shima bazai so ace ko d'an yatsan ta wani banza yasake rik'ewa ba , haka ya zauna zaman jiran fitowar ta , yana zaune motoci suka fara wucewa dan tafiya gurin Kamu , kwata kwata bai ga Sanam ta fito ba har ya tashi yafara nufar cikin gidan dan ganin me takeyi , lokacin kowa yatafi wajen party har Ammin su Rauda da k'awayen ta itama , ita kuwa Rauda dama tuni suna can ana shirya ta daga can za'a wuce sa ita , yana tsaye yana kai kawo a harabar cikin gidan sai ga Sanam da gudu ta fito tana kuka rigar ta duk ta yage ana ganin jikinta , bayan ta Asuk' ne daga shi sai gaje ran wando ya biyota da gudu shima , wajen Huneed ta nufo tana fad'in " dan Allah ka taimaka min wallahi d'an iska ne , wani mari Huneed ya tsinka mata sannan ya janyo hannun ta ya kawo ta wajen Asuk' dake tsaye yana kallon su yace " gatanan kayi mata duk abinda kakeso kayi , mamaki ne yaka ma Sanam tafara Nazarin a inah tasan wannan muryar ? Asuk' ya rik'e hannun ta tare da

cewa " Huneed thank u Yana k'ok'arin janta ya shigar da ita cikin gidan , kwata kwata Sanam bata ceton kanta take ba so take ta tuna muryar waye wannan dan tabbas tasan muryar kuma taji ta ba sau d'aya ba , juyawa Huneed yayi yana dafe kansa yayin da Asuk' yake jan hannun Sanam zai shiga da ita cikin gidan , ita kuma tana wai wayen Huneed tana son sanin waye shi ? gab da zasu shiga k'ofar falor Huneed yace " Stop dawata murya wacce tasa dukan su suka firgita , tuni Asuk' yasaki Hannun Sanam yana duban Huneed wanda ya nufo su gadan gadan tamkar zaki , yana zuwa yashiga duka Asuk' yana fad'in " rungumar da kayi mata baiyi ba sai ka ai ga keta mata haddi , mara tarbiya kawai wawa jaki , sai dukan sa yake tamkar zautacce haka yakoma , tuni ya sumar da Asuk' sannan ya waiwayo kan Sanam wacce tagama tsurewa jikin ta sai rawa yake , yana zuwa yajanyo hannun ta batare dayayi magana ba har suka fita daga gidan suka nufi titi , tunda ya rik'e mata hannu ta tuno da ko waye , Huneed bai saki hannun Sanam ba har sai da suka isa Hotel d'in dayake suka shiga har cikin d'akin daya kama ...........

*Comment plss*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪

https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 14.

Sunfi kusan minty goma a haka sannan aka d'auke ruwa , da sauri Sanam ta mik'e daga jikinsa tana sunkuyar da kanta k'asa dan kunya ce ta kama ta , Huneed shima mik'ewa yayi tsaye yana dube dube tamkar wanda yake neman wani , motocin da suka hango sun nufo k'ofar gidan su Rauda ya tabbatar musu da Andawo daga wajen party , Huneed ya juyo ya kalli Sanam yace " zan iya tafiya yanzu tunda naga sundawo , inaso ki kula da kanki sai wani lokacin , bai jira amsar ta ba ya wuce yabar wajen......

Da kallo Sanam tabi bayan Huneed tana jin kamar ta tashi ta rungumosa, cikin ranta taji kamar ta kirashi tace yadawo su dauwa ma a haka, tana kallon bayan sa har ya k'ulewa ganin ta amman ta kasa d'auke idon ta akansa , tayi nisa cikin tunanin taji andafa mata kafad'a , da sauri tayi firgigit tadawo daga tunanin data keyi tana duban wanda ya dafa ta , Rauda tagani tasaha kwalliya cikin shigar amare ba k'aramin kyau tayi ba , Rauda tace " ina kikaje Sanam kwata kwata banganki a wajen Kamu ba , gashi in ankira wayar ki bakya d'agawa ina fatan dai lafiya ? murmushi Sanam tayi sannan tace " bansan wajen ba, kuma na hau taxi muka gama yawo bangane ba har aka fara ruwa , Rauda tace " amman Janifa ta gayamin cewa taga kin shirya cikin shigar da sukayi , kuma lokacin ankawo motoci amman baki shiga kowacce ba , Sanam ta mik'e tace " kawai Allah baiyi zanzo ba amman gobe insha Allah bazanyi missing d'in Lunch ba , tare suka jera suka shiga cikin gidan suna hira abinsu , koda suka shigo harabar gidan Sanam tashiga dube dube kozata ga Asuk amman bata gansa ba , haka suka shige cikin gidan wanda yake acike da mutane 'yan biki........

Sanam kwata kwata takasa rintsawa saboda tunanin Huneed , babu abinda ke mata yawo a ido sai hoton kwanciyar datayi a jikin Huneed , lumshe idon ta tayi tana wani murmushi tana k'ara rungume filon dake hannun ta , a hankali ta furta " wannan Guy d'in na musamman ne yana burgeni , a haka barci yayi gaba da Sanam cike da tarin mafarkan Huneed.......

A b'angaren Huneed tunda yabar wajen Sanam ya taho sukayi waya da ogan su , nan aka sheda masa kiran gaggawar da ake musu akan rikicin da 'yan ta'adda suke a garin sakkoto , Kwata kwata Huneed kiran bai masa dad'i ba kawai dai dan ba yadda zaiyi ne , amman kafin yatafi ko sau d'ayane sai yakoma yaga Sanam dan yarinyar ta tsaya masa arai , kawai halayen tane basuyi ba kwata kwata amman da sannu zai gyara ta .......

Washe gari.....

Tunda Sanam ta tashi taji tana k'aunar ta sake ganin Huneed , bayan ta karya tayi wanka tashirya cikin wata doguwar riga me kyau daga cikin wad'an da ya siya mata , samun kanta tayi da saka d'aya daga cikin Hijab d'in mahadin rigunan , ba k'aramin kyau tayi ba ita kanta sai sai k'ara duba mirror take , tana fitowa su Rauda suna zaune suna shirya abubuwan da zasu yi

amfani dasu anjima , suna ganin ta suka tsaya suna kallon ta kowanne sai yaba kyan datayi suke , Rauda tace " Sanam kowanne kaya kikasa sai kinyi kyau inama ace nice haka , murmushi tayi sannan tace " kema haka ai kike My R kowanne dresing kikayi sai yayi miki kyau , Rauda tayi murmushi tace " ai nasan kinfini nesa ba kusa ba , wai ina ma zakije haka muna shirye shirye kina ficewa ke kuma ? Sanam tace " sorry my R yanzu zandawo ba dad'ewa zanyi ba , da sauri ta fice dan batason Ammi taji zata fita ta tsaida ta ma , tana fitowa harabar gidan suka kuma karo da Asuk , tana ganinsa ta had'e ranta tana yin gefe da fuskar ta , shima dayake yanajin haushin ta ko kallon ta bai kuma ba ya shige abinsa tamkar bai ganta ba .....

Taxi ta tsaida tagaya masa inda zai kaita , sai da ta shiga ta zauna sannan tafara zancen zuci " to yanzu innaje mezan ce masa nazo yi ? wata zuciyar tace " kawai kice kin yarda abinki ne shine kika dawo d'auka , tana wannan tunane tunanen nata har suka zo dai dai k'ofar Hotel d'in , fitowa tayi sannan tabiya me taxi kud'in sa yayi gaba , ta dad'e a k'ofar wajen tana kaiwa da komowa , da shawarar da zuciyar ta ta yanke nacewa wani abun ta yardar tashiga ciki......

Tunda gari ya waye Huneed ya had'a kayan sa cikin jakar sa , wajen goma na safe a can k'asar ya fita yashiga gari zaiyiwa Hajiyar sa siyayya , daga can ya biya airpot yagama komai jirgin su zai tashi k'arfe uku na rana , yana gama komai ya nufi gidan su Rauda ya tsaya daga wajen daya saba tsayawa yana lek'en harabar gidan ko Allah zai sa Sanam ta fito , yafi minty 30 amman baiga kowa ba sai yara suna ta wasan su abinsu , ganin yana k'ara b'ata lokaci yasa ya juya zai tafi , wata zuciyar tace " to inta fito mai zai ce mata ? kawai ya juya ya hau taxi yakoma Hotel d'in , a lokacin Sanam na zaune a reception dan sun sheda mata me number da ta tambaya ya fita , tana xaune ta had'a kai da gwiwa taji wani k'amshi ya doki hancin ta , tana d'agowa taga wucewar Huneed batare da ya kula da ita ba , sai da tabari ya jima da wucewa sanna ta nufi d'akin nasa......

Tana zuwa ta k'wank'wasa k'ofa daga ciki yace " yes coming , tura k'ofar tayi tashiga cikin d'akin lokacin dagashi sai tawul zai shiga wanka , tana ganin da haka ta juya da baya zata koma waje , da sauri yace " karki fita bati nashiga toilet wanka zanyi , da sauri ya fad'a cikin toilet d'in yanajin wani farin ciki da ganinta dayayi , Sanam kuwa yadda tagansa ba k'aramin tsoro taji ba , tunda take bata tab'a ganin jikin namiji haka ba sai yau , samun waje tayi ta zauna tana tunanin meyake shirin faruwa da itane.......

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/27, 09:45] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 14.

Sunfi kusan minty goma a haka sannan aka d'auke ruwa , da sauri Sanam ta mik'e daga jikinsa tana sunkuyar da kanta k'asa dan kunya ce ta kama ta , Huneed shima mik'ewa yayi tsaye yana dube dube tamkar wanda yake neman wani , motocin da suka hango sun nufo k'ofar gidan su Rauda ya tabbatar musu da Andawo daga wajen party , Huneed ya juyo ya kalli Sanam yace " zan iya tafiya yanzu tunda naga sundawo , inaso ki kula da kanki sai wani lokacin , bai jira amsar ta ba ya wuce yabar wajen......

Da kallo Sanam tabi bayan Huneed tana jin kamar ta tashi ta rungumosa, cikin ranta taji kamar ta kirashi tace yadawo su dauwa ma a haka, tana kallon bayan sa har ya k'ulewa ganin ta amman ta kasa d'auke idon ta akansa , tayi nisa cikin tunanin taji andafa mata kafad'a , da sauri tayi firgigit tadawo daga tunanin data keyi tana duban wanda ya dafa ta , Rauda tagani tasaha kwalliya cikin shigar amare ba k'aramin kyau tayi ba , Rauda tace " ina kikaje Sanam kwata kwata banganki a wajen Kamu ba , gashi in ankira wayar ki bakya d'agawa ina fatan dai lafiya ? murmushi Sanam tayi sannan tace " bansan wajen ba, kuma na hau taxi muka gama yawo bangane ba har aka fara ruwa , Rauda tace " amman Janifa ta gayamin cewa taga kin shirya cikin shigar da sukayi , kuma lokacin ankawo motoci amman baki shiga kowacce ba , Sanam ta mik'e tace " kawai Allah baiyi zanzo ba amman gobe insha Allah bazanyi missing d'in Lunch ba , tare suka jera suka shiga cikin gidan suna hira abinsu , koda suka shigo harabar gidan Sanam tashiga dube dube kozata ga Asuk amman bata gansa ba , haka suka shige cikin gidan wanda yake acike da mutane 'yan biki........

Sanam kwata kwata takasa rintsawa saboda tunanin Huneed , babu abinda ke mata yawo a ido sai hoton kwanciyar datayi a jikin Huneed , lumshe idon ta tayi tana wani murmushi tana k'ara rungume filon dake hannun ta , a hankali ta furta " wannan Guy d'in na musamman ne yana burgeni , a haka barci yayi gaba da Sanam cike da tarin mafarkan Huneed.......

A b'angaren Huneed tunda yabar wajen Sanam ya taho sukayi waya da ogan su , nan aka sheda masa kiran gaggawar da ake musu akan rikicin da 'yan ta'adda suke a garin sakkoto , Kwata kwata Huneed kiran bai masa dad'i ba kawai dai dan ba yadda zaiyi ne , amman kafin yatafi ko sau d'ayane sai yakoma yaga Sanam dan yarinyar ta tsaya masa arai , kawai halayen tane basuyi ba kwata kwata amman da sannu zai gyara ta .......

Washe gari.....

Tunda Sanam ta tashi taji tana k'aunar ta sake ganin Huneed , bayan ta karya tayi wanka tashirya cikin wata doguwar riga me kyau daga cikin wad'an da ya siya mata , samun kanta tayi da saka d'aya daga cikin Hijab d'in mahadin rigunan , ba k'aramin kyau tayi ba ita kanta sai sai k'ara duba mirror take , tana fitowa su Rauda suna zaune suna shirya abubuwan da zasu yi amfani dasu anjima , suna ganin ta suka tsaya suna kallon ta kowanne sai yaba kyan datayi suke , Rauda tace " Sanam kowanne kaya kikasa sai kinyi kyau inama ace nice haka , murmushi tayi sannan tace " kema haka ai kike My R kowanne dresing kikayi sai yayi miki kyau , Rauda tayi murmushi tace " ai nasan kinfini nesa ba kusa ba , wai ina ma zakije haka muna shirye shirye kina ficewa ke kuma ? Sanam tace " sorry my R yanzu zandawo ba dad'ewa zanyi ba , da sauri ta fice dan batason Ammi taji zata fita ta tsaida ta ma , tana fitowa harabar gidan suka kuma karo da Asuk , tana ganinsa ta had'e ranta tana yin gefe da fuskar ta , shima dayake yanajin haushin ta ko kallon ta bai kuma ba ya shige abinsa tamkar bai ganta ba .....

Taxi ta tsaida tagaya masa inda zai kaita , sai da ta shiga ta zauna sannan tafara zancen zuci " to yanzu innaje mezan ce masa nazo yi ? wata zuciyar tace " kawai kice kin yarda abinki ne shine kika dawo d'auka , tana wannan tunane tunanen nata har suka zo dai dai k'ofar Hotel d'in , fitowa tayi sannan tabiya me taxi kud'in sa yayi gaba , ta dad'e a k'ofar wajen tana kaiwa da komowa , da shawarar da zuciyar ta ta yanke nacewa wani abun ta yardar tashiga ciki......

Tunda gari ya waye Huneed ya had'a kayan sa cikin jakar sa , wajen goma na safe a can k'asar ya fita yashiga gari zaiyiwa Hajiyar sa siyayya , daga can ya biya airpot yagama komai jirgin su zai tashi k'arfe uku na rana , yana gama komai ya nufi gidan su Rauda ya tsaya daga wajen daya saba tsayawa yana lek'en harabar gidan ko Allah zai sa Sanam ta fito , yafi minty 30 amman baiga kowa ba sai yara suna ta wasan su abinsu , ganin yana k'ara b'ata lokaci yasa ya juya zai tafi , wata zuciyar tace " to inta fito mai zai ce mata ? kawai ya juya ya hau taxi yakoma Hotel d'in , a lokacin Sanam na zaune a reception dan sun sheda mata me number da

ta tambaya ya fita ,  tana xaune ta had'a kai da gwiwa taji wani k'amshi ya doki hancin ta ,  tana d'agowa taga wucewar Huneed batare da ya kula da ita ba ,  sai da tabari ya jima da wucewa sanna ta nufi d'akin nasa......

Tana zuwa ta k'wank'wasa k'ofa  daga ciki yace " yes coming , tura k'ofar tayi tashiga cikin d'akin lokacin dagashi sai tawul zai shiga wanka ,  tana ganin da haka ta juya da baya zata koma waje , da sauri yace " karki fita bati nashiga toilet wanka zanyi , da sauri ya fad'a cikin toilet d'in yanajin wani farin ciki da ganinta dayayi , Sanam kuwa yadda tagansa ba k'aramin tsoro taji  ba , tunda take bata tab'a ganin jikin namiji haka ba sai yau , samun waje tayi ta zauna tana tunanin meyake shirin faruwa da itane.......

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_ 😍🌹
[9/27, 09:46] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir Rahim*

Chapter     15.

Bayan minty 7. saiga Huneed ya fito sanye da kayansa , har lokacin Sanam tana

duniyar tunani batasan ma ya fito ba sai da yayi mata gyaran murya , da sauri ta dawo daga tunanin tana d'ago kai a hankali tana dubn sa , wani kyau yayi mata cikin k'anan nun kaya , Huneed yana da k'ira me kyau dayake jan hankalin 'Yan mata da ita , kana kallon da kaga cikakken namiji jarumi wanda baya shayin komai , yana kama da wannan sabon jarumin na indi'a Allu Arjun , sosai Sanam ta shagala a kallon sa tamkar wacce ta warke daga makanta , ganin ta kafeshi da idanu yasa yace mata " Hy 'yan mata wannan kallo haka kuma ? wata kunya ce ta rufe Sanam tayi saurin yin k'asa da kanta , a hankali ya furta " ya kike ya gajiyar ki ta dukan ruwa , ina fatan bakiyi zazzab'i ba dai ? Sanam tace " lafiya lau babu abinda nayi , kaima dafatan kadawo lafiya ? Huneed yace " yes nrml nake dan yanzu haka ma shirye shiryen barin k'asar nake , wani abu Sanam taji ya tsaya mata a k'irji wanda ta shiga tambayar ko meye oho , cikin zuciyar ta dai taji rashin dad'in maganar tasa dayayi , tambaya ta shiga yiwa kanta meyasa dayace zai tafi taji rashin dad'i haka ? maganar sa ce ta katse ta da yace mata " ko akwai wani abun da kike buk'ata ne ? da sauri Sanam ta girgiza kai alamar babu abinda takeso , Huneed ya tab'e baki irin ko ajikinsa ya juya gaban mirror yana gyara kansa , ganin shuru Sanam tak'i yin magana yasa ya juyo yace " Babbar direba ko dai akwai abinda kika manta ne shine kika zo d'auka ? Sanam tace " Ae daman ina tunanin ko nabar d'an kunne na anan ne , Huneed yayi murmushi sannan yace " baki bar d'an kunne ba sai agogo nagani gashican , nuna mata inda A gogon ta yake na gold. Sosai Sanam ta shiga mamakin halin Huneed , kwata kwata ma ita ta manta da Agogon ta d'an kunnen ma ta fad'esa ne kawai , dan tasan bata bar d'an kunne ba ashe tabar a gogo , Agogon ta yana da mutuk'ar tsada dan Daddyn tane ya siyo mata shi a America , ba yadda Mumy Nafeesa batayi ba akan ya siyo mata irin sa amman yak'i , akan hakan har matsala suka samu da Daddyn lokacin , d'auko Agogon tayi ta saka a hannun ta tana cewa " nagode sosai bari nazo natafi Allah ya sauke ka lafiya , Huneed yace " Ameen nagode da addu'a , amman ke sai yaushe zaki koma gida ne ? Sanam tana saka takalmi tana fad'in " bazan dad'e ba nima zantaho , da kallo Huneed yabi yatsun k'afar ta ta wanda yayi bala'in had'uwa cikin takalmin filet , a hankali ya furta " komai naki yayu yadda akeso , halinki ne kawai mara kyau duk da naga kin fara rage wani Abun........

Har Sanam ta bud'e k'ofa zata fita Huneed yace " inaso ki kula da kanki har kidawo gida , sannan karki k'ara yin direbin a cikin wannan k'asar saboda nan ba Nageria bace , Banda saka k'ananun kaya plss ki kula sosai kinji k'anwata , Sanam wani dad'i takeji mutuk'ar Huneed nayin magana , musamman maganar sa ta k'arshe da yakira ta da sunan k'anwar sa , a hankali tace " zan kiyaye insha Allah , amman inason card d'inka saboda wani lokacin , murmushi Huneed yayi sannan yace " ni da ba ma'aikaci ba me yahad'ani da card , kawo phone d'inki insa miki number ta sai mudunga gaisawa tunda yanzu munzama abokai mundaina fad'a ko ? murmushi Sanam tayi tana d'aga kai alamar Ae , mik'a masa wayar tayi yasa mata number sa ta Nageria sannan ya bata wayar ta ta , tana ansa ta dube sa tace " Allah ya sauke ka lafiya ta juya ta fita bata jira cewar saba , har ta fice daga d'akin kwata kwata ya kasa motsi , wata k'aunar ta ce ta shige sa lokaci d'aya , sai sannan ya kuma jin dadin yadda ta fara canza halayen ta , wani dad'i yaji ya kamashi ganin yadda tasa doguwar rigar daya ce ta dunga sawa , haka ya gama shiri cikin farin ciki tare da kewar Sanam d'in , sosai yakejin k'aunar ta na ratsa cikin duk wasu k'ofofi na jikin sa .........

Sanam na fitowa ta sauko k'asa tasamu waje guda ta zauna , kuka ta shiga yi  tana share hawayen da ke zubo wa akan kuncin ta ,  cikin zuciyar ta take fad'in " meyasa nakejin wani iri a game da kai ?  tabbas najin tamkar inbishi mutafi iya jiya kawai nakejin wani abu game dashi , wata zuciyar ta ta kuma tace " Son shi kike Sanam wannan shine So  , da sauri tace " a'a ba soyayya bace kawai kulawar da yayi danine lokacin da Asuk yaso ketamin haddi ,  ta dad'e tana sak'e sak'e akan Huneed sannan ta mik'e tafita daga cikin Hotel d'in .......

Huneed tuni ya janyo trolly d'insa yafito daga Hotel d'in , yana tafe yana murmushi shi kad'ai wanda yakejin wani shauk'i ,  Sanam har lokacin ta kasa barin k'ofar Hotel d'in saboda son tasake ganin Huneed ,  tana hangoshi tayi saurin lab'ewa bayan wata bishiya tana lek'oshi , wani kyau taga ya kuma yi mata ga glass daya sa tamkar ba indiye , Taxi ya tsaida ya hau suka tafi sannan Sanam ta fito daga wajen data b'uya , da kallo tabi bayan motar har ta k'ulewa ganin ta sannan itama ta tsaida Taxi tayi gidan su Rauda........

*Hmm wallahi nagaji da rashin Comment dinku*
[9/27, 09:47] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 16.

Har aka gama shagalin bikin Rauda Sanam bata cikin sukuni , tunda Huneed yatafi tamkar yatafi da duk kan wani sukuni nata ,  gashi shuru  sai jiran kiran wayar sa take amman

bai kira taba ,  haka suka kai Rauda gidan ta sosai anyi shagali tamkar baza adaina ba ,  haka aka mik'a Amarya gidan ta kowa ya kama gabansa...

Sanam tuni tunanin Huneed yafara damunta , tuni tabi shafin sa na Face book tana neman number sa , akuwa tayi sa'a tasamu ranar murna sosai tamkar tayi tsalle , kiran wayar tasa tashiga yi har ta katse bai d'aga ba ,  haka ta kuma bin number tasake kira amman yanzu ma baid'aga ba ,  sai da tayi kira biyar ba a d'agawa har tagaji ta ajiye wayar tana jin babu dad'i , ring din wayar ne yasa da sauri ta d'auki wayar tana tunani ko shine ya biyo ta , number Hajiya Nafeesa tagani wanda tasa Mummyna , d'an guntun tsaki taja sannan ta d'aga wayar tana fad'in " Mummyna barka da wannan lokaci , Hajiya Nafeesa cike da kissa irin ta ta ta manyan mata tace " Barka kadai My Luv yakike ya Turkey ? Sanam tace " lafiya lau Mummy ya gida ya kowa da kowa ? lafiya lau Luv kunsha biki nasan kin gaji sosai amman yaushe zaki dawo?  Sanam tace " ban fara shirin taho ba amman inaso intaho gida dan ina da abubuwan da zanyi , Hajiya Nafeesa cikin ranta tace " nima nafiso kiyi kidawo dan insamu infara gabatar da aikina ,  a fili kuma tace " yaka mata kidawo dan ina missing d'inki sosai , gashi Fahad ma kullum cikin zance ki yake wai gidan babu dad'i tunda bakyanan ,  Sanam ta tab'e baki tamkar tana ganin Fahad d'in tace " ina nan tafe Mummyna kice ina gaida Uncle d'in , daga nan tace " Byee Mum zan fita yanzu sai nadawo mayi waya , kafin Hajiya Nafeesa tace wani abu tuni Sanam ta kashe wayar .....

Tunda Huneed yadawo Nageria aiki yasa shi gaba , dan yana dawowa aka turasu Zamfara dan maganin ' Yan ta'addar dasuka dami garin , tunda yatafi baya samun wani lokaci gashi wajen babu network bare yayi waya , kullum zuciyar sa tana tunanin Sanam dan yasan dole zatai ta zaman jiran kiran sa , wata zuciyar tace masa " wannan mara kirkin ai farin ciki zatayi da baro k'asar dakayi ,  wata zuciyar tace " aikuma alamun ta kamar tadaina komai datakeyi , haka yashiga tunani akan Sanam yana lissafo kyan dirinta da kuma uwa uba kyan fuskar ta baki d'aya .....

Ranar da suka dawo gida da nasarar da suka samu a zamfara , ranar Sanam tayi masa wanna kiran ya shigo sai dai yana kallo yak'i d'agawa , dan basosai yake d'aga kiran number da baisani ba , duk da yaga number ba ta k'asar bace amman kwata kwata bai kawo Sanam ce ke kiran saba ,

Acan b'angaren Sanam kuwa  tunda ta fice yawo bata dawo ba sai dare , koda ta dawo wanka tayi tasa kayan bacci ta kwanta abinta , dan kwata kwata Sanam bata damu da ibada ba , karatun addinin ma ba damunta yayi ba bare , dan haka tana kwanta tawa ta d'auko wayar ta tafara chat da k'awayen ta , sai ta duba number Huneed taga yana kan online , da sauri tafara murna tana shirin yi masa magana , wata zuciyar tace mata " kina mace me Daraja da Aji amman kiyi masa magana , inajin ma yana ganin kiranki d'azu amman yak'i d'agawa , sannan ai tunda yana da number ki yakamata ace ko sau d'ayane ya kiraki kun gaisa , haka Sanam tabi shawarar zuciyar ta ta fasa yiwa Huneed magana ,  hirar su suka ci gaba dayi ita da Diyana

tana ta basu labari akan k'awayen su na Nageria , sai wajen k'arfe d'aya sannan Sanam ta sauka daga online  tayi kwanciyar ta , sai dai me ? tana kwanciya hoton Huneed yafara yi mata yawo a idanun ta ,  musamman lokacin data gansa d'aure da Tawul da kuma lokacin data fad'a jikin sa a k'ofar gidan su Rauda ,  haka tai ta juyi ta kasa bacci tamkar mara lafiya , tashi tayi ta kuma d'aukar wayar ta tashiga Face book shafin sa , aikuwa tana shiga taga bai dad'e dayin posting ba da shigar sa ta cikakken Army , zoom d'in pic d'in tayi tana k'are masa kallo , murmushi tayi tana shafa fuskar sa tana fad'in " tabbas ka cika cikakken namiji wanda yaka mata a jinjinawa ,  babu Namijin da Sanam ta tab'a so a duniya sai kai , har wani lumshe ido take tana shafa masa fuska tare da tuno yadda yake komai nasa irin na isassun maza , tuni ta danna kiran number sa dan tana buk'atar jin wanna  daddad'ar muryar tasa , addu'a tashiga yi aka Allah yasa ya d'aga mata kira wanna  karan , ring take har ta yanke ba'a d'aga ba , sake kira tayi karo na biyu sai da takusa yankewa sannan ya d'aga yana fad'in " Assalamu Alaikum , cike da tsoro Da rawar Murya Sanam tace " wa'alaikas salam  barka da dare ,  da sauri Huneed ya watstsake daga baccin da yasoma kamashi , cikin ransa yafara fad'in " tabbas wannan muryar ta Sanam ce , duba number yayi yaga number ta k'asar waje ce , da sauri yace " wanakeji kamar K'awata Sanam ? Murmushi Sanam tayi har sautin na fito tace " nice nakira dafatan ban shiga hak'k'in ka ba kana bacci ? Murmushi Huneed yayi yace " kin shiga hak'k'ina kuwa dan ina tare da mata ta kika kirani , yanzu haka gashican ta turoni waje ta kulle d'akin ta , Sanam jitayi wani abu ya tokare k'irjin ta wata zufa ta karyo mata , cikin ranta tace " dama mutum nan yana da mata bata sani ba ? kamar yasan abinda take tunani kenan yace " kinsan mantawa nayi kwata kwata ban sheda miki ina da mata ba har da yara guda biyu , yanzu gashi kinjawomin kwanan k'ofar waje ,  cikin murya me sanyi Sanam tace " kayi hak'uri wallahi bansan kana da mata ba da bazan kira ka a wannan daren ba , kabata hak'uri kaji sai da safe , kafin ta kashe wayar yayi sauri yace " lah babu komai muci gaba da magana kinji , yakike yana baroku dafatn komai nrml ? Sanam da kishi yake taso mata kawai tace masa " lafiya nake komai yana nan yadda kabarshi amman kayi hak'uri sai da safe , bata jira cewar saba ta kashe wayar dukan ta tana jifa da ita , kafin kuka ya biyo baya tare da jin haushin kanta na kiran datayi masa , tabbas da tasan yana da aure da baza ta saka shi a cikin ranta har haka ba , yanzu yazatayi da Soyayyar sa wacce tashiga zuciyar ta lokaci d'aya ? kuka take sosai tana jin babu dadi , gashi ita tun tasowar ta batason kishiya koda ta sittira ne bare ya kai ga had'a miji ,  kuka takeyi tare da addu'ar cire son Huneed daya kamata batare da ta gama shirya hakan ba.......

Huneed tunda ya fahimci Sanam kishi ne yasa takashe waya , dariya yashiga yi sosai yana murna yadda ta fad'a son sa , dan tabbas wanna kad'ai zai tabbar masa da ta fad'a soyayyar sa ,  kwanciya yayi yana tuno yadda komai nata yake , murmushi yake in ya tuna yadda take gudu sosai a titi ranar da yaje k'asar Turkey , a hankali ya furta " Iluv u my Baby Sanam   I really luv u more , wani lumshe ido yayi lokacin daya tuna yadda ta fad'o jikin sa da ana ruwan saman nan , tunda ga ranar ya tabbatar wa da kansa yana son Sanam d'in ,  dan haka dole da safe ya rarrashi Abarsa dan kar yaje wani yayi masa bugun baya  abarshi da hamma , duk da yaga tarkon sa yakama kurciya bazai yi wasa da wannan damar tasa ba , amman dole sai ya jajurce akan tarbiyar Sanam , dan kwata kwata bata da tarbiya me kyau gashi uwa uba yadda ya fahimce ta bata da ilimin addini ,  a shirye yake ya tsaya tsayin daka ya gyara ta dan yasamu

nagartattun 'Yaya............

*Tofa su Huneed har anfara tunanin Yara tun ba ashawo kan Sarauniyar Rigima ba*😹😹

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce😍🌹
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala Writer's Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

_Ina yiwa d'aukacin Masoyana barka da sallah , dafatan kowa yayi sallah lafiya Allah ya karb'i ibadun mu , 🙏🏻🙏🏻Allah ya mai mai ta mana Ameen_

*Mundawo hutu zamu d'ora Allah yabamu ikon rubuta dai dai 👏🏻👏🏻 wanda za'a amfana

dashi*

Chapter 17.

Sanam kuka take sosai tamkar wacce akace Mahaifanta sun mutu , a haka bacci yayi gaba da ita mai cike da mafarki iri iri akan Huneed........

Hajiya Nafeesa ce rik'e da waya a hannu ta na neman number wata k'awar ta Hajiya Harira , bugu d'aya Hajiya Harira ta d'aga wayar tana fad'in " Manya manya maganin k'anana k'anana , murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " kune manya ai Hajiya Harira , kwata kwata ba'ajin ki agari tamkar laya kin b'ace , Hajiya Harira tace " Abubuwa sunyi yawa wlh shiyasa kikajini shuru , Hajiya Nafeesa tace " inason ganinki dan akwai wani aiki dana keso kimin , murmushi Hajiya Harira tayi sannan tace " shu'uma kice neman da kikemin badan Allah bane kenan ? dariya Hajiya Nafeesa tasa sannan tace " sai kinzo zamuyi magana kawai , nan sukayi sallama da juna kowacce ta katse wayar ta .......

Washe gari..
Sanam jitayi tanason tahowa gida , kwata kwata bata da sukuni saboda tunanin Huneed , babu kalmar dake mata yawo sai kalmar *Ina da Mata har da yara biyu,* wato mata garesa harda yara biyu ita kuma fa ? hawayen da ya cika idanunta tasa hannu ta goge , tabbas so baisan waje ba taya zai kaita inda bata da mahalli , dan ko zata mutu babu aure bazata auri namijin dake da mata ba , tayi nisa cikin tunani taji andafa kafad'ar ta , firgigit tayi takai duban ta ga gefen ta Mumyn su Rauda ce tsaye tana k'are mata kallo , wani murmushi Sanam ta k'ak'alo tana duban Mumyn , cikin harshen turanci Mumy ta tambayi Sanam meke damun ta haka take tunani , nan Sanam ta karkace tace babu abinda ke damunta kawai tana son tafiya gida ne , Mumyn Rauda ta zauna gefen Sanam tace mata " ko akwai abinda akayi mata takeson tafiya ? Sanam ta gyad'a kai alamun a'a , kawai tanason ta tafi ne saboda Babu Rauda zaman babu dad'i , Mumy Rauda tashiga lallab'ata akan tabari ta huta sosai sai ta koma k'asar Nageria d'in , badan Sanam ta so ba ta hak'ura akan zata k'ara sati sannan ta tafi.......

Huneed tuni yafara bincike akan gidan su Sanam , dan yanason sanin waye Mahaifinta da kuma asalin ta , cikin kwana biyu Huneed yasamu cikakken bayani akan wacece Sanam da kuma Mahaifinta har ma da sanin ai nahin wacce ta haifeta.....

Sosai Huneed yaji K'aunar Mahaifiyar Sanam na yadda ta sadaukar da 'Yar ta ga kishiyar ta , gashi yadda yasamu labari babu wanda ya b'ata Sanam face Daddyn ta da kuma kishiyar

Mumynta , nan ya k'udirta aransa sai ya gyara ta tamkar yadda Mumyn ta take .....

Kwanci tashi ba wuya a gurin Allah ,

Sanam tuni an hallara a airpot d'in k'asar Turkey za'a taho gida , Mumyn Rauda da Rauda da mijinta sune sukayi mata rakiya zuwa Airpot , suna rungume da juna ita da Rauda sai hawaye suke har aka fara kiran sunayen fasinja , haka suka rabu suna kewar juna tare da d'agawa juna hannu har Sanam tashige cikin jirgi.......

*Gida Nageria*

jirgin su Sanam ya sauka a garin Abuja , tuni Fahad yaje d'auko a airpot , tana saukowa daga jirgi a hankali tamkar wacce batason saukowa , wani matashin saurayi shine ya matso daf da ita suka jero tamkar tare daman suke tafiyar......
[9/27, 09:49] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 18.

Dai dai da zasu sakko daga step din k'arshe na jirgin , Sanam ta zame tayi baya zata fad'i , da sauri wannan guy d'in ya rik'ota ta fad'a jikin sa tamkar a shirin film , duk wanda ya dubesu a lokacin sai yayi tunanin mata da miji ne suke tare , da sauri Sanam ta turesa tana

janye jikin ta kafin tayi saurin saukowa daga jirgin , mutanen data gani ne yasa ta jin kunya tare da saurin nufar wajen ake parking din motoci.....

Tana k'ara sowa Fahad ya fito daga motar yana murmushi tare da nufota tamkar zai rungume yana fad'in " oyoyo My Angel , ganin yana neman rungume ta yasa tayi saurin dakatar dashi tana fad'in " thanks tayi saurin yi gefe tana bud'e bayan motar ta shige abin ta .....

Fahad sosai yaji babu dad'i akan abinda Sanam d'in tayi masa , murmushi yayi na mugunta a zuciyar sa yace " zakizo hannu zaki gane baki da wayo sai na cire miki wannan jin kan naki , nufar motar yayi zai shige a lokacin shikuma wannan saurayin ya k'araso , sallama yayiwa Fahad yabashi hannu sukayi musabiha , bayan sun gaisa saurayin nan ya dubi Fahad yace " dan Allah Yayan mu in babu damuwa zanyi magana da Babyn dake bayan motar , Fahad ya k'are masa kallo yayi d'an mutmushi yace " bisimillah ka yi mata magana , nan yayi masa godiya ya k'arasa jikin murfin motar inda Sanam din take , Fahad dariyar mugunta ya shiga yi masa dan yasan halin Sanam bata son jira mutukar tadawo daga tafiya , koda ya k'arasa jikin motar bubbuga glass yayi, Sanam tanajin sa kuma tana ganin sa amman ko motsi batayi ba bare ta bud'e , wayar ta tashiga dubawa tana jin wani haushi na tsayawar da Fahad d'in yayi bai shigo sun tafi ba , tsaki kawai tashiga yi dan batason b'ata lokaci ko kad'an , ganin Fahad bashi da niyyar tahowa su tafi kuma shima mutumin nan bashida niyar tafiya yasa ta sauke glass d'in motar , murmushi yayi yana duban ta kafin yace " kin kai kuma kin isa kiyi komai , kallo d'aya nayi miki nasan kin cika cikakkiyar mace wacce ta isa , ina neman Alfarma guda biyu zuwa uku a wajen ki dafatan zan samu ? Sanam tunda yafara magana tanajin sa amman ko kallon da batayi ba , cikin ranta tace " kaima ka isa a soka amman ko k'afar Huneed baka kama ba , nan take taji tanason ganin Huneed da kuma son jin muryar sa , cikin ranta take fad'in " nadamu da kai amman kwata kwata naga ko sau d'aya baka damu dani ba , Maganar saurayin dayake tsaye a kanta itace tadawo da ita daga duniyar tunanin Huneed datakeyi , murmushi tasamu kanta dayi sannan ta dubesa tace " bawan Allah kayi hak'uri sauri nake kazo kasameni a gida muyi magana , Murmushin jin dad'i yayi sanna ya dubeta yace " nagode sosai kuma zaki ganni in sha Allah , sunana Jaydeen A Ambasodor nasan kinsan Mahaifina a cikin garin nan na Abuja ? sarai Sanam tasan waye Jaydeen kuma tasan waye mahaifinsa da irin kud'in da yake dashi , amman sai cewa tayi " nifah bansan wani me irin wanna sunan ba ma , sosai Jaydeen yaji rashin dad'in maganar da Sanam tayi , amman saboda yarinyar lokaci d'aya ta tafi dashi , dan duk yawan duniyar da yayi bai tab'a karo da mace me k'irar Sanam ba , ga kyau ga diri tamakar itace ta shirya kanta , maganar tace ta katseshi tace " dan Allah yiwa direban can magana yazo mutafi , mamaki ne ya kama Jaydeen ganin yadda Fahad ya had'u amman take ce masa direba , shi duk a tunanin sa ma Yayan tane , zuge glass tayi batare da tak'ara magana ba , shima shigewa yayi yasanar da Fahad tare da tambayar sa inane gidan su , nan Fahad yabashi address sukayi sallama kowa yashige ya tafi.......

Hajiya Nafeesa tuni sunje wajen wani boka ita da k'awar ta Hajiya Harira , duk ta sanar dashi yadda takeso araba tsakanin Sanam da Abban ta , nan yabata magun guna kala kala wanda zatayi amfani dashi ......

Tana dawowa tashiga kitchen da kanta tayi girki kala kala , tana murna yau Sanam zata dawo taci wannan maganin shikenan Daddyn ta ya tsaneta , dan duk duniya bata da wacce ta tsana a yanzu tamkar Sanam ......
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR* *KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 19.

Tunda ga farko gate masu gadin gidan Alhaji Abba suka san 'yar lele tadawo , dan yanayin yadda akeyin hon. Kad'ai zai tabbatar maka da isowar Sanam gida ......

Tunda tafito daga motar suke zubewa suna mata sannu da zuwa amman ba wanda ta amsawa , hanyar k'ofar falon su tabi tana danna wayar ta , Tura k'ofar tayi wani k'amshi ya daki hancin ta , lumshe ido tayi dan tana mutuk'ar k'aunar k'amshin turaren wutar , cikin ranta take fad'in " Mumy akwai san k'amshi da tsafta shiyasa ko da yaushe intayi tafiya take missing d'in komai na Mumyn nata , bata gama zancen zucin ta ba taji muryar Mumyn tana fad'in " oyoyo My luvly dauther your welcome , da sauri Sanam ta fad'a jikin Hajiya Nafeesa tana fad'in " Miss u my mumyna , ina dawowa naji k'amshin turarenki me dad'i , murmushi Hajiya Nafeesa tayi tana wani rausayar da kai tace " wannan k'amshin ai na musamman ne , dan ke nasa *Zee MD* ta had'amin turaren ta me k'amshi da kama gida da jiki da kuma kaya , nasan kina son had'in turaren ta shiyasa na shirya takanas naje gidan ta harda na wanka da Humra na anso miki , murmushi Sanam tayi sannan tace " nagode Mumyna bari nashiga ciki nayi wanka sai na fito , da sauri ta nufi sama inda d'akin ta yake ......

Hancin motar Huneed ce ta shigo gate d'in gida su , saukar sa kenan daga taraba sunje wani aiki , yana fitowa daga motar sukayi karo da Hisham yana k'ok'arin fita , yana ganin d'an uwan nasa yafara fara'a yana fad'in " Soja mazan fama saukar yaushe ? Huneed yayi murmushi yace " saukar yanzu dan ko cikin barrack bashiga ba nataho gida , Hisham yace " sannu da zuwa ya anshi jakar hannun nasa ya juya suka shiga cikin gidan tare.......

Fahad yanemi parking space ya ajiye motar sannan ya shigo cikin gidan , karo sukayi da Hajiya Nafeesa lokacin Sanam ta hau sama sai ita kad'ai a zaune , Kusa da ita Fahad ya zauna yana fad'in " ina 'yar mulkin take ? Hajiya Nafeesa tayi masa nuni da baki alamar tana sama , tab'e baki yayi sannan yace " wallahi wannan yarinyar bata da mutunci ko kad'an , wai ni zata kallah ta kirani da direban ta , Hajiya Nafeesa ta dube sa tace " Sanam d'in ce tace maka direba ? Fahad cike dajin haushi yashiga bawa Hajiya Nafeesa labarin duk yadda sukayi a airpot , sannan yace " wanda yaje gun nata da zumar yana sonta shi ta turo wai ya kira mata direban ta , murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " k'yale ta kawai iya yaune duk rashin mutuncin nata , dan mahaifin ta tana juya mata baya zata dawo k'ark'ashin ikon mu , a lokacin zaka shigar da manufarka nasan auren ta kaga babu ta yadda za'ayi tak'i ka saboda bata da majin gina , dama kuma kaga bata damu da wannan saunar uwar tata ba , hasalima sai da nasan yadda nayi ta tsani mahaifiyar tata , kaga bata da inda zata nufa dole sai wajen mu dai , wani dad'i sosai Fahad yaji har da murmusawa tare da jinjinawa yayar tasa , dan yana mugun jin sha'awar Sanam , tunda yake mu'amala da mata bai tab'a cin karo da mace me k'irar jikin Sanam ba , komai na jikin ta ya had'u sosai , hatta da faratan hannun ta da k'afa abin kallah ne , nan yafara hango shi yana jikinta yana sarrafa ta yadda yakeso......

Sanam na shiga d'akin ta taci karo da wani k'amshin na musamman , lumshe ido tayi tana bud'e hanci tana shak'ar k'amshin , toilet ta fad'a danyin wanka , nan ma karo tayi da turaren wanka me k'amshi ta tsiyaya a cikin abin wankan ta , cikin ranta ta furta " gaskiya matar nan ta iya turaruka masu k'amshi , ga k'amshin me sanyi da kuma dad'i da sanyaya zuciyar me shak'a , tana shiga cikin ruwan wankan tafara lumshe ido tana wani sirtaccen murmushi.......

Koda Sanam tagama wanka tafito , shieyawa tayi cikin wasu riga da wando masu kyan gaske , gasu da rashin nauyi sosai sunyi kyau , wayar ta ta d'auka ta fito daga cikin d'akin ta sauko k'asa abinta.......

Tana sakkowa idon Fahad k'ur akanta yana kallonta , wani yawu yake had'iya jikake k'utt.
duk kallon dayake mata kwata kwata bata kula dashi ba , dan ta tattara hankalinta akan wayar ta tana nemo lambar Daddyn ta , tana k'arasowa taja kujera ta zauna tafara magana " Mumy me kika dafa min dan nayi missing din girkin ki , Murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan cikin kissa tace " abincin da kika fiso my Shalele , dan nasan dama dole zakiyi missing din girkin nawa , Sanam zatayi magana kenan sai Alhaji Abba ya d'aga wayar yana fad'in " welcome my queen dafatan kindawo lafiya ? Sanam tace " lafiya lau my Daddy , nayi Missing d'inka inason

inganka ,  nan tashiga zabga masa shagwab'a tamkar wata yar k'aramar yarinya ,  da k'yar ya lallab'ata sannan ya sheda mata gashinan yanzu zai taho ,  murna tashiga yi sosai  tana niyyar kashe wayar ya dakatar da ita , cike da lallab'awa yace " kin manta baki tambayi Mumyn taki ta biyu ba , Sanam tamkar tana gaban su ta tab'e baki sannan tace " nifa Daddy banda wata Mumy bayan tanan gidan  kuma ai ita gata muna tare ,   Hajiya Maimuna dayake wayar Hands free take tana jin abinda Sanam d'in tace , Murmushi tayi na takaici batare da tace komai ba ta mik'e tabar wajen , shima kuma Alhajin bai wata nuna damuwa ba game da jin maganar Sanam d'in , Kashe wayar tayi sannan ta fara janyo kulolin da Hajiya Nafeesa ta jera mata su ,    tuni Hajiya Nafeesa tafara wani shu'umin murmushi , duban Fahad tayi suka had'a ido sannan suka murmusa....
[9/27, 09:52] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter      20.

Sanam tana bud'e kular taga sakwara  sosai taji dad'in ganin nata , janyo d'aya kular tayi tabud'e miyar agusi da ta wadatu da naman rago sai k'amshi ke tashi ,  d'auko guda d'aya tayi tasa a filet tare da zuba miya tajanyo tana fad'in " Mumy tamkar kinshiga zuciya ta kinsan inason cin sakwara , tunda naje Turkey nake kewar cin ta  amman bansamu ba , cike da kissa Hajiya Nafeesa tace " haba my luv kinsan komai da nasan zai faran ta miki ai shinakeso , yanzu dai bari nashiga d'aki na fito nasan lokacin kin gama ci sai kibani labarin Turkey , Sanam tayi murmushi tace " wanne labari Mumy ? sai dai ko labarin bikin da akayi zanbaki , Hajiya Nafeesa tace " ai daman shi nakeso kibani bari na fito....
Fahad shima tashi yayi yabi bayan Hajiya Nafeesa yana fad'in " Aunty ina key d'in motar ki zanfita ? ...

Sanam lomar ta d'aya taji muryar Diyana tana sallama , da gudu Diyana ta taho tana fad'in " Oyoyo my Besty ta , nayi missing d'inki sosai tunda kika tafi ko nemana bakyayi , murmushi Sanam tayi sannan tace "kinsan biki naje dole kimin uziri amman kina raina nima , zama tayi ta janyo filet d'in sakwarar dake gaban Sanam tace " kice nazo asa'a anyi best food d'inki , Sanam tace " wallahi kuwa Mumy ce tamin na murnar dawowata , lomata d'aya kika shigo zaki samin rani kawai , Murmushi Diyana tayi tana fad'in " naji d'in ai nima kinsan inason Sakwara sosai , Sanam tace " to gatanan ai sai kiyi ta fama , zata sake magana wayar ta tashiga ruri , d'auka tayi tana duba screen d'in wayar number Huneed tagani , da sauri ta mik'e tana cewa " Diyana ina zuwa , da kallo Diyana tabi bayan Sanam da kallo tana fad'in " a lallai Besty kinyi kamu wannan rawar jiki haka ,.....

Sanam can bayan gida ta fita sannan ta d'aga wayar , tana d'agawa tayi sallama tamkar ba ita ba , Huneed najin muryar Sanam ya lumshe ido yanajin saukar wani nishad'i , a hankali ya furta " My speacial ya kike ? Sanam sauke wayar tayi daga kunnen ta tana k'ara duban wayar , dagaske Huneed ne yakira ta da My Speacial ko dai kunnen tane ? maganar dataji ya kumayi ne yasa ta maida wayar kunnen nata , ci gaba yayi da magana yana cewa " andawo lafiya ? sai sannan mamaki ya kama Sanam taya yasan ta dawo ma ? murmushi yayi me sauti tana jiyowa yace " kina mamakin ta yadda akayi nasan kindawo ko ? to kibar mamaki kawai dai na tsoka ne kine , murmushi tayi itama sannan tace " yakake ? lafiya lau nake dafatan kindawo lafiya , Sanam tace " lafiya lau nadawo kaima ina fatan nasameka lafiya ? Huneed yace " lafiya lau nake sai dai kawai inason ganin kyakkyawar fuskar Mata ta , Sanam tace " ai sai ka koma gida ka kalleta ko zaka samu sauk'i , batajira yace wani abun ba ta kashe wayar sabo da wani kishi da yataso mata , kwata kwata idon Sanam ya rufe ko gaban ta bata gani ta nufi cikin gida da gudu ta haye sama d'akin ta......

Hawaye ne ke zuba a idon ta ta fad'a kan gadon ta , cikin ranta tace " me yake nufi dani ne ? daga munfara magana sai yadunga min maganar matar sa ina ruwana da ita , sosai Sanam keyin hawaye saboda wani mugun *Kishi* dataji yana taso mata......
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 21.

Huneed tunda yaji yadda Sanam ke magana k'arshe ma ta kashe waya yake mamaki , to shifa yasan har yanzu bai furta mata yana sonta ba , amman taya take da wannan kishi haka ?  to kodai itama kamar yadda yakamu da sonta haka itama ta kamu da nasa ne ? idan kuwa hakane to tabbas zai yi rawa ya juya dan daman fargabar sa ita ,  kuma abinda yasa yasan ta dawo shine   ' Diyana ce tazo wucewa d'azu suna tsaye da Hisham ,  tana ganin su ta k'araso tazo suka gaisa anan take shedawa  Hisham ai Sanam tadawo ,  murmushi yayi sannan a hankali ya furta ai dole na shirya zuwa lallashi ,  tashi yayi ya nufi toilet dan watsa ruwa.......

Kwata kwata Diyana bataga shigowar Sanam ba , hankalin ta na kan cin sakwara da miyar agusi ta ,  dama Diyana akwai shegen kwad'ayi gashi gidan su basu da wani k'arfi sosai , sanadin k'awancen su da Sanam ma a sch suka had'u , Yayan Baban Diyana yana da kud'i shine ya d'auki nauyin karatun ta shiyasa tasamu tayi sch d'aya dasu Sanam ,  ga Diyana akwai gayu da gwalli dakuma shish shigi , ta duk'ufa tana ta cin Sakwarar ta taji muryar Hajiya Nafeesa tana fad'in " Diyana ina kuma Sanam d'in ? sai sannan ta saita kanta dan gudun yarfi , dan tasan halin Hajiya Nafeesa akwai wulak'anci da jin kai ,  gaishe ta tayi tace " Mumy barka da yamma dafatan kin wuni lafiya , Hajiya Nafeesa a tak'aice ta amsa da cewa " lafiya ina Sanam ?  Diyana tace " naga ankira wayar ta tafita waje ta d'aga shine bata dawo ba , Hajiya Nafeesa da sauri ta dubi Diyana tace " taci Abincin nan kuwa ?  Diyana tace " e nashigo nasameta tana ci daga nan muka fara magana sai kuma aka kira wayar tata , wata ajiyar Zuciya Hajiya Nafeesa tayi  idon ta ya rufe kwata kwata tace " Alhamdulillah ,  sannan ta kuma kallon Diyana tace " kin tabbata dai taci ko ? Diyana cike da mamaki tace " ea na tabbata Mumy , cikin ranta tace " meyasa Mumyn Sanam takeso taci Abincin nan haka ? kodai akwai abinda takeso tayi mata ? ganin Diyana ta tafi Nazari yasa Hajiya Nafeesa ta saita kanta tace " kinsan k'awar taki batason cin Abinci shiyasa nadamu , kuma kinga daga tafiya tadawo yakamata ace taci abinci kar Daddyn tq yayi fad'a ,  dayake Hajiya Nafeesa ta k'ware wajen kissa da kisisina tuni ta shigar da Diyana.......

Sanam tuni bacci yayi awon gaba da ita , daman agajiye take ga kuma kuka da tasha  ai tuni tayi nisa a bacci....

Diyana ganin shuru shuru Sanam bata dawo ba yasa ta mik'e dan ta lek'a , dai dai lokacin Daddyn Sanam ya bud'e k'ofar palor ya shigo shima , sunayin karo da Diyana yaji ya tsani ganinta ya had'e fuska sosai ,  Diyana ta rissina tana gaidashi  , wata harara ya wurga mata

yatsa tsaki batare da ya amsa ba yayi gaba , duk abinda yafaru akan idon Hajiya Nafeesa ba k'aramin dad'i taji ba ganin maganin yafara aiki , cikin ranta tace maganinki ai kwad'ayayyi yar banza da wofi , Diyana tunda taga kallon da Daddyn Sanam yayi mata da kuma k'in kula ta dayayi jikinta yayi sanyi , Daddyn da inya ganta har tsokanar ta yake tare da wasa da dariya , amman yau ko kallo bata ishe shiba sai ma harara da tsaki , tabbas inajin akwai abinda yafaru dole tasamu Sanam suyi magana , sai dai tana fitowa harabar gidan bataga Sanam ba , ba inda bata duba ba amman babu Sanam babu dalilinta , cikin ranta tace " to ita kuma ina tayi haka ? gashi duk motocin gidan suna ajiye bare tace fita tayi , har zata koma cikin gidan wata zuciyar tace " karki shiga kuma yanzu Daddy yasa miki duka , tuni ta fice daga cikin gidan batare da ta kuma bi takan neman Sanam ba ....

Alhaji Abba yana k'arasowa Hajiya Nafeesa tafara murmushin kissa tana fad'in " wato anji shalele ta dawo shine aka taho a ganta ko , murmushi yayi yana mejin dad'in yadda Hajiya Nafeesar ke nunawa 'Yar tasa tilo soyayya , ko ba komai hakan yana sawa yaji yakuma santa sosai , zama yayi a d'aya daga cikin luntsuma luntsuman kujerun falor yana fad'in " wai ina take ne ? Hajiya Nafeesa cike da murmushi tace " inajin tana d'akin ta , amman bari naduba nagani ko bataji shigowar kaba , da sauri ta nufi sama dan ganin Sanam d'in ko tana nan , dan ta matsu taga sun had'u yayi mata yadda yayiwa Diyana , wata dariya tayi tare da furta " Sanam ki shirya yau kinzo hannu , sai na rusa miki farin cikin ki saina saka kinzama abar tausayi kuma mak'ask'anciya , haka ta k'arasa cikin d'akin Sanam d'in .....

Tana tura k'ofar tasamu Sanam kwance a gado tana bacci , gashin kanta ya rufe mata duk ilahirin fuskar ta , tsayawa rayi tana mamakin meyasa Sanam d'in bacci a irin wannan lokacin ? tunowa da tayi in Sanam na bacci ba'a tashin ta yasa ta tsaya , dan tabbas in ta tashe ta to rarrashin ta ma sai yazama aiki kafin tayi shuru , har ta juya zata fita taga Sanam d'in ta motsa , da sauri tace " My luv kin tashine ? Sanam ta bud'e idon ta a hankali tana duban Hajiya Nafeesa , a hankali ta furta " natashi Mumyna akwai wani abin ne ? Hajiya Nafeesa tace " Daddyn ki ne yazo yakeson ganinki shine nazo kiranki naga kamar bacci kike , Sanam jin ance Daddy yasa ta mik'e zaune tana fad'in " ganinan zuw Bari nayi wanka dan jikina ciwo yake min , Hajiya Nafeesa tayi murmushin yak'e tace " to shalele inkin fito kisamemu a k'asa , Sanam tace " to tana mik'ewa ta nufi toilet.......

Bayan Minty 10 saiga Sanam ta sauko sanye da riga da siket na wata babbar atamfa , sosai kayan suka amshi jikinta suka mata kyau , kanta babu d'an kwali sai wani k'aramin gyale da ta yafa kalar jikin atamfar , sai kuma filet shoe d'in ta datasa , sosai tayi kyau sai k'amshi ke tashi ajikinta ta ko' inah , tana k'arasowa Daddyn ta yafara murmushi yana fad'in " your welcome my love , a hankali Sanam ta k'araso jikinsa tana murmushi tare da murnar ganin Mahaifin nata , tabbas 'Da da Mahaifi sai Allah wata k'auna ce a tsakanin su me zafi , Alhaji Abba yana mutuk'ar ji da tilo d'in 'Yar sa , dan haka a koda yaushe bayason yin nisa da ita , sundad'e a manne da juna suna murnar ganin juna kafin Sanam tasamu guri kusa da Daddyn nata ta zauna , gaishe shi tayi cike da girmamawa dan Sanam duk iskancin ta tasan darajar gaida

iyaye ,  amsawa yayi cike da so da k'auna yana cewa " kinga yadda kika rame kuwa ? nasan ba lallai kina cin Abinci ba acan , shiyasa nafison muyi tafiya tare saboda baki kulawa ,  Hajiya Nafeesa tamkar gunki haka ta koma tunda Sanam ta fito da yadda taga Daddyn nata ya tare ta , cikin ranta take fad'in " wato da alamar Sanam bataci maganin nan ba kenan ?  tabbas bata ci ba tunda gashi Diyana taci kuma taga Yadda Daddyn Sanam d'in yayi mata ,  tayi nisa cikin tunani taji muryar Alhaji Abba yana fad'in " Hajiya Nafeesa ko bakyaji ne  ? firgigit tace " inaji Alhaji kasan in muna tare da Sanam bana iya sauaran komai sai sautin ta , murmushi yayi sannan tace "   ai gatanan ta dawo sai kitajin sautin muryar ta ta ,  nan suka saka dariya wacce a b'angaren Hajiya Nafeesa yak'e ceb, dan ji take kamar ta mik' e ta shak'e uba da yar saboda takaici ,   sukuwa ko ajikin su sai hira suke cike da nishad'i ,  tuni Hajiya Nafeesa ta mik'e tace " zataje d'aki tadawo ...

Tana shiga d'aki ta d'auko wayar ta ta shiga kiran Hajiya Harira.......

*Rashin Comment* *shine yake sani typing kad'an*🤷🏻‍♀️🤷🏻‍♀️

_Indai zanga Comment  to kuwa zan muku typing me yawa_

*Dan Allah kugyara kudunga Comment*

*'Yar Mutan Kanawa* _Ce_✍🏻🌹😍
[9/27, 09:54] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*Hamdala* *Writer's* *Association* 💪
https://www.facebook.com/111403834371046

✨✨ *{{* *H.W.A* *}}*✨✨

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

⚜️ *BU'DA'D'DIYAR SOYAYYA*

Jameey yar' mutan kankia

*Promo* *Promo* *Promo*

Daga yau 21/5/2022 promo dinmu zai fara , har zuwa 30/5/2022 inshaa Allah , ga yanda promo din yake.

#300-sau biyu a rana
#500-sau ukku a rana
#700-sau hudu a rana

kiyi man wannan number magana danjin yanda zaki biya 08160508316

Chapter 22.

Kuka Hajiya Nafeesa ta fashewa da Hajiya Harira , da sauri Hajiya Harira tashiga tambayar ta " lafiya kike irin wannan kuka haka ? waye ya mutu kuma ? Hajiya Nafeesa tace " wallahi wanda ayi mutuwa da abinda yafaru , dasauri Hajiya Harira tace " sakin ki Alhaji Abban yayi ne ? da sauri Hajiya Nafeesa ta dakatar da kukan tace " ki rufamin asiri ba sakina yayi ba shirin mune dai ya lalace , wani guntun tsaki Hajiya Harira tayi saboda takaici , taso ace ma sakin Hajiya Nafeesan akayi tasamu tayi wuff da Alhajin , a fili kuma tace " garin yaya akayi hakan kuma ? kinfi kowa sanin irin wahalar da mukaci kafin musamu wajen wannan bokan , ga mak'udan kud'in da kika kashe , Hajiya Nafeesa ta goge Hawayen ta tace " duk tarin kud'in

dana kashe bashine yada meni ba , kawai ina tunanin yadda zamu kuma komawa wannan dajin me nisan tsiya , gashi bokan nan kwata kwata bashi da imani wajen cewa sai ya kwanta dani , Hajiya Harira tace " wannan ma me sauk'i ce mutuk'ar buk'ata zata biya , sai dai kar mukoma kizo kisake yin sakaci wani abun yafaru kuma , wai garin yaya hakan tafaru shirin namu ya lalace , nan Hajiya Nafeesa tashiga gayawa Hajiya Harira duk yadda abin yakasan ce , wata ashar Hajiya Harira tayi tana fad'in " shegiyar k'awar tata ce me kwad'ayi munafika , wanda ma da Alhajin ya tsaneta kinga zata rage zuwa gidan sai muyi yadda mukeso , nan Hajiya Harira tashiga kwantar wa da Hajiya Nafeesa hankali har da k'ara tinzura ta akan lallai sukoma wajen bokan , abinka da wacce tayi nisa zuciyar ta ta k'e k'ashe tuni takuma jin wani k'arfi yazo mata , take suka shirya randa zasu koma wajen boka me doki.....

Sanam sai hira suke da Daddyn nata cike da so da k'auna , anan yashigo mata da maganar taje ta gaida mumyn ta Hajiya Maimuna , Sanam take fara'ar dake fuskar ta ta dakushe , cike da shagwab'a tace " Daddy nifa kasan matar nan taka ba sona take ba , koda yaushe naje gidan nan bata da aiki sai yimin fad'a tana yimin wa'azi , murmushi yayi sannan yace " haba Baby kinsan duk duniya bayan ni babu wanda zai soki tamkar ita , ko kin manta itace ta haifeki kinga dole zata soki fiye da saninki , Sanam tamkar wata yarinya tace " wallahi Mumyn nan gidan tafita sona sosai kuma kaima kasan hakan Daddy , shuru yayi yana nazari " tabbas yasan Hajiya Nafeesa nasan Sanam tamkar itace ta haifeta , sai dai yasan baza ta tab'a yi mata irin son da Mahaifiya kewa 'ya'yan taba , amman saboda kar yaja zancen yace " shikenan Baby abar zancen duk sanda kika samu lokaci kije sai ku gaisa da ita , turo baki tayi tana fad'in " to Daddy .......

Huneed tuni ya shirya cikin wani yadi me tsadar gaske , ga wani had'edd'en turare daya fesa sai tashin k'amshi yake , yana fito yashiga falor Hajiyar su d'auke da sallama a bakin sa , amsawa tayi cike da sakin fuska tare da nuna kulawa ga d'an nata , durk'usawa yayi a k'asan cafet yace Hajiya ta barka da wannan lokacin , cike da fara'a tace " Barka kadai My son , wannan wanka daga gani nasan wajen sirikata za'aje , sunkuyar da kai yayi yana dariya kafin yace " Hajiya ta inaso kiyimin addu'a yau zanje na sanar da wacce nakeso inason ta , murmushi tayi sannan tace " koda yaushe ina maka addu'a kai da d'an uwanka , Allah yazab'a muku mataye nagari masu k'aunar ku , Allah yayi muku Albarka tare da sauran 'Yayan musulmi baki d'aya , sannan inaso inkaje kagaida min da ita kace ina maraba da zuwan ta gidan gwarzon d'ana , murmushi Huneed yayi yana mejin dad'in maganganun Hajiyar tasa , mik'ewa yayi yana fad'in " zataji insha Allah Hajiya ta sai nadawo , yasa kai ya fice daga falor cike da farin ciki fal a zuciyar sa , ......

Hajiya Maimuna ce zaune ita da Mahaifiyar ta tana hawaye , share mata hawayen nata Mahaifiyar ta tayi tana fad'in " kici gaba da addu'a Maimunatu insha Allah komai zaizo k'arshe duk tsanani yana tare da sauk'i , wata rana zata gane muhimmancin ki kuma saitayi nadama sosai , yanzu kici gaba da mata addu'a dan addu'arki tafi komai tasiri a wajen ta , muma muna yi miki kuma duk daren dad'ewa komai zai zo k'arshe , da irin wannan dad'a d'an kalaman Hajiya Rabi take kwantar wa da 'yar ta ta hankali duk san da taje gida , yauma tun fitar Daddyn

Sanam ta hau motar ta tayo gidan su dan kawo kukan ta da Mahaifiyar ta ta , Tabbas duk wanda yarasa *Uwa to yayi rashin Babban jigo a rayuwar sa wanda babu madadin ta* , *Allah yajik'an iyayen mu wad'an da suka rigamu hidan gaskiya* , _wad'an da suke a raye kuma Allah kabamu ikon yi musu biyayya_🙏🏻🙏🏻

Sosai Hajiya Maimuna ranta yayi mata dad'i da yadda mahaifiyar ta ta ta kwantar mata da hankali , nan tasaki jiki taci gaba da hira da Hajiyar ta ta har lokacin da tayi mata sallama ta koma gida .......

Hajiya Rabi sosai take tausayin 'Yar tata ganin yadda akayi mata fin k'arfi akan 'yar ta , ita kanta batace ga randa ta tab'a ganin Jikar tata Sanam tazo gidan nata ba , amman haka take kwantar mata da hankali har tasamu ta sauko......

Sanam hirar su suke akan komawar ta sch dazatayi , Hajiya Nafeesa ce ta fito daga b'angaren ta tamkar babu abinda yake damunta , tana zuwa tasamu guri ta zauna hirar suka ci gaba dayi har ita , cikin ranta tana fad'in " kuyi duk abinda zakuyi nan da kwana hudu zan raba ku da farin cikin dake fuskokin ku , sallamar da megadi yayi ita ta katsesu , cike da girma mawa yace " ranki yad'ad'e ana sallama dake a waje , Sanam tasan da ita yake amman ko kallon sa batayi ba , sai Hajiya Nafeesa ce tace " waye yakeson ganin nata ? risinawa yakumayi yace " wani mutum ne a waje ban waye shi ba , Hajiya Nafeesa tace " kaje kace " yashigo ka kaishi d'akin saukar bak'i gatana zuwa , Sanam da sauri ta kalli Hajiya Nafeesa tana fad'in " Mumy taya zakimin haka ? murmushi tayi cike da kissa tace " haba my Luv kinsan dai yakamat ace kinfara sauraren samari dan kin isa kuma kin kai , nan tashiga lallab'a ta har tasamu ta amince zataje , Alhaji Abba yana jinsu ko tari baiyiba yada saka aransa zai fita dan ganin waye yazo gun 'yar tasa , dan yanson ace kowaye yazo to yaasance d'an mutunci ne wanda yasan mutucin ta , wanda zai iya rik'e masa yar sa batare da ta nemi komai ta rasa ba , mik'ewa Sanam tayi ta fita ahaka dan tace babu abinda zata canza ko kuma ta gyara , .....

tana zuwa K'ofar d'akin saukar bak'i taji wani k'amshi yana fitowa , lumshe idanun ta tayi tana son tuna inda tasan k'amshin turaren , ta dad'e a tsaye tana tunanin sannan ta tura k'ofar a hankali tare da yin sallama , Huneed na zaune yana dannan waya yanajin shigowar ta ya d'ago yana amsa sallamar tare da duban ta , Sanam naganin Huneed k'irjinta ya buga take taji wani abu ya tsaya mata a k'irji wanda tarasa ko na farin cikine ko akasin hakan , kafesa tayi da ido tamkar taje tafad'a jikin sa wani kyau datatga yayi mata , tayi nisa a tunani taji yana hure mata ido yana fad'in " irin wannan kallo sai kace baki tab'a ganina ba , da sauri ta rufe fuska tana murmushi tare dajin kunya , shima murmushin yayi yace " barka da fitowa shugabar 'yan rigima , rigimar ki tana da yawa kinsa na rud'e har naga bazan iya jira ba sai nazo , Sanam wata kunya takumaji tamkar ta nitse cikin ranta tace " kardai ace ya fahimci ina kishinsa ? kuma mutuk'ar ya fahimta to tabbas yasan tana sonsa kenan ? a hankali ta furta " wayyo shikenan na rusa ajina a idon sa , Huneed kamar yasan abinda take tunani yace " Sanam dan mace taso Namiji ba laifi tayi ba fa , hasalima hakan yayi duk da baki furta min kina sona ba , amman iya hakan ya bayyana min cewa yadda nakamu da sonki nima haka kike sona , sai dai a zahirin

gaskiya nafi sonki dan tunda ga randa nafara ganinki nakamu da sonki sosai , duk wannan takurar da nayi miki da kuma yadda na dunga bibiyar ki wallahi sonki ne yasa hakan , durk'usawa yayi da gwuiwar sa k'asa yace " Sanam yau ga Huneed a gabanki ina me rok'on soyayyarki , inason kizama uwa awajen 'Yayana sannan ki zama wacce zata zame min bangon jingina duk lokacin da nazo gareki ......

Sanam tamkar zata saka ihu saboda murna , wani dad'i takeji har ranta sai dai kuma ai yace mata yana da mata , to taya zata rayu da wanda yake da mata , dan ita fa ko a sittira batason kishiya balle a rayuwar gidan mijin ta , dan ta tsara rayuwar da zatayi da mijinta mutuk'ar tayi aure , to taya zataso wata takasance tare da mijin nata , ganin shurun da tayi yasa Huneed karaya yana mik'ewa yana duban ta , idanun sune suka had'u waje guda take kowa yaji wani abu tunda ga tsakiyar kansu har ilahirin gangar jikinsu............
[9/27, 09:55] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir* *Rahamanir* *Rahim*

Chapter 23.

Sunfi Minty biyar ahaka kafin Sanam tayi k'arfin halin janye nata idon , Ajiyar zuciya suka saki lokaci d'aya kafin kuma shuru yasa ke biyo baya , k'wan k'wasa k'ofar d'akin ce ta katsesu su dukan su suka dubi hanyar shigowar , Me gadin gidan ne ya shigo d'auke da sallama a bakin sa sannan yace " ranki ya dad'e Alhaji yace kuje keda bak'on naki ku samesa a palor sa , Sanam ta d'aga masa kai alamar to batare da ta furta komai ba , Bayan fitar megadi da kamar minty biyar Sanam tadubi Huneed tace " Bisimillah katashi muje gun Daddy yana

kiran mu , Huneed batare da fad'uwar gaba ba ya mik'e suka jera suka nufi cikin gidan ....

Tunda Jaydeen ya isa gida ya ke maganar Sanam , Mumyn sa ta dube sa tace " My Son. Kodai gamo kayi a hanya ne ? tunda ka dawo kake zancen yarinyar nan , ko abinci kaki tsayawa ka nutsu kaci , murmushi Jaydeen yayi sannan yace " Mumy dan dai baki ganta ba ne shiyasa zaki ce haka , Yarinyar ta had'u sosai Mumy ga ta irin macen da nakeso ce , Hajiya Halima tayi murmushi sannan tace " wacce irin mace ce kake so My son . ? kafad'i ko wacce irin mace ce a duniyar nan , mutuk'ar kud'i zai iya siyo maka soyayyar ta to tabbas kasame ta ka gama , yanzu abinda nakeso dakai shine " ka tsaya kaci abinci kayi wanka sai ka nutsu ka fad'amin yar gidan waye a garin nan na Abuja , Murmushi Jaydeen yayi najin dad'in abinda Mumyn nasa tace , fara cin Abincin yayi yana fad'in " nasan komai nakeso a duniyar nan kuna samar min shi Mumy , dan haka inaso a wannan lokacin a nemomin auren wannan yarinyar dan shine kawai cikar burina a yanzu , nan yaci gaba da bata labarin irin had'uwar da Sanam d'in tayi , har kwatan ta mata yadda take magana yake cike da sauk'i , Jaydeen kenan 'Da d'aya tilo a gurin Ambasador da kuma Hajiya Halima......

Sallama su Sanam sukayi a palor cikin gidan inda Daddyn nata yake zaune shi da Hajiya Nafeesa , amsawa Hajiya Nafeesa tayi d'auke da murmushi a bakin ta , sai dai tana had'a ido da Huneed taji k'irjin ta ya buga , kwata kwata taji tana tsoron sake kallon sa batare da tasan me hakan ke nufi ba , A b'angaren Alhaji Abba kuwa yana kallon Huneed yaji ya masa kwarjini gashi ingarman Namiji wanda kowacce mace zatayi burin kasan cewa tare dashi , take ya fara fara'a tare da cewa " sannu da zuwa sirikina , kunya ce ta kama Huneed ya durk'usa yana gaida Alhaji Abban , da sauri Alhaji Abba yace " mik'e ka zauna a kujera kaji kasaki jikin ka tamkar ba yau kafara zuwa cikin gidan nan ba , Huneed ya mik'e ya zauna a kujera yana murmushin jin dad'in karamcin da Alhajin yayi masa , Sanam zama tayi kusa da Daddyn nata tana murmushi najin dad'in yadda taga mahaifin nata ya karb'i Huneed , gaisawa sukayi cike da mutuntawa sannan Huneed ya juya yana gaida Hajiya Nafeesa , amsawa tayi tana k'ak'alo murmushin dole tare da yi masa sannu da zuwa , mik'ewa tayi sannan ta dubi Sanam tace " My Angel zo muje ki kawo masa kayan motsa baki , haka ake tarar bak'o maza muje kinji , Sanam ta mik'e tana turo bakin shagwab'a tana fad'in " kai Mumy nifa kinsan bansan yadda akeyi ba , da ido Huneed yabi Sanam da kallo a zuciyar sa yana fad'in " ashe a cikin gidan ma haka kike Sanam manya kenan , Alhaji Abba na lura da yadda Huneed d'in ke kallon 'yar tasa wani murmushi yayi irin nasu na manya......

Nan Alhaji Abba ya shiga yiwa Huneed tambayoyi game da asalin sa , Huneed ya gyara zama yafad'awa Alhaji Abba asalin sa da kuma aikin da yakeyi , Alhaji Abba yanajin Huneed yace shi d'an gidan Canal Abdallah marigayi ne yasan Huneed , dan bawani Mahaluk'in da baisan Canal Abdallah ba , yayi aiki tuk'uru a k'asar nan kafin Allah ya amshi ransa , kuma har gobe ana labarin yadda yayi gumurzu da mugayen mutane , Nan take Alhaji Abba ya jinjinawa Huneed da yadda yake k'ok'ari shima , dan da alama shine zai maye gurbin Mahaifin sa , sosai Alhaji Abba yaji ya yarda da Huneed kuma ya amince masa a matsayin wanda zai zama miji ga shalelen 'Yar tasa , gyaran murya yayi sannan yace " naji duk bayaninka kuma na gamsu , dan

haka nabaka izinin kaci gaba da zuwa wajen Sanam har Allah ya dai daita hankulan ku , Allah yayi muku Albarka yasa Alkairi a cikin tarayyar ku , Huneed ya amsa da Ameen tare da rissinawa yana fad'in " nagode sosai Daddy Allah yaja da rai , da Ameen Alhaji Abba ya amsa tare da mik'ewa ya haye sama ....

Sanam ce ta fito ta wata kusurwa rik'e da tire a hannun ta , tana k'arasowa ta ajiye a gaban Hubeed tana fad'in " bisimillah ga abin tab'awa , Huneed ya kalleta yana murmushi tare da kashe mata ido yace " ai bazan iya tab'a komai anan ba sai naji daga bakin gimbiya ta in ta amince dani , Sanam tayi wani wal da ido sannan tace " ni bazan iya soyayya da me mata ba , da ace baka da mata to tabbas zan iya ansar tayinka kodan na rama abinda kamin a baya , da sauri Huneed ya dubeta yace " waye yace miki ina da aure kuma ? Sanam ta kallesa tana hararar sa tare da turo baki tace " waye kuwa ya gayamin in ba kai ba , ko kamanta randa muka fara waya kace na tasoka kan tare da iyalinka , sannan sauran wayoyin ma da muke kullum sai kamin zancen matar ka , wata irin dariya Huneed ya fashe da ita yana duban Sanam , sai dayayi me isar sa sannan yace " ni fa bani da wata mata tsokanar ki nakeyi for sale ne inkin shirya , duban sa tayi ya kashe mata ido ta kauda kai sannan tace " sainayi shawara naga a wajen da yakama ta insaka , Huneed ya taso ya dawo kuda da ita numfashin su na dukan juna yace " abar maganar wasa Babyna wallahi da gaske nake k'aunar ki kuma aure nakeso muyi , yanzu maganar da nake miki Daddy ya amince min akan inzo neman auren ki ya bani ke , da sauri Sanam ta dube sa ya d'aga mata kai alamar da gaske , k'asa tayi da kanta dan tabbas ba wasa a cikin idon sa , ci gaba yayi da magana yace " ina fatan zaki iya zama da Soja ? Sanam bata d'ago ta dube sa ba kuma batace komai ba , Huneed jikin sa yayi sanyi kodai Bata son sa ? wata zuciyar tace " inbata sonka yazatayi kishinka , jin shurun da yayi yasa Sanam d'agowa tana duban sa kafin tace " dama kai Soja ne ? Huneed cike da Comfidence yace " Soja ne ni Sanam ina fatan jin hakan bazai sa ki canza ra'ayi akaina ba , yadda ya marairaice yayi kalar tausayi yasa tace " inaso kabani lokaci zanyi tunani , sannan ta mik'e tafara tsiyaya masa lemo a cup , kallon ta yashiga yi yana zancen zuci " Allah yasa ki amince min dan in har kika k'i to tabbas nasan zan shiga wani halin Sanam , mik'o masa lemon tayi tare da janyo filet d'in su donut da samosa tane fad'in " maza kaci kar muyi fad'a , murmushi yayi yana curb'ar lemon yana fad'in " ai bazan so yin fad'a da Gimbiya taba , sai dai lallashi da tausasawa wanda kayi ada ma angode , Sanam tace " nikuma kasan ban gode ba , dan saina rama duk abinda kamin d'aya bayan d'aya , dariya yasa yana gutsirar Donut d'in yace " haba gimbiya ta kiyi hak'uri dan karkimin horon da zan kasa rik'e kaina , hira sukeyi sosai me dad'i har yayi mata sallama yatafi.......

Bayan fitar sa da kamar minty biyar saiga megadin su ya shigo , har lokacin Sanam na zaune tana murmushi ita kad'ai tare da jin wani nishad'i , zuwa yayi ya rissina a gabanta yana mik'a mata wata leda yace " ranki ya dad'e gashi inji bak'on ki daya fita yanzu , hannu tasa ta ansa sannan ta sallamesa yafita , tashi tayi da ledar a hannu ta nufi sama cikin d'akin ta ....

Alhaji Abba yana hawa sama d'akin Hajiya Nafeesa ya shiga , nan ya zauna yana fad'a mata yadda sukayi da Huneed , yace " nifa yaron sosai ya burgeni dan har na aminta dashi , yanzu kawai sonke Inji ta bakin Shalele in ta amince dashi shikenan , Hajiya Nafeesa ta tab'e baki sannan tace " nikuma Alhaji sai nake ganin kamar kayi saurin yadda dashi , yana da kyau dai kayi bincike akansa sosai dan tabbatar da waye shi , sannan kana ganin Sanam ta dace da ta auri Soja ? gaskiya ni ba irin mijin da nakeso Sanam ta aura bane wannan , Murmushi Alhaji Abba yayi sannan yace " kufa mata akwai ku da san burga , amman fisabilillah ina aibun Soja ? kuma abin burgewa yaron yana kasuwanci sosai to meye laifinsa ? inaso ki sameta kuyi magana mutuk'ar yayi mata shikenan dan nima ya yimin , kuma gashi d'an gidan manyan mutane ko iya nan nasan Sanam tayi mijin da yadace , in kuma itama ra'ayin naki gareta to babu takura Allah yabata wanda zaiyi dai dai da ita , yana gama magana ya shiga toilet d'in dake cikin d'akin.....

Hajiya Nafeesa ta bi bayansa da harara tana fad'in " zaka canza ne dan wannan komawar da zanyi gun boka har da zancen shegen saurayin nata zanje , dan kwata kwata ni baiyimin ba ko kad'an kuma bazai tab'a yimin ba , take ta fice daga d'akin tana kiran number Hajiya Harira......

Sanam tana shiga d'aki tafad'a kan gado tana murmushi , ledar da aka kawo mata ta shiga bud'ewa , wasu manyan turaruka tagani masu tsadar gaske kala kala , sai wani Hankici me kyan gaske da hoton heart a jikin sa sai k'amshi yake , tana duba wata leda daban kuma taga su chocolate kala kala masu tsadar gaske , murmushi tayi tana fad'in tamkar kasan inason chocolate , sai wata Ambulance k'arama data gani ajikinta wata tak'arda an rubuta " _ina sonki da dukkan zuciyata Sanam_ tana bud'ewa taga bandir d'in dubu dari sannan ankuma rubuta " _Gashinan babu yawa ko sweet kinsha_ wani murmushi ta kuma yi tana jin dad'i , tunda take babu wani mahaluk'in daya tab'a bata kyautar kud'i , saboda yadda matsayin ta yake amman yau gashi Huneed yabata , duk da yasan matsayin ta da kuma irin dukiyar mahaifin ta amman baisa ya karaya ba yayi mata kyauta , tabbas wannan Huneed d'in nata nadaban ne , kuma taji dad'in yadda yayi mata hakan ko ba komai ya nuna mata irin k'aunar daya kemata , kwanciya tayi tana duba wannan takardar me rubutu tana ta maimaita kalmar " inasonki da dukkan Zuciyata Sanam.....

Huneed yana k'ara sawa gida ana sallar magariba , arwala yayi sannan ya wuce masallaci , tunda yashiga cikin masallaci bai fito ba sai bayan sallar isha'i , mutuk'ar Huneed yana gari to indai yashiga masallaci baya fitowa saiyayi tilawar k'ur'ani tare da azkar yake fitowa , gida yashiga kai tsaye ya nufi falor Hajiyar su , yana zuwa yasameta ita da Hisham suna hirar su gwanin sha'awa , dan Hajiyar su mace ce ita me janyo 'Ya'yan ta jikin ta , shiyasa sukuma suka maida ta abokiyar shawar su tare da fad'a mata duk wata damuwar su , yana shigowa ya k'araso gunta ya zauna yana fad'in " sannu da gida Hajiyata , murmushi tayi tana fad'in " sannu da dawowa Huneedullah dafatan kabaro sirikar tawa lafiya ? Murmushi yayi sannan yace " nabarota lafiya Hajiya har tace ingaidake kafin tazo , Hisham yafara murmushi yana fad'in " au

kace zance kaje shiyasa naganka kayi guyu sosai tamkar sabon ango , dukan su suka sa dariya Huneed yana fad'in " Naje neman aure ne wacce zata zo ka runga ce mata Aunty , Hisham yasa dariya yace " zance mata Aunty indai zata dunga bani lafiyayyan Abinci , Hajiya tayi dariya tana fad'in " yauwa kaji acici ko baisan komai ba sai ci , nikam naga randa zaka rage wannnan cin Abincin naka Hisham, Hisham yace " aikuwa sai sai in k'ara Hajiya tunda gashi zamu samu kuku , kinsan 'Yan matan zamanin nan akwai iya girki kala kala , dariya suka kuma sakawa baki d'aya Hajiya na fad'in " kai tafican matan zamanin da duk basu iya girkin gargajiya ba sai nasu na iyayi , Huneed yace " ko bata iya ba Hajiya ai sai ki nuna mata kinga kema kin huta shiga kitchen , murmushi tayi sannan tace " baza ayi haka dani ba kuwa , yarinya daga zuwan ta ace tana aikin girki ai sai ta gaji baruwana , yanzu dai gayamin yadda kukayi da ita , nan Huneed yashiga bawa Hajiya da Hisham labarin yadda sukayi da Alhaji Abba da kuma ita kanta Sanam d'in .........

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 24.

Sosai Hajiya taji dad'in yadda Huneed ya sheda mata Baban Yarinyar ya amince masa , nan tayi masa addu'ar samun nassara tare da daidai tawa da Sanam d'in .......

Sanam na zaune a kan gadon ta rik'e da wannan takadda , sai murmushi take tare da d'aukar chocolate tana sakawa abakin ta , wayar tace tashiga ruri da sauri ta d'auka tana duba

screen d'in wayar , number Diyana tagani  da sauri ta d'aga tana fad'in " kina ina k'awata yau anzo har gida wajena zance , wai dama zanga wannan ranar ace ga wani yayi zarrar zuwa wajena da sunan yana sona  ? Diyana tayi murmushi sannan tace " Besty ai kece kike tsare gida dayawa , amman kinsan ko a sch kina da tarin masoya 'Ya'yan Manya wanda suka amsa sunan su a Nageria ,  amman kallo ma basu isheki ba saboda halinki , lallai ko waye wannan ya cika me sa'a dakuma zarrah kuma lallai shid'in Sadaukine a cikin maza , Sanam tayi murmushin jin dad'in yadda Diyana ke kuranta Huneed , duk da itama ta yadda da lallai Huneed jarumine ko acikin mazan ,  a hankali ta furta " tabbas Jarumine sosai Diyana , kuma yayi Nasara a cikin zuciyata  , dan tuni zuciya ta takamu da san shi tuntuni  , Diyana ta k'yalk'yale da dariya tana fad'in " gaskiya da zangan sa a daren nan dana sheda masa cewa ya k'arawa malamin sa kud'i , dan wannan tsayuwar da yayi masa ta dare yayi amfani , dariya sosai Sanam take tana fad'in " wato dan kinji cikina shine zaki tsokaneni ko ? to ai ban sheda masa ina son nashi ba dan haka har yanzu zuciyar sa acikin zulumi take ,   Diyana tace " ai aikin gama ya ruga da yagama tunda har yayi nasarar shiga zuciyarki ai ya wuce gun ,  sosai suka sha hirar su wacce rabi duk labarin Huneed Sanam ke bawa Diyana , a k'arshe sukayi sallama akan zasu had'u gobe a garden wajen hutawa dan sake tattauna wa .........

Jaydeen sosai yasawa Mumyn sa rigimar sai an nemo masa gidan su Sanam ,  Hajiya Halima tace " to yanzu My son a wanne estete take da zan tafi nemo maka ? shuru yayi na wasu lokacin kafin yace " tana  Estate d'in Area 11  kamar haka naji Direban daya zo d'aukar ta ya fad'a ,  Hajiya Halima tayi murmushi sannan tace " to ka kwantar da hankalin ka zuwa safiya sai mu shirya muje  Area 11 d'in  muduba cikin Estate d'in nasu ,  Jaydeen ba haka yaso ba so yayi ace a daren nan Mumyn nasa taje ta dubo masa gidan su Sanam , dan ko sunan ta ma bai rik'e ba  sai dai zanen surar ta dayafi komai tafiya da hankalin sa har yatsaya masa aransa ,.......

Washe gari sai wajen Sha d'aya Sanam ta tashi daga bacci , dama batayi baccin gajiya ba shiyasa bata tashi da wuri ba , abinka da wacce ibada bata dama ba , tana mik'ewa tashiga toilet tayo wanka abinta tare dayin brush , tana fitowa ta zauna gaban Mirror tana shafa mayukan ta masu tsadar gaske , sannan ta d'auko Humra masu k'amshi tabi jikin nata dasu , take tafara wani lafiyayen k'amshi tamkar amarya , Kwata kwata kwalliya ba damun Sanam tayi ba , kwalli kawai tasa a idon ta sannan ta shafa lips stick a abakin ta , take tayi wani kyau na daban tamkar kasace ta , tabbas duk Namijin da yayi tozali da Sanam dole zuciyar sa ta harba , wani kyau gareta me d'aukar hankali ,  ribom ta d'auko tashiga tattaro gashin kanta me uban yawa wanda baya kitsuwa , tana saka ribom d'in ya zubo gadon bayan ta tamkar a indian film   , bud'e wajen kayan ta tayi ta d'auko wasu riga da wando sababbi masu kyan gaske , rufewa tayi sannan ta d'auko turarukan da Huneed ya kawo mata tashiga fesawa a cikin kayan ,  tana saka kayan tasake yin wani kyau tamkar kasace ta , rigar ta tsaya mata iya cinya me k'aramin hannu , shikuma wandon tamkar fela haka k'asan sa ya bud'e tare da wasu duwatsuna masu kyan gaske , mayafin kayan ta yafa d'an k'arami ta rufe kanta sannan tasa filet d'in takalmi tafito daga d'akin tayo k'asa.......

Jaydeen tuni ya shirya yasa Mumyn sa a gaba sun nufo Area 11 , dayake unguwa ce ta masu dashi kuma bawani yawa gidajen ciki suke dashi ba tuni me gadin cikin Estate d'in yagane wacce yake nufi , take ya sheda musu number gidan , wasu mahaukatan kud'i Jaydeen ya d'iba yabawa me gadin tare da yi masa godiya , har k'asa ya durkusa ya ansa yana musu godiya suka wuce ciki .....

Sanam na saukowa ta nufi dinning don karyawa , tana zuwa me aikin su tayi saurin had'a mata tea tana rissinawa tana fad'in " ranki ya dad'e barka da fitowa tafatan antashi lafiya , Sanam batare da ta dube ta ba tace " lafiya taci gaba da danna wayar ta , sak'on Huneed ne ya shigo wayar ai take tafara murmushi , Uwani ta rissina tana fad'in " ranki ya dad'e me zan had'a miki a cikin kayan karin ? Sanam tace " jeki kawai zan had'a da kaina ta fara duba sak'on , kowanne sak'o na soyayya ne masu dad'in karantawa , nan Sanam ta shagalce wajen karan ta sak'on Huneed tare da maimai tasu , .......

Tunda ga k'ofar gate Hajiya Halima tasan lallai ba k'aramin me kud'i bane me gidan , hon sukayi me gadi ya lek'o dan ganin waye , ganin bai dan motar ba yasa ya fito ya k'arasa wajen su , gaisawa sukayi sannan suka sheda masa su bak'ine sunzo gun matar gidan , megadi yace " to Hajiyar tasan da zuwanku ? Hajiya Halima ta yi murmusjo sannan tace " batasan da zuwan mu ba amman kaje ka sheda mata matar Ambasador ce tazo gunta , da sauri Mehadin yace to bari naje nadawo , komawa tayi ciki dan shedawa Hajiya Nafeesa zuwan su , koda yashiga yasamu Sanam sai wayar ta take sha abinta hankali kwance , sallamar ma batasan yanayi ba , har Hajiya Nafeesa ta sauko daga sama ta amsa masa ya sheda mata bak'in datayi , izini ta bashi akan yabarsu su shigo....

Hajiya Halima suna shigowa ciki ta k'ara tabbatar da irin gidan da take so d'an ta ya nemo aure , murmushi tayi tana kallon Jaydeen wanda shima ita yake kallo yana murmushin , K'ofar palor suka tura dai dai lokacin Sanam ta mik'e zata koma sama dan wayar tasu da Huneed ta yawaita , taga kuma kamar Hajiya bak'i tayi ita kuma batason duk abinda zai shigar musu rayuwa , karo taci da Jaydeen tatafi zata fad'i k'asa yayi saurin taro ta jikin sa , a hankali ta bud'e ido suka had'a idanuwa da Jaydeen , wata fad'uwar gaba ce ta ziyarci Sanam cikin ranta ta furta wannan lokacin ma , to meya shigo dashi gidan mu har muka kuma karo haka ? suntafi tunani su dukan su sun manta a inah ma suke sukaji gyaran muryar Hajiya Halima , Da sauri Sanam ta turesa tana mejin kunya , sannan tayi saurin hayewa sama abinta...........
[9/27, 09:59] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee* *MD*

*WOMEN* *WRITERS* *ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir* *Rahim*

Chapter 25.

Jaydeen yayi murmushi tare da binta da kallo har ta haye saman , juyowa yayi ya kalli Mumyn sa sukayi murmushi tare , dai dai lokacin Hajiya Nafeesa ta sauko daga sama cikin shiga ta Alfarma sai zabga k'amshi take , tana ganin Hajiya Halima tasaki murmushi tana fad'in " lale marhabun da manya manya , Hajiya Halima itama tagane Hajiya Nafeesa dan sun tab'a had'uwa so biyu , d'aya a wajen Wankin kai d'aya kuma a Dinner bikin 'yar gidan Hajiya Turai , dan har sunyi musayar contac kafin asace phone din Hajiya Halimar , nan suka gaisa cike da sakin fuska tare da tambayar bayan saduwa , nan danan Hajiya Nafeesa tasa aka kawo musu abin motsa baki , hira suka shigayi sosai shikuwa Jaydeen duk hankalin sa na wajen Sanam , Allah Allah yake yaga takuma fitowa dan yanason yasake ganin ta da wannan shigar , Hajiya Halima ta dubi Hajiya Nafeesa tace " to mufa da magana mukazo akan yaron naki , murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " to meke tafe daku dan tunda kuka shigo naga yakasa sakin jiki , Hajiya Halima tace " dama yarinyar wajen ki yagani sunhad'u a jirgi tun daga Turkey , tunda yadawo bashi da zance sai nata yau dai nasashi a gaba muka fito neman ta , to Allah yasa muka samu gidan ashe ma yar wajen kice , Hajiya Nafeesa tayi murmushi sannan tace " tabbas Sanam ce dan itace taje Turkey , lallai abu yayi kyau to Allah ya tabbatar mana da Alkairi , cike da fara'a Hajiya Halima ta amsa da Ameen , sannan tace " amman ina fatan ba'ayi mata mijiba dan karmuyi nema cikin nema , dariya Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " bakuyi ba dan bata kula kowa saboda karatu takeyi , wani dad'i Jaydeen yaji aransa jin ance bata kula kowa nan ya k'udurta aransa zaiyi yadda zaiyi ganin tazama tashi shi kad'ai , sakkowar Sanam daga sama yasa Jaydeen katse tunanin sa yq zuba mata sex eyes d'in sa , wasu kayan yakuma gganin ta dasu wanda sukaci uwar na d'azu kyau da tsaruwa , gashi sun kama mata jikin ta komai nata ya baiyana , jiyayi tamkar yatashi yatafi da gudu ya d'auketa cak yadunga zagayawa da ita , ko kallon inda suke Sanam batayi ba tanufi hanyar fita daga falor , da sauri Hajiya Nafeesa tace " My luv zo mana , Sanam ta tsaya cak tamkar baza ta zo ba sai kuma ta jiyo ta

tako a hankali , tana k'arasowa ta tsaya tana turo baki tare da cewa " Gani Mumy sauri nake zamu fita nida Diyana , Hajiya Nafeesa tace " baki ga munyi bak'i bane zaki fita ko gaisawa bakuyi ba , Sanam ta d'an turo baki tare da kallon b'angaren da Hajiya Halima suke tace " sannu n ku anyini lafiya , Hajiya Halima cike da sakin fuska tace " lafiya lau My Dauther , Sanam bata sake bi takan su ba tayi sauri juyawa ta fice Abinta , Jaydeen tuni yatashi yabi bayan ta dan yana son suyi magana.....

Hajiya Halima da Hajiya Nafeesa sukayi murmushi ganin yabita , Hajiya Halima taja ajiyar zuciya tace " Allah ya dai dai tasu dai , Hajiya Nafeesa ta amsa da Ameen , suka ci gaba da hirar su irin tasu ta manyan mata......

Sanam na fitowa tuni dama tasa an wanke mata motar , tana fitowa ta nufi wajen motar zata shiga , da sauri Jaydeen yasha gaban ta yana fad'in " haba sarauniyar mata abin kuma 'yar haka ce ? Sanam ta ya mutsa fuska batare da tace dashi kanzil ba , gyara tsayuwar sa yayi sannan yace " wajenki fa nazo amman naga kina neman fita batare da munyi magana ba , Sanam tadube sa a wani shek'ek'e sannan tace " wajena kamar yaya ? dan Allah Malam inason kabarni ina sauri zanfita ne , Jaydeen sosai yaji rashin dad'i abinda Sanam d'in tayi , amman sai ya shanye tare da k'ak'alo murmushi yace " haba Gimbiyata , amman kinsan yadda nadamu dake kuwa ? dan Allah kibani aron minty 5 zamuyi magana plss , dafe kai Sanam tayi sannan tace " Inajinka fad'i abinda zaka fad'a dan sauri nake , Jaydeen yace " Ina Sonki Sanam kuma ina son muyi aure dan Allah kisoni , zanbaki duk wata kulawa plss kisoni My Sanam , Samun kanta tayi da kallon sa kafin tayi murmushi tace " inaso nan da sati biyu kadawo zanfad'a ma duk abinda na yanke , bata jira cewar sa ba ta shige motar ta taja tana zuba hon.Da sauri me gadi ya bud'e mata gate ta fice da mugun gudun nata data saba.......

Jaydeen binta yayi da kallo har ta fice daga gidan , cikin zuciyar sa yake tunanin " meyasa komai takeyi burgesa take , duk irin yadda ta raina masa hankali amman ko kad'an baiji yana jin haushin taba sai ma k'ara shiga ransa datayi , tunowa yayi da yadda 'yan mata ke binsa suna mutuk'ar son sa , har da masu bashi jikin su saboda yayi amfani dasu , tabbas Sanam ta dabance ita kuma tashiga zuciyar sa kuma bayajin zai iya rqbuwa da ita , juyawa yayi yashiga cikin gidan dan yanaso yasamu Number ta wajen Mumyn ta .......

Huneed shida Hisham suna zaune a k'ofar gate d'in gidan su , wannan al'adar Huneed ce indai yana gari , koda yaushe zaka samesa a k'ofar gida shida d'an uwansa suna hira , Sanam ce tazo ta wuce da mugun gudun nan nata da tasabayi , Hisham ya d'ago yana kallon motar wacce har ta k'ule yace " gaskiya wannan yarinyar bataji wato haryanzu bata daina gudun ba kenan , Huneed sosai yaji ransa ya b'aci wato Sanam zata dawo da halinta kenan , wayar sa ya lalubo ya danna kiran ta , har ta katse bata d'aga ba haka ya jera mata kira sau uku amman bata d'agawa, test ya tura mata sannan ya ajiye wayar tasa.....

Tana zuwa unguwar su Diyana tasamu Diyana a tsaye a k'ofar gida tana jiran ta , shigowa

motar tayi sannan suka nufi Garden na cikin Asokoro .......

Hajiya Halima tuni sukayi sallama da Hajiya Nafeesa , nan suka kuma musayar contac tare da alk'awarin zuwan da Hajiya Nafeesar tace zatayi , Jaydeen yadubi Hajiya Nafeesa yace " Mumy dan Allah kibani Number Sanam dan inaso muyi waya , Hajiya Nafeesa cike da fara'a tabashi phone d'in ta tare da gaya masa sunan da zaigani akan number Sanam d'in , Bayan ya d'auka sukayi mata sallama tare da fitowa harabar cikin gidan , siyayyar da Hajiya Halima tayiwa Sanam tabawa megadi ya shigar mata da ita sannan suka tafi......

Sanam da Diyana zaune akan wani had'add'en cafet suna hira , Duk rabin hirar akan Zuwan Huneed ne sannan kuma tashiga bata labarin Jaydeen , Diyana tayi murmushi sannan tace " besty kawai haka zakice min kinyi samari jarumai , zan so ingansu dukan su dan jinjina musu ta yadda suka tunkareki , Sanam tayi murmushi tace " kefa Diya akwai ki da iskanci , nifa kwata kwata ban shirya soyayya yanzu ba dan kinsan yadda nakeson in koma inyi degree dina , in nace zan had'a karatu da soyayya bazan nutsu yadda nakeso ba , sannan shifa Huneed Soja ne kuma kinsan yadda natsani soja da d'an sanda , dariya Diyana ta tuntsire da ita har da rik'e ciki , Sanam ranta yafara b'aci saboda iskancin Diyana , duban ta tayi rai a b'ace tace " meye hakan kuma wannan dariya saikace mahaukaciya , Diyana ta dubeta kuma har lokacin dariya take tace " wallahi dariya kika ban wai bakyason Soja da 'Dan sanda , to dan Allah besty meye aibun su ? ni wallahi inason auren Soja kodan inzai tafi yak'i inrakoshi ina kuka , sannan kuma wallahi sojojin nan akwai iya soyayya sosai , Sanam ta tab'e baki sannan tace " wasu kuma akwai iya duka kuma ina ganin tamkar yanayin sa me dukan ne shi , Diyana tace " taya zai doki wacce yake so ? dan Allah kidaina wannan tunanin kawai ki zab'i wanda zuciyarki ta kwanta dashi , kinsan dai dole zakiyi aure tunda baza asakaki agaba ana kallo ba , Diyana tace " ke kanki kinsan ina da samari 'Yayan manya wadan da suka amsa sunan su , amman ban tab'a jin inason wani ba sai akan wannan Sojan , dan gaskiya tun ina turkey nafara sonsa , kuma a kullum son sa k'aruwa yake a cikin raina , Diyana tace " to ai tunda kina sonsa komai yazo da sauk'i , kawai ki anshi soyayyar sa nasan bazakiyi dana sani ba , nan suka ci gaba da hirar su tsakanin su na kawaye kuma aminan juna...........
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 26.

Sai yamma lik'is su Sanam suka baro cikin Garden , gidan su Diyana tafara zuwa ta sauke ta sannan ta jiyo da motar ta tayo gida.....

Huneed sau kusan takwas yana kiran Sanam amman bata d'agawa , tunani ya shiga yi anya lafiya kuwa ? tun sanda ta fita da gudun nan daga Estate d'in yake dakon dawowar ta , yana zaune a wajen har ogan sa ya kira sa akan yana son ganin sa , haka ya shiga gida ya shirya sannan ya fito da motar ya nufi kiran Ogan nasa.....

Koda Sanam ta dawo gida tana shigowa palor tasamu Hajiya Nafeesa da Fahad zaune suna hira , sallama tayi k'asa k'asa sannan ta nufi hawa sama , da sauri Hajiya Nafeesa tace " Sanam zonan mana , kwata kwata Sanam batasan ganin Fahad shiyasa ta canza fuska da tashigo , k'arasawa tayi kusa da Hajiya Nafeesa tace " gani Mumy , Duban ta Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " waye ya tab'amin ke naga fuskar ki haka babu walwala ? Sanam ta d'an saki fuska kad'an tace " babu komai Mumy kawai nagaji sosai ina buk'atar hutawa , Hajiya Nafeesa tace " kuma gashi inason yin magana dake amman in kin huta sai ki sauko kici abinci sai muyi magana , Sanam tace " to Mumy tana fad'in haka ta juya dan dama a k'age take ....

Da ido Fahad ya bita kafin yace " gaskiya hak'uri na yana k'ok'arin k'arewa , wannan sura me kyau kana tare da ita amman ace har yanzu bakayi test d'in ta kaji yadda take ba , Hajiya Nafeesa ta galla masa harara tana fad'in "kaifa baka da kunya Fahad har yanzu halin nan naka yana nan nabin matan banza , sosa kai yayi yana fad'in " to ai Aunty kinsan abun ne sai da dabaru yanzu , kinsan dai bani da kud'in da zan yi aure yanzu kuma ke kin ki min auren , Hajiya Nafeesa ta kallesa tace " wai dama nice zanyi maka aure Fahad ? wai aikin da kace kanayi a libiya dama k'arya kake , Fahad yace " haba Aunty nawa ne duka kud'in da nake samu da zan yi aure , nifa nafiso nayi kud'i tamkar mijinki in gina gida me kyau wanda yafi nakin nan , dan Allah Aunty ki taimaka kisa baki Sanam ta soni nasan Mahaifinta zai mallakamin kud'ad'e , Hajiya Nafeesa taja Numfashi tace " Sanam bazata Amince da kai ba Fahad , dan ko idanuwan ta ka duba zakaga tsanar ka a ciki , inajin ka gwada mata halin naka shiyasa , amman tabbas

naso ace kuna shiri da ita da ko ta b'angaren ta masamu kud'in da mukeso mu samu , Fahad yace " nifah bawani hali dana nuna mata , kinsan halin shegiyar yarinyar da girman kai tare da wulak'anci , kuma fa duk lefin kine Aunty yarinya k'arama ta dunga wahalar dake , kawai sawa zakiyi a kashe ta sannan akashe uban nata ki mallaki kud'a d'enki mukama gaban mu , duban sa Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " baka da hankali Fahad inason mijina fa kawai dai Sanam d'in ce na tsaneta , kuma inajin rashin dadi yadda Alhaji yake fifita ta akan komai , duk wasu Companoni da Alhaji ya mallaka gida da waje sunan Sanam ne akai , cewa yake ya mallaka mata komai to yanzu ko mutuwa Alhaji yayi me zan tsira dashi tunda banice na haifeta ba , maganar da nake maka yanzun haka Uwar ta wani cikin gareta itama , Fahad da sauri ya furta " kutt kawai kice ke zaman banza kike a gidan nan , Hajiya Nafeesa tace " zaman asara dai dan wannan yafi zaman banza , Fahad yace " in zaki yadda tunda kince Alhajin yakusa yin tafiya ta wata goma me zai hana inyatafi kice masa kina da ciki , da sauri Hajiya Nafeesa ta dubi k'anin nata , d'aga mata kai yayi alamar ae cike da rashin fahimta tace " kamin bayani yadda zan fahimta , Fahad ya gyara zama yace " akwai wata budurwa ta da muke chat kuma anan garin take , to yarinyar iyayen ta talakawa ne shiyasa take fita yawon ta , gata da kula kulen maza kuma tana da saurin d'aukar ciki , zan d'auko ta in kawota gidan nan muyi tarayya da ni da ita har tasamu ciki , kinga da wannan cikin nata zamuyi amfani muce kece me cikin har Allah yasa ta haifesa , ke kuma zaki samu wani likitan da zai miki alllurar da zaki kumbura kidinga canzawa a yadda da cewar kina da cikin , sosai Hajiya tashiga nazarin magangun k'anin nata , tabbas indai hakane Fahad yana da basira sosai kuma ta jinjina masa da irin wannan aider tasa , nan yashiga bata labarin irin hajiyoyin da yake kulawa suma sunsha aikata hakan in suka ga basu haihu ba , take Hajiya Nafeesa tayi na'am da shawarar Fahad sannan tace yakawo mata yarinyar tagani , ......

Sanam na shiga d'akin ta wanka tashiga tayi sannan ta fito , sai a lokacin ta d'auko wayar ta dan ta duba tagani , Miss call 20 tagani ga kuma test kala kala anyi mata , dubawa tayi taga kiran Huneed wajen goma tare da test d'in sa , dafe kai tayi tana fad'in ohh my god na manta kwata kwata da wayar ma , Test d'in dayayi mata ta karanta wanda fad'a yayi mata akan gudun data fita d'azu tanayi , murmushi Sanam tayi sannan a hankali ta furta " shauk'in soyayyarka itace tamin yawa har nake wannan gudun , amman daga yau nadaina dan banaso mu kuma wani fad'an , kiran wayar tashi tashiga yi har ta katse wayar bai d'aga ba , Sanam ta furta wato fushi kayi kaima bazaka d'aga ba kenan , haka ta dudduba sauran kiran wanda duk number d'aya ce kuma batasan number ba , tsaki taja ta ajiye wayar tare da hayewa gado ta kwanta , ..

Jaydeen da Hajiyar sa tunda suka taho daga gidan su Sanam suke hirar ta , Hajiya Halima tace " gaskiya yarinyar tahad'u sosai dole tasace zuciyar Jarumin d'ana , murmushi Jaydeen yayi sannan yace " Mumy yarinyar fa ta had'u sosai ba inda bazan shiga da ita ba , daman Abokaina na cewa saga irin yarinyar da zan aura , aikuwa zasu ganta wacce zatafi duk nasu matan cewar Hajiya Halima , dan tana son duk abinda zai kankarowa Tilon d'anta mutunci , kuma ta shirya tsaf dan bin duk wata hanya da Jaydeen zai samu Sanam , Abinda ya tsaya mata arai shine ganin kwata kwata Sanam bata kama da Hajiya Nafeesa , Sanam Farace Sol har wani jaja takeyi tsabar farinta , gata da wani sirtaccen kyau mara misaltuwa , ga gashi

tamkar 'Yar india ga dirin jiki tamkar dai ita tazab'i halittar ta ,  ita kuma Hajiya Nafeesa ba fara bace kuma ba bak'a bace , kawai dai tana da kyau itama ga kuma dirin jiki , kawar da zancen tayi daga zuciyar ta tana fad'in " inajin ita ko da Mahaifin ta take kama.....

Bayan Huneed yagama ganawa da Ogan sa ya fito yaga kiran Sanam , zama yayi cikin motar sannan yashiga kiran number ta ta ,  sai da ta kusa yankewa sannan Sanam ta d'aga , Huneed yace " barka da wannan lokacin My wifey , Sanam wani lumshe ido tayi tare da janyo filo tana k'ank'amewa dan jin dad'in sunan daya kira ta dashi , murya k'asa k'asa tace " Barka kadai dafatan kayini lafiya , Kashe murya yayi yana fad'in " ban yini cikin sukuni ba tunda banji muryar wacce zata sakani inyini cikin sukuni ba , Murmushi Sanam tayi sannan tace " ayya sorry yau busy nayi dayawa ban samu d'aukar waya ba , Huneed yace " shiyasa naga kinfita da wannan gudun naki da kikamin alk'awari kindaina , Sanam batasan sanda tasa dariya ba tana fad'in " sorry Sojana nadaina daga yau ,  wani dad'ine ya rufe Huneed dajin sunan da Sanam ta kirashi dashi , a hankali ya furta My Wifey d'an mai maita sunan da kika kirani dashi plss , sai sannan Sanam taji kunya ta rufeta da sauri ta kashe wayar , Huneed murmushi yashiga yi nasamun Nasarar mallakar zuciyar Sanam d'in ,  wani nishad'i yajishi aciki nan da nan ya tada motar ya nufi gida dan bazai iya jurewa ba dole yaje yaga sanyin idaniyar sa , .......

Tuni Fahad yakira Maryam a waya ya sheda mata yana son ganin ta , Maryam dayake Allah yasa mata k'aunar Fahad jitayi tamkar tayi tsalle saboda murna , nan ya kwatanta mata gidan Hajiya Nafeesa sukayi sallama , ........

[9/27, 10:00] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 27.

Tuni Maryam ta shirya tsaf ta nufo gidan Hajiya Nafeesa , dan cike take da d'okin sanin dalilin kiran nata da Fahad yayi , tana zuwa k'ofar gate ta kira Fahad ta sheda masa gata nan a k'ofar gate d'in gidan ......

ba ad'auki lokaci ba Fahad yak'araso suka shigo gidan tare , tunda Maryam ke shige shige bata tab'a shiga gidan daya had'u kamar wannan ba , tuni tasaki baki sai kallon ko'inah take na gidan tamkar 'Yar k'auye , Fahad yajanyo ta jikin sa yana fad'in " wannan irin kallon gida tamkar wacce tazo daga Ruga ? Murmushi Maryam tayi sannan tace " ai gidan ne yayi mugun had'uwa tamkar a turai , gaskiya banga laifinka ba Dear daka dawo wannan gidan da zama , dan ko nice Yaya ta take irin wannan gidan wallahi da gudu zan had'o kayana nadawo , dariya Fahad ya shiga yiwa Maryam yana fad'in " ai yanzu ma zaki dunga shigowa duk sanda kike so idan har kin amincewa me gidan da buk'atar ta , Maryam ta dubi Fahad alamar tambaya ? ya d'aga mata kai yace " muje daga ciki sai muyi magana ,.....

Tana shigowa cikin Palor gidan sai kawai taga ashe harabar gidan ba komai bace duba da irin had'uwar da palor yayi , sakin baki tayi tana kallon palor wanda yagaji da had'uwa tamkar a turai , ba kowa a palor shiyasa Maryam tasaki jiki tana k'arewa palor kallo , Fahad ya mik'e yana ce mata " bari naje nayiwa Hajiya Magana kinji , Maryam tace " to batare da ta dube saba , sama ya haye abin sa ya nufi d'akin Hajiya Nafeesa.......

Sanam tunda tagama waya da Huneed takejin wani dad'i na ratsa duk ilahirin jikin ta , mik'ewa tayi tafad'a toilet dan yace mata gashinan zuwa , samun kan ta tayi da murnar son ganin sa dan haka dole tayi masa kwalliya ta musamman ......

Hajiya Nafeesa na zaune suna waya da Hajiya Harira Fahad yashigo d'akin , sallama tayi wa Hajiya Harira tana fad'in " sai mun sake waya ta katse wayar , duban Fahad tayi sannan tace " lafiya kuwa ? Fahad ya zauna a hannun kujerar dake bedroom d'in nata yace " Yarinyar nan da zamu sa aikin itace ta k'araso , Hajiya Nafeesa tace " har tazo kenan , kaje kufara magana ganinan zuwa ka gaya mata komai da muke so tayi kafin nazo , Fahad ya mik'e yana fad'in " to shikenan sai kin sakko , har yaje bakin k'ofah zai fita Hajiya Nafeesa tace " Fahad inaso kaduba ko 'inah na palor nan ka tabbatar ba kowa dan banaso muyi magana wani yaji , Fahad yace " angama Hajjaju yasa kai yafice daga palor......

Koda Sanam ta fito daga wanka zama tayi a gaban Mirror tayi kwalliya ta musamman , bayan tagama tabi jikin ta da wata had'add'iyar Khumra , bud'e dirowar kayan ta tayi tafara duba wanda zata saka , idanun tane suka sauka kan wata atamfar ta sabuwa d'inkin riga da

siket strike  gown , tsagar dake bayan siket d'in abud'e take ko kad'an ba'arufe taba , sosai kayan suka kama jikin ta , hips d'in ta tamkar an dasa mata shi haka yayi , d'an kwalin ta ta d'aura dan Sanam sosai ta iya d'aurikan d'an kwali kala kala , fesa   turatuka daya kawo mata tayi sai mur mushi take , mayafi kalar atamfar ta d'auko k'arami tare da wani hill d'in takalmi tasa , kana ganin ta sai kazata wani gagarumin biki zataje irin had'uwar datayi ,  tana cikin saka takalmi kiran wayar Huneed ya shigo wayar ta , sai da takusa yankewa sannan ta d'aga yace mata ya iso ,  nan tace masa ya k'arasa d'akin saukar bak'i gatan zuwa , dama tuni tasa angyara d'akin tare da turareshi da turaruka masu k'amshi ,  sai da tabari minty 10 tayi sannan ta fito daga d'akin nata tanufo k'asa ...

Fahad tuni ya wassafawa Maryam abubuwan da suke so zatayi ,  duk shaid'an cin Maryam sai da ta girgiza da batun su ,  amman yadda Fahad ya shiga kwad'ai ta mata yadda zata samu kud'i da irin yadda zata huta tuni taji ai abun ma bakomai bane , ita da tasaba yin ciki ta zubar so d'aya ne ma ta haihu ta yarda jaririn tun randa yazo duniyar , bare wannan da gata zai samu itama ta samu ai ta warke zata amince da wannan abun ko dan son datakewa Fahad d'in ,   tana cikin zancen zuci suka hango sakkowar Sanam daga sama cikin takun ta na isa da izzah ,  tuni Maryam tasaki baki tana kallon Sanam  cikin ranta fad'i take " tsarki ya tabbata ga Mahaliccin wannan sura me kyau , tabbas wannan yarinyar ta had'u tamkar ita tayi kanta ,  lallai 'Yayan masu kud'in nan suna hutawa ga kyau ga kud'i kamar su sukafi kowa a gun Allah , da sauri tace " Astagafirlah Allah muma kabamu kud'in nan muhuta ,  Sanam nagama sakkowa ko kallon wajen da suke batayi ba bare tasan Allah yayi ruwan su agun , haka ta fice daga palor tabarsu da shak'ar k'amshin ta , Fahad har wani lumshe ido yake yana bin Mazaunan ta da kallo har ta fice ,  cikin ransa yake kissima yadda zai sarrafa Sanam duk randa ya damk'eta a hannun sa ,  Maryam ta dubesa tace " Dear wannan kyakkyawar Babyn fa Yarinyar Auntyn naka ce ? Fahad yace "ea yarinyar tace  Maryam tace " gaskiya ta had'u sosai tamkar ita tayi kanta , zata sake magana tahango Hajiya Nafeesa tana sakkowa itama ,  Acikin second biyu Maryam ta k'arewa Hajiya Nafeesa kallo taga yadda suke kama da Fahad ,  cikin ranta tace "inajin ita yarinyar da Babanta take kama dan ta nunka Hajiya Nafeesa kyau sosai ,  ....

Tunda Sanam tayi sallama palor bak'i Huneed ya shak'i k'amshin ta , tana shigowa yayi mutuwar zaune saboda tsabar had'uwad dayaga tayi masa ,  tasbihi yashiga yiwa Allah tare da addu'ar Allah ya mallaka masa Sanam a matsayin mata yasan yagama dacewa ,  haka ta k'araso har kusa dashi tana murmushi tashiga gaidashi , yaji dad'in yadda Sanam ta gaidashi tare da nuna masa ashe itama tana da tarbiya ba laifi , duk yadda yake tunanin Sanam sai yake ganin ashe tana da dad'in zama  , yasan da sannu zata dawo yadda yake buk'ata insha Allah , nan Huneed yashiga tambayar ta ya Mumy da Daddy , tace"  Mumy Ifylau take  Daddy kuma yana d'aya gidan bangan saba amman nasan Ifylau yake , Huneed ya d'an dubeta da mamaki a fuskarsa yace " dama Daddy matan sa biyu kenan ?  Sanam tace ea su biyune amman nidai guda d'aya nasani Mumyna bansan wata ba bayan ita , Murmushi Huneed yayi yana duban Sanam yace " wato kishi kike taya Mumyn ki ko ? canza fuska Sanam tayi tana fad'in " plss Sojana mubar wannan maganar muyi hirar mu kaji , ganin batason maganar yasa Huneed yayi shuru tare da d'auko wata hirar daban.......

Hajiya Nafeesa tana zuwa Maryam ta gaida ta cike da girmamawa , Hajiya Nafeesa ta kalleta cike da kulawa ta amsa , tambayar Fahad tayi akan yafad'awa Maryam komai da suke buk'ata tayi ? Fahad ya amsa da nafada mata kuma ta amince , Hajiya Nafeesa tadubi Maryam tace " kinji komai ina fatan bazamu samu matsala ba  ? kuma inason wannan Abun yazamo sirri tsakanin mu , daga ke sai Fahad saini banason surutu dan kinsan koni wace  duk abinda naga zai ban matsala zan kaudashi , Maryam tayi kasa da kai tana fad'in " Insha Allah bazan gayawa kowa ba komai kikeso nayi Alk'awarin yi miki shi , Hajiya Nafeesa tace " yauwa kiturawa Fahad account Number dinki zaisa miki kud'i sai najiki , tana kaiwa nan ta mik'e ta ta haye sama abinta..........

*Tabbas in banga Comment ba bazan cigaba da Typing ba*😡😡😡
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter     28.

Maryam bin Bayan Hajiya Nafeesa tayi da kallo tana k'issima ina ma itace a wannan matsayin ,  Fahad ne ya katse mata tunanin ta yace " to My Baby kinji komai kuma ina

fatan zaki bamu had'in kai ? Murmushi Maryam tayi sannan tace " angama Oga na ai farin cikin ka kai da Auntyn mu nima shine nawa , Fahad ya dubeta yace " kizo mushiga daga cikin d'akina tun yau nafara aikin samo Baby Boy , Maryam tawani kashe masa ido tana mik'o hannu alamar ya d'auketa , murmushi Fahad yayi sannan yace " Baby ai kinyi nauyi dayawa kawai ki mik'e mutafi , turo baki Maryam tayi har sai da Fahad ya d'auke ta ya nufi bed room d'in sa da ita......

Sosai Sanam tasaki jikinta da Huneed suka sha hirar su , sai wajen goma da rabi yayi mata sallama ta rakoshi har jikin motar sa yatafi , juyowa tayi d'auke farin ciki akan fuskar ta , batasan meyasa in suna tare da Huneed kwata kwata bataso yayi nesa da ita ba , dai dai da zata shiga k'ofar palor Fahad da Maryam suka fito suma hannu cikin hannu , tsayawa Maryam tayi cak tana kafe Sanam da idanu , Sanam mamakine ya kamata naganin Fahad tare da mace sun jero daga cikin gidan hannu cikin hannu , koda yake bazatayi mamakin ganin hakan ba tunda tasan waye Fahad farin sani , kallo d'aya tayiwa Maryam ta d'auke kai tare da bi ta gefen su ta shige abinta......

Maryam ta dubi Fahad tace " gaskiya wannan yarinyar Auntyn naka ta had'u sosai , duk da naga kamar zatayi rashin Mutunci amman tashiga raina sosai tayimin , dama zaka had'amu k'awance wallahi dana ji dad'i , Fahad ya dubi Maryam yace " mutuk'ar kina son zaman lafiya koda kinzo gidan nan to karki shiga shirgin Sanam , bata da mutunci ko kad'an batak'i ta tsinkaki a cikin taron mutane ba , Maryam tace "wow My Dear sunan nata ma wallahi ya had'u gaskiya tahad'u shiyasa sunan ta ma yake had'add'e , Fahad ya rik'o hannun ta yana muje kar Sanam ta zautaki tun d'azu sai yaba kyanta kike , Maryam tayi murmushi tana fad'in " ai dole na yabi kyanta amman da alama ita da Mahaifinta take kama ko ? Fahad kawai ea yace tare da d'auko wata hirar , dan shi yafara gajiya da tambayoyin Maryam d'in tamkar 'Yar jarida......

Jaydeen tunda suka koma gida da Hajiyar sa yake faman kiran wayar Sanam , sai dai ko sau d'aya bata tab'a d'agawa ba , har a whaspp yayi mata magana nan ma bata dawo masa da reply ba , gashi kullum soyayyar ta k'ara ninkuwa take cikin ransa , tunyana hak'uri har yagaji Hajiyar sa tasan halin dayake ciki , d'aukar waya tayi ta kira Number Hajiya Nafeesa , bayan sun gaisa takeyi mata bayani akan k'in d'aga wayar Jaydeen da Sanam keyi , sannan ta k'ara da cewa shine dalilin kiran nata taji ko lafiya kuwa ? Hajiya Nafeesa tasan halin Sanam sarai bata da mutunci , musamman indai batason Abu to bataso ko kad'an ya rab'e ta , cikin iya siyasa da kissa tace " kinsan Halin yaran yanzu tunda ga ranar da kukazo na gaya mata muka shiga wasan b'uya da ita , kuma inajin ba lallai in tana da number tasa ba , amman insha Allah zan mata magana zata d'aga , sannan A bawa My Son d'ina hak'uri Sanam tamkar tazama tashi angama , Hajiya Halima akayi dariyar jin dad'i ta shiga godiya tare da addu'ar Allah ya daidai tasu , Nan suka tab'a hira kafin suyi sallama da juna......

*Bayan kwana biyu*

Tuni Soyayyar Huneed da Sanam tayi k'arfi sosai , koda yaushe suna mak'ale da juna a waya suna shan luv , saboda Huneed Sanam taji bazata iya fita wata k'asar karatu ba , dan

haka ta zab'i tayi karatun ta a nan , Daddyn Sanam sai shirye shiryen tafiya yake zuwa Jamus , sosai yake jin dad'in had'uwar Tilon 'Yar tasa da Huneed , yagama yabawa da hankalinsa da kuma irin yadda yake ja jurtacce , cikin satin da Alhaji Abba zai tafi Jamus Allah ya sauki Hajiya Maimuna wato Mahaifiyar Sanam , ansamu Twins mace da Namiji cike da k'oshin lafiya , karkiso kiga Murna wajen Alhaji Abba tun A asibiti yake kiran wayar Sanam , sai dai kwata kwata bata d'aga ba saboda lokacin tana tare da Huneed , itama Hajiya Nafeesa tana wanka tabar wayar a palor k'asa shiyasa batasan yakira ba , ganin haka yasa Alhaji nufo gidan Bayan an sallamesu daga asibitin yakawo su gida , yana shigowa gidan yasamu Huneed da Sanam a farfajiyar gidan suna hirar su cike da nishad'i , tana ganin sa ta mik'e tana murnar ganin sa , shima baki bud'e ya nufosu yana murmushi tamkar wanda akayiwa Albishir da gidan Aljannah , kafin ya k'araso tuni Huneed shima ya mik'e ya nufesa yana rissinawa yana gaidashi , cike da sakin fuska ya amsa yana tambayar sa 'yan gidan , Huneed yace " lafiya lau suke Daddy duk suna gaidaka , ina amsawa sosai nima in ka koma ka gaidamin da Hajiyar taka , ..... Zataji insha Allah inji Huneed...

Alhaji Abba ya dube su yace " Abin farin cikine yasameni tare daku baki d'aya , Sanam tayi murmushi tace " ai tunda kataho nagane hakan Daddy meyasamu ? murmushi yayi sannan yace Mumyn ki ce ta haifa miki k'anne Twins , Suna nan kamar su d'aya dake har sun so ma sufiki kyau , Nan danan fuskar Sanam ta canza daga murmushi zuwa b'ata fuska , shikuwa Huneed tuni ya saki murmushi yana fad'in " Masha Allah Allah yarayasu yayi musu albarka , Lallai munyi k'anne har naji d'okin nagansu , duban Sanam yayi yaga canzawar datayi lokaci guda duk wata walwala ta tafi daga fuskar ta , Alhaji Abba inda sabo yasaba da halin Sanam na rashin jituwar da batayi da Mahaifiyar tata , duk da tunfarko yana da laifi dan ko kad'an bayaso ayiwa Sanam fad'a , duk rashin kunyar da zatayi wa Hajiya Maimuna baya tsawatar mata , amman ya d'auka in taji anyi mata k'anne zatayi murna sai yaga sab'anin hakan , duban ta yayi yace " My luv bazaki tayani murnar samun Yara ba kenan ? kin manta koda yaushe kina fad'in yaushe za'a haifa miki k'anne wanda zaki dunga wasa dasu kina jin dad'i , amman yau gashi nazo miki da albishir kinyi shuru ko murna bakyayi da hakan , Sanam ta turo baki tana fad'in " Daddy nifa nafison ace Mumyna ce tanan gidan ta haifamin k'anne , ni kasan ba zuwa nake gidan waccan Mumyn ba kaga baruwana da yaran data haifa , kuma Daddy har kafara cewa sunfini kyau wato zaka koma Sonsu kenan nikuma kadaina sona , Alhaji Abba yayi murmushi yana duban Sanam wato kishi zata fara dasu kenan , Huneed shima murmushi yayi duk da cikin zuciyar sa yana tunanin meyasa Sanam kwata kwata batason Matar Daddyn nata , tabbas yana ganin tsantsar kiyayyar matar a idon ta duk da baisan me tayi mata ba , haka Daddy yashige ciki yana fad'in " bari naje nayiwa Hajiya Nafeesa Albishir , ....

Koda Daddy yatafi Huneed ya dubi Sanam yace " Baby meyasa abin farin ciki yasamu Daddy amman ke bazaki taya shi ba ? karki manta in ita mahaifiyar yaran ta kasance me laifi a gunki to ai su yaran basuyi miki komai ba , asalima su basusan komai ba a yanzu sai Mahaifiyar su , dan haka karki k'ullacesu a cikin zuciya kijasu ajikin ki tunda sud'in jininki ne kuma 'Yan uwanki ne , inaso ki shirya gobe In Allah ya kaimu zaki rakani muje tare mugan su , Sanam duk jikin ta yayi sanyi game da maganganun da Huneed yayi mata , kuma ko kad'an bata yi masa musu indai yace mata Abu , haka ta amsa masa da Allah ya kaimu suka ci gaba da hirar su...

Lokacin da Alhaji Abba ya shigo palor dai dai lokacin Hajiya Nafeesa ke saukowa daga sama , yana ganinta yasaki murmushi yana kallon ta , itama martanin murmushin ta maida masa tare da kashe masa ido , tana k'arasowa tashige cikin jikin sa , shima rungumeta yayi yana fad'in " d'awisu sarkin ado sannu da fitowa gimbiya ta ,  Hajiya Nafeesa takuma lafewa a jikin sa tana fad'in " Alhajina kadawo lafiya ina kewarka sosai , Alhaji Abba yace " ai nayita kiran Wayar ki keda Babyn ki baku d'aga ba , dama sonake inyi muku Albishir munsamu k'aruwa , tuni Hajiya Nafeesa gaban ta ya fad'i ta d'ago tana duban Alhaji Abba sannan tace " waye ya haihu ?  Alhaji Abba cike da murmushi yace " Hajiya Maimuna ce ta haifo mana Twins mace da namiji ,   ai jitayi tamkar an soka mata wuk'a wani abu ya tsaya mata a k'irji yakasa wucewa , sai a hankali ta saita kanta gudun karya gane sannan tace " Alhamdulillah kace munyi yara Masha Allah , Allah yaraya su yayi musu Albarka  , nan tashiga nuna masa murnar ta wacce a iya bakice batakai zuci ba....

Alhaji Abba sosai yaji dad'in yadda Hajiya Nafeesa ta nuna farin cikinta , har addu'a yake mata akan Allah yabata itama  saboda kyan halinta , baisan nan cikin zuciyar ta cike take da tsanar gudan jinin nasa ba , dayasan yadda takeji a yanzu da ya gaggauta tashi ya fita dan tasamu tayi kuka ko abunda ya tsaya mata a zuciya zai wuce........

[9/27, 10:02] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATIN* 📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Raheem*

Chapter 29.

Sama Alhaji Abba ya haye yana fad'in " yaufa ciki na babu komai ataimako da ruwan lipto kafin asamar min abinda zanci , Hajiya Nafeesa tabishi da harara amman a fili ta furta " Angama Angon k'arni , murmushi Alhaji Abba yayi cikin zuciyar sa yana jin dad'in sunan da takirashi dashi , .....

Hajiya Nafeesa tana shiga cikin kitchen tasa kuka mara sauti , yanzu ta k'ara tabbatar da cewa Hajiya Maimuna tayi mata zarrah ta ko ina , dana sani tashiga yi na irin abubuwan datayi a baya , dan danan Abubuwan dasu faru a baya suka shiga dawo mata cikin kwakwalwar ta.......

*Wacece Hajiya Nafeesa*

Malam Umar shine asalin Mahaifin Hajiya Nafeesa , haifaffiyar garin Maiduguri ce asalin Bare bari , Mahaifin ta Malam Umar Da Mahaifiyar ta Falmata , su Uku iyayen su suka Haifa Tahir Nafeesa da Fahad , Mahaifin su bawani me k'arfi bane amman yana da wadatar zuci , Mahaifiyar su tana sana'ar ta ta hannu a cikin gida , da haka suke rufawa juna asiri suke zaune lafiya , tun tasowar Nafeesa take da buri sosai , ko cikin k'awayen ta tana da nuna itad'in me aji ce da kuma nuna itad'in yar wani ce , Ba laifi Nafeesa kyakkyawa ce sai dai Bak'a ce ita ko kuma ince chocolate colour , tana da tsayi me tafe da dirin jiki shiyasa take rud'a maza sosai da wannan surar ta ta , Nafeesa tana da son abin duniya shiyasa duk saurayin da yazo gunta in taga babu mamora atare dashi take yagashi , hakan yasa duk samarinta suka kasance attajirai masu kud'i sosai , sai dai duk cikin samarin nata ba wanda ke sonta da aure sai dai su shek'e ayar su.....

Tuntana b'oye b'oye kar iyayen ta sugane har suka fahimci halin data ke dashi , Nan Mahaifinta Malam Umar yayi ta fad'a yana cewa sai ta fito da miji yayi mata aure ko kuma ya bata wanda yayi masa , akwai wani Alhaji da sukafi shek'ewar su tare , sosai takejin dad'in Mu'amala dashi dan haka tasamesa da maganar itafa agida andame ta akan tayi aure , dan haka kawai ya turo gidan su suyi aure tunda suna son juna , Alhaji Dauda yanason Nafeesa sai dai shi ba soyayyar aure yake mata ba , Amman ko dan ya huta da ita dole ya aureta na wucin gadi tun da tana sonsa , batare da b'ata lokaci ba yaturo akayi bikin su shida ita....

Bayan tarewar ta a gidan sa tagane Matan sa Uku Yayan sa goma sha takwas , haka ya had'asu gida d'aya tashiga takurar gaske , dan kwata kwata matan sa basu da mutunci haka ma 'Yayan nasa , dan ma itama bata da mutuncin shiyasa suke shakkar ta kad'an.....

Tana shiga tasamu ciki Alhaji Dauda naganin haka yasa ta agaba akan saita zubar , shifa bai aurota dan tayi ciki yanzu ba kawai yanaso su huta ne shida ita , Nafeesa tace itafa bazata zubar da ciki har sai ta haifesa , nan Alhaji Dauda yafita sabgar ta ko kallo bata ishe shiba , a hankali tagane duk matan gidan sune suke d'aukar nauyin yaran su wajen karatu da maka

mancin su , ganin haka yasa taje ta samu Alhajin Akan ta shirya aje a zubar da cikin , dan itakam bazata iya wahala da yara ba haka kawai wanda azubar ta huta , haka kuwa akayi Alhaji Dauda baki har kunne ya d'auketa sukaje aka zubar da cikin , tunda ga lokacin Alhaji Dauda yashiga bawa Nafeesa kwayoyin hana d'aukar ciki , itama batare da damuwa ba ta dunga d'ibgawa cikin ta dan son faran ta masa rai , ana haka ta wayi gari Mahaifar ta tasamu matsala ko ciki bazata iya d'auka ba , anan kuma Alhaji Dauda ya fara tsiyacewa ko Abinci ba'aci A gidan sa , tuni Nafeesa tashiga yi masa iskan ci kala kala har sai da yagaji yasaketa , yana sakin ta tadawo ruwa ta goge tamkar batayi aure ba taci gaba da iskancin ta , tun Malam Umar nayi mata fad'an takuma wani auren har yagaji ya k'yaleta .....

Ana haka suka taho kawo Amarya Abuja wata k'awarta , Anan Allah ya had'ata da Alhaji Abba ya nuna yana sonta , tuni ta amince duba da yanayin data gansa Alhajin burni ga kud'i ga kuma Kyau , ya sheda mata yana Mata kuma shekarsu hud'u da aure amman bata haihuba , Sosai Nafeesa taji kishi akan matar tasa , dan tasan tabbas matar sa tana hutawa ina ma bashida mata ita kad'ai zai aura , amman jin dad'in ta guda d'aya jin ance matar tasa bata tab'a haihuwa ba , tana komawa Alhaji Abba yaje gar Maid neman auren ta , bawani jan lokaci aka d'aura musu aure Amarya Nafeesa ta tare gidan mijinta dake Abuja.....

Bata dad'e da tarewa ba Allah yabawa Hajiya Maimuna ciki , kar kaso kaga murna wajen Alhaji Abba , Hajiya Nafeesa tayi bak'in ciki sosai amman saboda kissa sai take nuna tamkar tafi kowa murnar samun cikin , saboda wannan ciki da Hajiya Maimuna tasamu sai da Alhaji Abba ya biyawa mutum arba'in Hajji , ciki harda iyayen Hajiya Nafeesa da ita kanta da kuma Yayan ta Tahir , .....

Ciki na shiga wata tara Alhaji Abba yadaina zuwa ko'inah , kullum yana tare da Hajiya Maimuna yana bata kulawa , wata ranar Alhamis ta tashi da nak'uda akayi asibiti da ita , cikin sauk'i batare da tasha wuya sosai ba Allah yabata 'Yar ta kyakkyawa me kama da ita , 'Yan Uwa da Abokan Arzik'i sosai suka tayasu murnar Samun K'aruwa , Hajiya Nafeesa cike da kissa tashiga hidima kullum tana gidan Hajiya Maimuna tana rungume da Da Jaririya , kayan barka akwati set goma ta had'awa Jaririya duk saboda iya kissa , sosai Alhaji Abba yaji dad'i na irin yadda take nunawa gudan jinin sa Soyayya , itama Hajiya Maimuna sosai taji dad'in irin hidimar da Hajiya Nafeesar keyi , Ranar suna yarinya taci Suna Hafsat sunan Mahaifiyar Alhaji Abba suke kiran ta da Sanam , sun sha hidima sosai sannan kowa ya watse aka bar me jego da Baby Sanam , tundaga nan Hajiya Nafeesa ta shiga yin Magiyar abata Sanam in antashi Yayeta , lokacin da aka Yayeta Alhaji Abba da kansa yad'aukota batare da Hajiya Maimuna tace kanzil ba , dan dama ita macece me hak'uri basawa ba fitar wa , tunda ganan rik'on Sanam yadawo k'ark'ashin Hajiya Nafeesa , kuma tunda ganan tashiga horor da Sanam da tusa mata ak'idar tsanar Mahaifiyar ta , ....

Wannan shine tarihin Hajiya Nafeesa a tak'aice ...... .......

*kuyi Manegi*✍🏻
[9/27, 10:04] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 30.

Ajiyar Zuciya Hajiya Nafeesa tayi tare da yin wani murmushin mugunta , tabbas Lokaci yayi da zata fara yak'i da Hajiya Maimuna , a haka ta gama had'a masa ruwan lipton d'in ta fito daga kitchen ta nufi sama , karo taci da Sanam zata sakko itakuma , Hajiya Nafeesa cike da kissa tace " Baby ashe munsamu k'aruwa Mumyn ki tacan gidan ta haihu , ya mutsa fuska Sanam tayi sannan tace " nifa ba ruwana da haihuwar ta , gashi daga haihuwar ta har Daddy yafara cewa wai yaran sunfini kyau , aikuwa Hajiya Nafeesa cikin zuciyar ta wani dad'i taji ya ratsa ta , dan tasan Halin Sanam da son yara da kusan kullum sai tasa ta gaba da tambayar yaushe zata haifo mata Baby , ko kuma ta dunga rigimar itama sai an haifo mata k'anne tunda taje gidan su k'awayen ta taga suna da k'anne , a haka har ta girma tana k'ulaficin ganin tana da k'anne , sai gashi k'annen sun samu amman bata murna da samun su , wani dad'i Hajiya Nafeesa taji sannan ta dubi Sanam tace " kwantar da hankalin ki Babyna , kinsan Daddyn ki da tsokana amman nasan ko rabinki bazasu kamo a kyau ba , wani murmushin jin

dad'i  Sanam tayi sannan tace "shiyasa nake k'aunar ki Mumyna , nasan kece kad'ai bazaki juya min baya ba , Daddy kuwa nasan yanzu batani yake ba ta sababbin Babys d'in sa yake , Hajiya Nafeesa tace " Rabu dashi ai da tsohuwar zuma ake magani ,  kece dai tagaban goshi ko ank'i ko anso ,    Sanam tayi murmushin jin dad'i tare juyawa zata sauka daga benen ......
Har ta kusa sauka Hajiya Nafeesa ta d'aga murya da cewa " yaushe zakije kiyi mata barka tare da gano jariran ?  Sanam ta juyo tana fad'in " Mumy nifa wallahi banson zuwa amman Huneed yace dole na shirya gobe muje tare  , wata fad'uwar gaba Hajiya Nafeesa taji dan ko kad'an ita dai wannan Huneed d'in bai yi mata ba  ,  tunda tafara ganin sa taji ta tsanesa  gashi kuma yadda ta fahimta Sanam tafad'a soyayyar sa ko daga ganin yadda take rawar k'afa dashi , cike da kissa tace " yauwa nagode wa Huneed da ya miki hakan , in ba haka ba nasan ba zuwa zakiyi ba lallai yayi min maganinki , turo baki Sanam tayi cike da Shagwab'a tana cewa " au Mumy haka zaki ce ma kenan  ? kawai dai zanje ne shima badan shi ba sai dan ra'ayin kaina sannan kuma inason inga yaran da Daddy yace sunfini kyau ,   Murmushi Hajiya Nafeesa tayi tana nufar d'akin ta tana fad'in " baki da dama Baby kedai akwai rigima , cikin ranta kuma tashiga tunanin yadda zata raba Sanam da wannan shegen Huneed d'in .....

*Washe gari*

Tuni Sanam tabawa Diyana labarin Mumyn Asokoro ta haihu , Diyana tashiga murna tare da cewa Besty yaushe zamuje barka inga 'yan biyu  ? nasan yaran sun had'u sosai koda bangan su ba , kinsan Allah Sanam inason Mumyn Asokoro saboda tana da mutunci gata me kyau har ta fiki kyau , Sanam cike da jin haushin Diyana tace " sai ki koma gidan ta da zama ki ta kallon ta , tunda kinason ta saboda tana da kyau ko to madallah  sai anjima , kit ta kashe wayar batare da Diyana tayi magana ba , Diyana rik'e da waya a hannu tana mamakin irin tsanar da Sanam tayiwa Mahaifiyar ta ta , wannan wacce irin rayuwa ce ace mutum da uwar sa amman ko zan cen ta bayaso anayi masa ,  ina ma itace tasamu uwa irin Hajiya Maimuna wallahi da duniya sai tasan wace Uwar ta , mata gata me mutunci ga kyau tamkar ita tayi kanta , duk kyan Sanam inta tsaya gaban Hajiya Maimuna wallahi sai ta dusashe ,  tab'e baki Diyana tayi sannan ta furta " duk wannan makirar matar itace tasa kika tsani Mumyn ki Sanam , amman insha Allah watara na zaki so ta kuma zaki k'aunace ta ,  ......

Huneed tunda sukayi waya da Sanam yace " ta shirya k'arfe biyar na yamma zai zo suje barkar ,  tana sama tunda garin Allah ya waye bata sakko ba , ko kayan break a kitchen d'in ta na cikin d'aki ta had'a komai ta karya ,  Hajiya Nafeesa ce ta turo k'ofar d'auke da sallama a bakin ta , Sanam ta amsa mata tare da cewa "Sorry Mumy yau banzo na gaidaki ba keda Daddy ko ? Hajiya Nafeesa tayi murmushi tare da cewa " nasan baki tashi da wuri bane Daddyn ki kuma ya tafi gidan masu jego tun k'arfe goman safe , Sanam taji rashin dad'i yanzu har Daddyn ta yafara fita batare da yagan ta ba ?  wani haushin jariran taji ya kama ta , duk yanayin data shiga Hajiya Nafeesa na kallon ta , kuma dama abinda takeso kenan ace Sanam tafara jin haushin Mahaifin nata ,  shima kuma zata san yadda zata fara tura masa tsanar Sanam d'in

shikenan tayi musu farraqu , lokacin da Alhaji Abba zai fita sai da ya shigo d'akin Sanam yasamu tana bacci , har shafa mata kai yayi yana fad'in " Rigimammiya ta haryanzu bata motsa ba , Hajiya Nafeesar ce cike da kissa tace masa yabar mata 'yar ta tana bacci karya tashe ta , murmushi yayi yafice yana nima bazan so ta tashi yanzu ba kar tashiga yimin rigima , amman yanzu sai ta nunawa Sanam cewa wai d'okin Yaran sa sababbi yake dan haka ya manta da ita , aikuwa tayi nasarar zuga Sanam dan sosai tashiga jin zafin Mahaifin nata tare da Twins d'in da Hajiya Maimuna ta haifa ........

Wajen K'arfe hud'u da rabi Huneed yakira wayar Sanam , d'agawa tayi lokacin tana zaune akan gadon ta tana shan chocolate , dan Sanam akwai shan zak'i tamkar sha zuma ma , d'aga wayar tayi a hankali ta furta Sojana💞 , har cikin jikin sa yaji muryar ta ta tare da jinsa a wani yanayi da yakasa bam ban cewa , cikin kasalalliyar Murya yace " Babyna ina fatan kin shirya dan banajin zan kai har k'arfe biyar d'in nan batare da nayi tozali da idanun ki ba , Sanam cikin murya me sanyi tace " ni dai bazani ba gaskiya dan banason inje inga sunfini kyau , gashi a saboda su yau Daddy ko damuwa baiyi dani ba harya fice baiga lafiya ta ba , kuma haryan zu Daddy bai kirani ba dan haka naji banason ganin su kawai mubarshi , Huneed ji yayi Dariya ta kamasa a hankali ya furta " haba Babyna taya zasu fiki kyau kinsan yadda kike da kyau kuwa ? kwantar da hankalin ki kizo muje mugansu kinga sai kiga kaman nin su , ni ajikina naji basu da wani kyau Babyna tafi su komai da komai , ked'in fa sarauniya ce acikin matan duniya kinga kuwa taya za'afiki kyau , nan Huneed ya shiga lallab'a Sanam da kalamai masu ratsa zuciya , aikuwa yayi nasarar shawo kanta tace zataje bari ta shirya yabata Minty 20 .......

Huneed sosai yayi dariya bayan ya kashe wayar , tabbas ya lura da Sanam k'uriciya nadamun ta , daga haifar yara tafara takun sak'a dasu tabbas yasan akwai me zuga Sanam , wannan kishin datakeyi da Maman yaran gaskiya yayi yawa , murmushi yayi tare da cewa " Zan yi k'ok'arin yadda zanyi naga nasa miki soyayyar k'annen ki koda ba uwa d'aya ce ta haifeku ba .....

Bayan minty 20 tuni Sanam ta shirya cikin wani had'adden less , d'inkin riga da siket ya kamata sosai d'in ki , less d'in kalar pink yaji duwatsu a jiki sosai , ta d'auki blue d'in gyale k'arami ta yafa tare da saka wani blue d'in takalmi me tsini , fesa turarukan ta tashiga yi masu k'amshi da tsadar gaske , tana gamawa ta kira wayar Huneed tana fad'in " Sojana💞 na shirya kai nake jira kawai , Huneed yayi murmushi yace " My angel kifito harabar gidan ku tun d'azu nake jiran sarauniya ta , murmushi tayi tare da kashe wayar sannan ta fito , koda tazo palor bata samu kowa ba haka tafice abinta ....

Tunda ta fito idanun da yake kanta yana yaba tsaruwar datayi , cikin ransa sai kuma hamdala yake ga Allah da samun Sanam cikin Rayuwar sa , tana k'arasowa ta shigo cikin motar tana wani kashe masa ido , shima kashe matan yayi yana fad'in " kinyi kyau sosai My Wifey tamkar kar mufita kinsan banaso ana gane min ke , murmushi tayi cike da shagwab'a tace " to muko ma kawai mu zauna dama nima bason fitar nake ba , dariya yasa yana fad'in " ank'i

wayon  sai munje munga Twins d'in Daddy , tuni yatashi motar me gadi ya bud'e musu gate suka fice.......

Sai da suka biya wani kataferen store Huneed yayiwa jarirai siyayya ,   duk inda suka gilma sai ankallesu saboda had'uwar da sukayi , suna gama siyayyar suka fito Huneed ya mik'awa  Sanam key d'in motar yace " ungo kiyi driving d'in mu nagaji dayawa , batare da musu ba Sanam ta karb'i mukullin tashiga b'angaren wajen driving , taja suka tafi.....

Tafiyar minty 10 ita takawosu Anguwar Asokoro ,  duk wanda ya kwana ya tashi a garin Abuja yasan Anguwar Asokoro unguwa ce ta masu dashi , unguwa ce data amsa sunan ta ta zallar masu kud'i da 'yan siyasa ,  gidaje ne had'add'u da suka tsaru tamkar a turai , Sanam ta shiga Hon. A k'ofar wani katafaren gida ,  dasauri aka wangale mata k'ofar gate d'in gidan me gadi yana musu sannu da zuwa , wajen parking space taje ta paka motar  tana duban Huneed , murmushi yayi mata sannan yace " yayi kyau babbar direba , ashe haka kika iya motar sai kace wata enginer , dariya tayi har dimple dinta ya motsa sannan tace " ai kafini iyawa tunda kai kana jan motar yak'i , Huneed yayi murmushi yace " kema zan koya miki dai kishirya ,  ganin Sanam sai jan shi da hira take tak'i bari su fita daga motar yasa shi cewa " My Wifey yakama ta mu shiga daga ciki ko ,  batace masa komai ba ta bud'e murfin k'ofar motar ta fice abinta , shima fitowa yayi tare da saka me gadi ya d'ebo kayan cikin but d'in motar ya biyosu dashi ......
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 31.

Jerawa Sukayi suka shiga cikin Palor gidan , kana ganin su tamkar miji da mata dan iya dacewa da juna sungama yi , Huneed tunda suka shigo cikin gidan ya raina kansa sosai , duk tsaruwar gidan su Sanam sai yaga ashe bakomai bane wannan shine k'arshen had'uwa , suna saka kansu cikin palor gidan wani k'amshi tare da wani dadda d'an k'amshi ya bugi hancin su , Sanam gawanar son k'amshi tuni ta lumshe ido tana kuma bud'e hanci tana shak'ar k'amshin turaren wutar , tunda takejin turaren wuta masu k'amshi bata tab'a karo da wannan me dad'in k'amshin haka ba..

Sallama sukayi su dukan su dan Huneed k'in yarda yayi ya tsaya a harabar gidan , shi burun sa bai wuce yaga Twins da suka kasance k'annen Bbyn tasa , palor cike yake da 'Yan uwan Hajiya Maimuna suna ta hira abinsu hankali kwance , sallamar da Su Sanam sukayi itace duk ta dakatar dasu daga hirar da sukeyi , tuni kallo ya dawo gun Sanam da Huneed wanda suka tsaya daga bakin k'ofa sukayi turus , Hajiya Maimuna idanu ta zubawa Sanam tana mamakin zuwan ta , dan rabon data ga Sanam a gidan nan har ta manta ma , d'aya daga cikin 'Yan uwan Hajiya Maimuna ce tace musu " sannun ku da zuwa bisimillah ku shigo , Sanam tamkar wacce batason tafiya haka ta taka ta zauna a d'aya daga cikin kujerun palor , Huneed ya durk'usa har k'asa yana gaidasu su duka , amsa masa sukayi cike da sakin fuska sannan ya mik'e shima ya zauna , Mamaki ne ya kama zuciyar Huneed ganin duk matan dasuke cikin palor kusan kamar su d'aya da Sanam , Wacce ya ke kallo kuma yaji ajikin sa itace me jegon tafi kowacce kama da Sanam , dan wallahi badan tana da shekaru ba kuma gata da jiki wallahi si yace Sanam ce , dan kamar tasu ta b'aci sosai . cikin zuciyar sa yake tunanin tabbas akwai abinda Sanam ke b'oye masa , amman wannan kana Ganin ta basai anfad'a maka ba kasan itace wacce ta haifi Sanam , wata ce daga cikin Matan tace " Sanam baki gan mu bane kikayi shuru batare da kin gaida mu ba ? sai sannan Huneed ya tuna da abinda Sanam tayi wato rashin gaida mutanen da tagani , shuru tayi tamkar wacce batasan ana magana ba , Huneed ya dube ta itama shi take kallo yashiga yi mata alama da ido akan ta gaidasu mana , d'auke kai tayi tana turo baki kafin tace " ina yinin ku , amsawa sukayi da lafiya sannan kowacce ta mik'e tana barin palor , Hajiya Maimuna ya rage a ciki itama kuma mik'ewar tayi zata bar palor , da sauri Huneed yace " Mumy ina Twins d'in suke plss , cak ta tsaya tana juyowa ta kallesa tabbas wannan ko waye yana da matsayi me girma a wajen Sanam , kuma ita kanta tunda suka shigo tare ta yaba da nutsuwar sa da kuma kwarjinin sa , a hankali Hajiya Maimun ta furta zan turo akawo maka su yanzu , sai dai dan Allah inaso kar kabawa wannan yarinyar ta kusa da kai yarana , dan shi mak'iyi duk lokacin da zai kusan ce ka to dole akwai mugun abu acikin ransa , tana gama magana ta juya ta bar palor abin ta itama...

sosai maganar Hajiya Maimuna ta ratsa zuciyar Sanam , mik'ewa tayi da sauri tayi hanyar barin palor idanun ta cike da hawaye , da sauri Huneed ya sha gaban ta yana fad'in " ina zakije Sanam ? inaso kidawo ki zauna dan akwai abinda nakeso ki sanar dani game da Mumyn Twins

, meye ya had'a da ita kuke irin wannan rayuwar haka ? sannan jikina yabani Mumyn Twins itace wacce ta haifeki Sanam duba da yadda kuke kama sosai , dan Allah ki taimaka ki cireni acikin duhu wallahi kaina yafara d'aukar zafi , daga Bayana su yaji ana cewa " tabbas Maimuna itace Mahaifiyar Sanam , Itace wacce ta ta raineta tuntana ciki har Allah ya fito da ita duniya , ta shayar da ita na tsawon shekara biyu bata re da ta k'osa ko gajiyawa ba , da sauri Huneed ya jiyo da ganin wacece take magana wata dattijuwa ce fara sol tamkar ita tayi kanta saboda kyau , kamar su d'aya da Sanam har tafi kama da Sanam d'in akan Mumyn Twins , Hannun ta rik'e da kyawawan jariran wad'an da suka sha kayan sanyi ajikin su , Sanam k'urawa Hajiya Babba idanuwa tayi dan tunda take bata tab'a ganin taba , gashi komai nasu iri d'aya dan har tafi kama da ita fiye da Mumyn nata , tabbas wannan ko tantama babu itace ta haifi Mumyn ta , take taji soyayyar dattijuwar me cike da kwarjini da kamala ya kama ta , ido ta zuba mata ko k'iftawa babu tana kallon ta , Hajiya Babba taci gaba da magana " tunda ga randa aka yaye Sanam bata k'ara zama tare da Maimuna ba , Mahaifinta ya d'auke ta yayi wa Matar sa kyautar ta wacce itace sanadiyyar raba Uwa da 'Yar ta , Sanam jin ance Hajiya Nafeesa itace sanadin rabata da Mumyn ta yasa taji haushin Hajiya Babbar ya kamata , take ta bud'e k'ofar palor ta fice abinta rai a b'ace , dan duk duniya batason atab'a Mumyn ta Hajiya Nafeesa wacce takejin ta duk duniya bata da kamar ta , ....

Huneed duban Hajiya Babba yayi cike da girma mawa ya gaida ta , amsawa tayi cike da sakin fuska dan tayaba sosai da hankalin sa , kuma tanaji ajikin ta shine zai kawo wa jikar tata Alkairi a cikin Rayuwar ta , ansar yaran yayi tare dayi musu addu'a ya d'auko wayar sa yayi musu pic , tabbas Daddy yayi gaskiya daya cewa Sanam sunfita kyau sosai gaskiya yaran sun gaji da had'uwa , k'aunar suce tashiga ratsa shi ta ko 'ina yana kallon su , tunowa da Sanam yasa yabawa Hajiya Babba su tare da mik'ewa yana fad'in zai tafi , Hajiya Babba ta dubesa tace " Yaro mungode sosai Allah yayi maka albarka , nasan wannan zuwan da kukayi kai ne ka saka Sanam tazo , hakan ya nuna mana tana sonka kuma kaima kana sonta , dan Allah inaso kayi amfani da soyayar ka da ita ka dai daita tsakanin ta da Mahaifiyar ta , ka kuma dunga nuna mata muhimman cin Mahaifiyar ta dan duk duniya bata da kamar ta , duk da munsan komai datakeyi yasamu nasaba ne daga irin hannun data taso , ilimin addinima ba lallai tana dashi ba dan Maimuna tasha gayamin ita kanta marik'iyar ta ta bata damu da ibada ba , dan Allah yaro ka taimaka ka ceto rayuwar ta daga cikin duhu ka dawo da ita haske , dan ajikina nakejin had'uwar ku da ita alkairine kuma tunda naganka naji kashiga raina , Huneed yace " insha Allah zanyi iya k'ok'arina naga Sanam ta canza halayen ta marasa kyau , kuma kiyiwa Mumy Albishir insha Allah ni Huneed nayi mata Alk'awari Sanam sai tadawo gare ta cike da so da k'auna , wani dad'i Hajiya Babba taji nan danan tashiga saka masa albarka yayi mata sallama yatafi.....

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Inayiwa d'aukacin Masoyana Barka Da Sallah , Dafatan kowa yayi sallah lafiya Allah ya maimaita mana👏🏻_
*Masu k'orafin bana typing dayawa da masu cewa sai na dad'e nake Typing , ina mai baku hak'uri akan hakan duk zangyara amman kudunga yin uziri , sannan duk wani marubuci yanaso yaga ana yi masa Comment duk lokacin da ya turo da book d'in sa , Amman dayawa a cikin ku basayin Comment , dan Allah munaso inkuji dad'in Book kudunga fitowa kuna yabawa Marubutan dan suma suji dad'i ,*

*Nagode Sosai Masoyana* _nima ina k'aunar ku tamkar inzo in sace ku mu rayu tare_😹🥰🥰🤝🏻💔🌹

Chapter 32.

Koda Huneed ya fito daga cikin gidan su Sanam neman ta yayi yarasa , da sauri ya shiga motar ya fice daga cikin gidan....

Hanya ya dunga dubawa ko zai ganta amman harya fita daga estete d'in Anguwar bai ganta ba , haka ya dunga ware ido yana kallon titi ko zai ci karo da ita , can ya hangota a tsaye tana kallon titi ranta duk a b'ace , dayake Unguwar babu masu Napep sosai sai dai in Allah yasa sun shigo da wani , wannan yasa Sanam bata samu abin hawa ba har wannan lokacin ,

yana k'arasowa ya kashe motar tare da fitowa daga ciki , Sanam ganin sa da tayi yasa ta kauda Fuskar ta gefe tamkar bata gansa ba ,...

Murmushi Huneed yayi sannan ya k'araso wajen da take , duban ta yayi yaga idanun ta sunyi ja tamkar ma kuka tayi , da sauri yace " Baby me yafaru dake haka naga idonki yayi ja ? Sanam jitayi tamkar yazo mata da rainin hankali , komai daya faru ai shine ya janyo mata , inda bai takura mata tazo ba taya zasu ganta bare su gaya mata magana , cike da jin zafin sa tace " dama sai da nace maka bazan zoba amman ka takura min nazo , ko kad'an basa k'auna sannan sun tsani Mumyna to meye amfanin inje inda suke , Huneed yayi murmushi sannan ya rik'o hannun ta yace " sud'in sunfi kowa sonki da k'aunar ki , kintab'a ganin uwar da zata durk'usa ta haifi d'a a cikin ta sannan tace bata k'aunar shi ? tamkar k'aramar yarinya haka Sanam ta gyad'a kai alamar a'a , Huneed yaci gaba da magana " To kidaina cewa basa sonki dan dukan su nagano tsantsar soyayyarki a idanun su , kece dai bakya son su tunda naga hakan atare dake , Sanam ta d'an dubesa kad'an sannan ta kauda fuskar ta , har wannan lokacin Huneed na rik'e da hannun Sanam d'in , k'asa yayi da murya sannan yace " inaso Babyna tadaina fushi da Mumyn ta kuma Mahaifiyar ta wacce takawo ta duniya , nasan zaki d'auka cewa Mumy Amarya tafi sonki fiye da Mumyn ki , to ba gaskiya bane dan duk duniya bayan Allah daya halicceki ba wanda ke sonki sai Mumyn Twins , karki manta itace tayi rainon cikin watakila ma bata iya cin komai , a haka har tayi nak'udar ki ta haifeki ta shayar dake har kika kawo wannan matakin , kinga kuwa duk wanda zai nuna miki soyayya bayan ta yake , tunda Huneed yafara magana jikin Sanam yayi sanyi sosai , ganin hakan yasa Huneed yaci gaba da yi mata nasiha tare da nuna mata girman iyaye musamman girman uwa , har suka shiga motar suka tafi yana kuma yi mata nasihar wanda yake da tabbacin tana ratsa Sanam har sassan jikinta.......

Hajiya Nafeesa tunda ta fita gidan Hajiya Harira suke shirya makircin su , har maganar Maryam da yadda suka shirya ita da Fahad sai data gaya mata , Hajiya Harira kuwa taci gaba da ingiza Hajiya Nafeesar akan hakan da sukayi yayi dai dai , sannan ta d'ora da cewa " kinga inkika samu ta haihu ta baki d'an shikenan dama kafin lokacin kin raba Sanam da Alhaji kinsa masa tsanar ta , Hajiya Nafeesa ta tab'e baki sannan tace " ai yanzu ko Alhaji ya daina son Sanam ba muci riba ba , tunda gashi yanzu ta kuma haifo masa wasu , yanzu haka maganar dana ke miki baki ga yadda yake rawar k'afa ba tamkar akansu aka fara masa haihuwa , Hajiya Harira tace " suma dole atashi tsaye akan su dan sonake dukan su ya tsanesu har ita uwar tasu , Hajiya Nafeesa tace " kin manta wannan shegiyar matar batajin asiri , wanne irin boka ne ba muje gunsa ba akan araba ta da gidan amman kina kallo kamar dasa ta ma akeyi , Hajiya Harira tace " kibani lokaci zan samo mafitar yadda za'ayi masu dukan su , haka suka yini suna k'ullah yadda zasu tarwatsa Sanam da Hajiya Maimuna.......

Huneed yaso su biya ta gidan su Sanam ta gaisa da Hajiyar sa , amman ganin duk Sanam d'in bawani walwala take ba yasa ya wuce da ita gida , suna shigowa Harabar gidan suka ci karo Jaydeen a tsaye jikin motar sa yana danna waya , Huneed na kallon sa yaji wani kishi ya kamashi dan ko ba'afada masa ba yasan wajen Sanam yazo , Sanam ta kalli Huneed lokaci d'aya taga ya canza fuska yana kallon wajen da Huneed yake , tamkar tasa dariya haka

taji ganin yadda ya had'e girar sama da k'asa tamkar bashine ke lallab'ata ba , a zuciyar ta tace bari nayi tsokana yanzu , kallon sa tayi tace " My dear ni zan shiga gida sai munyi waya ko , Huneed yadubeta sannan yace " zaki shiga gida ko kuma zakije wajen bak'on ki , to in kingaji da ganina ni bangaji da ganin ki ba kuma bayanzu nakeso ki tafi ba , wani murmushi Sanam tayi najin dad'in yadda Huneed ke san ta , dan tasan so ne kesawa a dunga jin kishin mutum , ta karyar dakai tana duban sa cike da shagwab'a tace " haba My dear daga ganin mutum sai kace bak'o na ne ? kasani ko bak'on Mumy ne ni bani dawani wanda mukayi dashi zai zo , Huneed yace " to koma waye dai bazaki fita ya kallemin mata ba , Jaydeen tunda motar Huneed ta tsaya yaji ajikin sa Sanam na ciki , dan dama me gadi ya sheda masa ta fita ita da wani , kishine ya kamashi tuni ya nufo wajen motar Huneed d'in , b'angaren da Sanam ke ciki ya shiga bugawa , Huneed ransa ya b'aci shima ya bude murfin b'angaren sa ya fito , Duban juna sukayi dukan su sannan Huneed yace " Malam lafiya zaka zo kana bugamin glass d'in motar ? Jaydeen ya kalli Huneed cike da isa yace " wacce take cikin motar nakeson magana da ita Malam bakai ba , Huneed ransa ya sake b'aci yace " meye had'in ka da mata ta dazakayi magana da ita ? Jaydeen yace " matarka kuma ashe har ka aureta batare da sanin iyayen ta ba , inaso kasani Sanam bata dace da namiji irinka ba ka kalleka ka kalli motar da kake hawa , wannan kad'ai ya isheka kasan ita ba sa'ar auren ka bace , Huneed yayi murmushin takaici sannan ya kalli Jaydeen yace " sannu d'an gidan k'aruna rainon biskit da chocolate , inaso kasani tunkafin in canza maka kalar fatar jikinka , Jaydeen ya kalli Huneed yaga lallai inyace zasuyi fad'a to tabbas sai ya doku a gunsa , dan jikin sa ko ina a murd'e yake , amman duk da haka Jaydeen bai karaya ba ya ci gaba da gayawa Huneed magana ....

Tuni Huneed yayi kansa yafara kai masa naushi a fuska , dai dai lokacin hancin motar Hajiya Nafeesa ya sako kai cikin gidan , da sauri ta fito daga motar ko kashe ta bata tsaya yi ba , tana zuwa tafara fad'in " meye hakan zangani kai meyasa baka da hankaline kasan dan waye kake duka haka ? Huneed yanajin abinda tace kuma yasan dashi take , ko waiwayo ta baiyi ba yaci gaba da dukan Jaydeen ,

Sanam tana cikin motar tana kallon duk abinda yake faruwa , sai dai ko ajikinta tunda dama ita bawani k'aunar Jaydeen d'in take ba , dan dama yadameta da yawa ga uban kiran waya ga kuma turo mata test kullum, Marin da Hajiya Nafeesa ta d'auke Huneed dashi shine yasa Sanam katse tunanin ta tana mai bud'e murfin motar ta fito ...........

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION* 📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Wannan Page d'in gaba d'aya sadaukar wane gareki , Aysha Fulani🥰 Happy Anniversary One years, Allah yakaramuku zaman lafiya keda Oga 🙏🏻🙏🏻 Allah yakawo mana yara nagari masu Albarka Ameen👏🏻👏🏻👏🏻🥰🌹💞_

Chapter 33.

Tana k'arasowa ta dubi Hajiya Nafeesa wacce ke uban sababi akan dukan da Huneed yayiwa Jaydeen , Sanam tace " amman Mumy meyasa zaki mari iya Huneed shi wannan sakaran bazaki maresa ba ? duban ta Hajiya Nafeesa tayi baki sake tana mai maita kalmar da Sanam d'in tafad'a , batare da Sanam tadamu da yanayin kallon da Hajiya Nafeesar keyi mata ba taci gaba da magana " Na ruga na zab'i wanda zanyi rayuwa dashi meye zaka dunga damuna , inaso kadaina zuwa wajena domin bazan tab'a saurarka ba , ta kalli Huneed wanda ransa yake a mutuk'ar b'ace tace " dan Allah My Dear kayi hak'uri da Hukuncin Mumy a gareka , Huneed jin abinda Sanam tace masa da kuma irin magan gun datayi yasa yaji zuciyar sa tayi sanyi , yasan ko iya haka ta nuna shine acikin zuciyar ta bawani ba , Huneed yace " Bakomi Baby indai akanki ne komai za'amin zan jure , abinda bazan iya jurewa ba shine wani banza yadunga kallemin ke ko kuma ya furta miki kalmar so , Jaydeen da hancin sa ya fashe da bakin sa tuni ya juya rai a b'ace ya shige motar sa yabar harabar gidan , shima Huneed sallama yayiwa Sanam sannan ya koma ciki motar yaja ya fice daga cikin gidan .....

Sanam ko takan Hajiya Nafeesa bata bi ba tashige cikin gida abinta ........

*Bayan kwana biyu*

Kwata kwata Hajiya Nafeesa ta d'aukewa Sanam wuta , ko hanyar bata bari su had'a ko da yaushe sai wasan b'uya take , in Sanam taje ganin ta sai ta tadda me aikin ta ta shaida mata batajin dad'i , ahaka tagaji da zuwa itama tashiga sabgogin gananta , ....

Soyayyar Huneed da Sanam sai k'ara yawa take , kwata kwata yanzu Huneed nema yake yakasa tafiya aikin sa , koda yaushe suna tare a waya kuma ko yaushe indai zasuyi waya sai ya mata maganar Mumyn twins , yana kuma nuna mata matsayin ta a gunta da kuma cusa mata soyayyar ta , yauma kamar kullum suna cikin waya da ita ya shiga tambayar ta wasu littattafai tasani na addini ? shuru Sanam tayi batare da tace masa kanzil ba , jin hakan ya tabbatar masa ko kad'an Sanam batayi islamiyya ba , murmushi yayi sannan yace " sai nemo mata malamin da zai dunga koya mata karatun alk'ur'ani da wasu littattafan na addini , batare da musu ba Sanam ta yadda dan itama tanaso tasan wasu abubuwan ,.....

Bayan kwana biyu da maganar su Huneed yasamo mata malamin kamar yadda yayi mata alk'awari , a sati zai dunga zuwa sau uku kuma Huneed ya gaya masa sunayen littattafan da zai koyar da ita , tuni Malam yafara zuwa kuma ba laifi Sanam tana bashi had'in kai......

Hajiya Nafeesa da Fahad zaun suna tsara yadda shirin su zai kasance , Maryam wacce itace cikon ta ukun su tuni tasamu ciki wanda bazaka ce ga namijin da yayi mata shi ba , mazan da take bi Ita kanta baza ta tantance ba , tuni Hajiya Nafessa tasa mata 2milloins a account , Maryam sai murna take dan itama zata faso gari kwana nan , Duban Hajiya Nafeesa tayi sannan tace "Hajiya inaso in badamuwa zan dawo gidan nan da zama , Hajiya Nafeesa tace " babu damuwa amman inaso kibari me gidan nan yatafi dan jibi zai bar k'asar nan , kuma zaiyi kamar wata tara ko goma bai dawo ba , dan akwai wani aiki dazaije koyowa , Maryam tace " nagode sosai Allah yanuna mana lokacin , Hajiya Nafeesa ta tashi ta haye sama abinta tabar Fahad da Maryam zaune , suna ganin Hajiya Nafeesa ta mik'e suka matso jikin juna suka fara tab'a juna da shafe shafe , Fahad yace " Babyna kisamun 1m. A account d'ina tunda kinga nine nasamo wannan aikin , Maryam ta d'an turesa tana fad'in " gaskiya bazai yuwuba Dear , kaifa Auntynka ce koda yaushe ka tambaye ta zata baka , nikuwa iya rabona zanci kafin inyi gaba , dan haka kayi hak'uri zan baka 200 Hundrend in sunyi maka , Fahad sosai yaji haushin abinda Maryam d'in tace , sai dai ba yadda zaiyi tunda nema yake kuma shi bawani kud'i Hajiya Nafeesa ke bashi ba , .....

Tunda ga ranar Hajiya Nafeesa ta tsiri cutar k'arya , haka ta k'i zuwa tayi barkar Twins har Akayi suna , koda Alhaji Abba yayi mata magana sai tace bata da lfy yanzu daga ta mik'e jiri take gani , amman da zarar taji sauk'i zata shirya taje taga yaran , ganin lokacin da take maganar ma tana kwance yasa yarda da ita kuma yace dole ta shirya taje taga likita , dama tuni ta biya likitan ta kud'i akan in sunzo ita da Alhaji lallai yace ciki gareta , aikuwa suna zuwa akayi gwaje gwaje likita ya sheda musu tana da ciki , sosai Alhaji Abba ya shiga murna yana mata addu'ar Allah ya sauketa lafiya , bakin sa ko rufuwa bayayi dan murna da baiwar da yake ganin yasamu , haka suka taho gida sai lallab'a ta yakeyi yana wani ririta ta , ita kuwa sai wani langab'ewa take tamkar me cikin gaske , Alhaji Abba yana shigowa palor yafara k'walawa Sanam kira , dan yasan zata fi kowa farin ciki da wannan ciki tunda kullum burinta Mumyn ta ta haifa mata k'anne , Sanam ta sauko daga sama tana fad'in " Daddy lafiya kuwa naji kana k'walamin kira ? Alhaji Abba yace " bani goron Albishir kafin infad'a miki , hannu ya mik'o mata yana murmushi , kallon Hajiya Nafeesa tayi sai wani ya mutsa fuska take ita ala dole me ciki ,

sake duban Mahaifin nata tayi sannan tace " Daddy nidai kafad'amin inji sai nabaka ko me kakeso , Murmushi ya sake yi sannan yace " Mumyn ki zata haifo miki k'ani ko k'anwa nan da 8Month , wani tsalle Sanam ta doka tana matsawa kusa da Hajiya Nafeesa "Mumy dagaske zaki haifo yaro daga cikin ki kema ? Murmushi Hajiya Nafeesa tayi sanna tace " Ea My luv zan haifo miki k'ani me kama dake wanda zaki dunga d'auka kina yawo dashi kema , nan Sanam ta shiga murna sosai , da sauri ta hau sama tana d'aukar wayar ta ta shiga kiran Huneed , yana d'agawa tafara cewa " My Husbee Katayani murna Mumyna tasamu ciki itama , Huneed yayi murmushi sannan yace " congrat My Baby kice dai yanzu zaku k'ara yawa kinzama Babba tunda gashi kina ta samun k'anne , Allah yarabata dashi lfy yasa watarana Albishir zakimin gashi kina d'auke da cikina , Sanam najin haka ta kashe wayar tana mejin kunyar maganar tashi......

Diyana ta kira tashiga gaya mata itama , murna ta taya ta tare da cewa " nace inzakije gidan Mumyn Twins kifad'an amman naji ki shuru , Sanam tace " bantashi zuwa bare in fad'a mikin amman kijira sai randa zani zan miki magana , tana kaiwa nan ta katse wayar tayi jifa da ita tana me fad'awa kan gadon ta .......

Da Alhaji Abba cewa yayi dole sai dai Hajiya Nafeesa ta shirya su tafi tare saboda ya dunga kulawa da ita , amman sam tak'i yarda ta lallab'ashi aka ai nan da wata biyu zata ware taji sauk'i , sannan ta k'ara da cewa zata kira waya can Gidan su a turo mata wata k'anwar ta , da haka ya barta tare da cewa ba lallai yayi wad'an nan watannin ba , nan yatafi yana kewar iyalin sa su duka suma suna kewar sa , musamman Sanam wacce itace ta rakashi air pot har kuka tayi lokacin da jirgin nasu zai tashi ....

Bayan kwana biyu tuni Sanam tafara zuwa Universaty ta abuja dan kammala digree d'in ta , duk kwana uku kuma Malamin Islamiyya nazuwa yana koya mata karatun alkur'ani , sosai tana maida hankalin ta a karatun duka , lokacin Huneed yayi tafiya zuwa Lagos wani aiki , sai dai ko yaushe suna manne da junan su a waya tamkar su janyo junan su , ......

Tuni Hajiya Nafeesa ta ware tadawo yadda take abinta , Maryam ma tuni ta dawo gidan da zama dan haka jin kanta da k'aryar ta sai suka k'aru , tana so ta shigewa Sanam amman ko kad'an ba fuskar daza ta tunkare ta , Koda Sanam taga Maryam a gidan sai Hajiya Nafeesa ta shara mata k'aryar wai 'yar gidan k'anin Mahaifin ta ce , Sanam da yake bata da damuwa da sabgar su shiyasa ko ajikinta.....

Yau takama asabar Su Sanam suna hutu dan haka tana gida abinta tana shan barci , wayar tace tashiga ruri cikin barci ta janyo ta ta danna ta kara a kunne , jin muryar Muradyn ta yasa ta wartsake tafara rikitashi da shagwab'ar ta , aikuwa Huneed ya kuma narkewa harji yake kamar ya bud'e ido yagan sa a gaban Sanam d'in sa , nan ya sheda mata gobe Sunday yana

hanyar dawowa dan shima yakasa komai yanzu in ba zuwa yayi yaganta ba  murna sosai Sanam ta shiga yi tana fad'a masa yadda tayi missing d'in sa , haka sukaita misayar kalamai har suka yi sallama da juna zuwa anjima .....

Tana kashewa ta kira Diyana tace mata lallai ta shiryo yanzu zata raka shopping , dan turarikanta sun kusa k'arewa gashi My Husbee d'in ta zai dawo ,  Diyana tace gatan dan tasan itama zata d'ibi abin datake so .....

Ba'afi minty Goma ba sai ga Diyana lokacin itama Sanam ta shirya cikin shigar ta me kyau sai k'amshi take , tana zuwa suka fito tare suna hira abinsu ,  dai dai wajen da zasu shiga mota Maryam da Fahad suka taho hannu cikin hannu ,  turus Diyana tayi tana kallon su tare da cewa " wanake gani Kamar Maryam Harka ?  Sanam ta kalli Diyana tare da kallon su Maryam d'in , itama Maryam Diyana take kallo duk jikinta na rawa kada asirin su ya tonu...........

[9/27, 10:05] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee* *MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter     34.

Ganin za'a ranfota yasa Fahad yayi saurin zungurar ta , da sauri ta saita kanta tana duban Diyana tare da cewa " Baiwar Allah banganeki ba ni sunana Maryam amman bansan d'aya sunan da kika kira ba ,  Diyana ta dube ta sosai sannan tayi murmushi tace " Haba Harka ko bacci nake naga me kama dake ai saina ganeta bare kuma ido biyu ,  Fahad a k'ufule ya kalli Diyana yana fad'in " ke dallah Malama ki iya bakin ki , wanne irin sunan banza ne haka kike kiranta dashi  tunda tace bata sonki ba ana dole ne ?  aikin banza kawai sai wani shishshigi kike

da cusa kai , sosai maganar ta tab'a zuciyar Sanam , tsawa ta dakawa Fahad d'in tana cewa " to kai ina ruwanka tunda ba kai take tambaya ba ,   juyawa tayi ta kalli Diyana tace "kema gashinan kinjawa kanki  ai , koda yaushe ina gaya miki ki rage cusa kai a irin wannan wajen , tsaki taja sannan ta wuce motar tabar su Fahad baki bud'e  , Diyana itama motar ta nufa tana mamakin yadda Maryam Harka ke neman raina mata wayo...

Sai da suka fita daga harabar gidan sannan ta dubi Sanam wacce har lokacin ranta yake had'e ,  a hankali ta furta " Besty wannan Maryam d'in kodai 'yar uwar kuce ?  nifah abin mamaki yake bani ganin yadda ta raina min wayo ,  Sanam tana tuk'in Motar ta kalli Diyana tace " to ke a inah kika santa ?  Diyana tace " wallahi A k'asan Unguwar mu take , duk cikin fad'in Unguwar nan bawanda bai san Maryam Harka ba , amman k'iri k'iri tana neman ta maidani wata bugun shaho , Murmushi Sanam tayi sannan tace "   Maganin ki ai tunda kin iya saka ido ai dole ayi miki haka , dama basu rufeki da duka ba kuma kinsan ba kwatar ki zanyi ba ,  Diyana tace hmm " nifah dole sai nabi duddugin abinda yakawo Harka gidan ku , dan duk inda taje to tabbas ba Alkairi akwai wani k'ullin ak'asa ,  Murmushi Sanam tayi sannan tace " aiki ne yasameki wallahi ,  Ni Mumy cemin tayi 'yar kanin Baban tace  , kinsan bawani sanin Family d'in ta nayi ba , tunda duk rabin su suna can Borno state  acan suke da zama ,  tunda tazo gidan naga take taken ta tanaso tasamu fuska a gurina nikuma tuni ba fara had'e girar sama da k'asa ,  dan kwata kwata banji ko kad'an zan bata fuska ba , Diyana ci gaba tayi da Maimaita kalmar 'Yar K'anin Baban ta ,  to itadai tun tasowar ta a layin su bata tab'ajin su Maryam harka suna da 'Yan uwa masu kud'i ba ,

Asalima Baban ta harya mutu sana'ar sa Baduku ne , ko zaman makoki ba'ayi masa ba saboda basu da halin yin abincin masu zaman makoki ,  itace take fita yawonta tasamo musu abinda zasuci ita da Maman ta da k'annen ta ,  Sanam jin Diyana tayi shuru yasa ta kalleta tace " ko kinfara bin diddigin ne tun yanzu ? murmushi tayi suka ci gaba da hirar su , sai dai Diyana ta k'udurta aranta tabbas sai tagano me Maryam tazo yi gidan su Sanam......

Bayan fitar su Sanam Maryam ta dubi Fahad tace " akwai matsala sosai fa , Fahad yace wacce irin matsala kenan ? wallahi wannan k'awar Sanam d'in da kagani unguwar mu d'aya da ita ,  tasanni farin sani   gata da iya saka ido tamkar 'yar jarida ,  Fahad yace " karki damu bari muje muyi magana da Aunty intaka ma a hanata shigowa gidan nan sai a hanata ,  sai sannan Maryam tasaki ajiyar zuciya suka shige cikin gidan.......

Huneed tunda sukaje gidan Mumyn Twins wato Mahaifiyar Sanam , sai da ya koma sau biyu gidan gar number ta garesa , har waya suke da Mumyn yana kwantar mata da hankalin ta , anan ya kuma jin halin Hajiya Nafeesa da yadda ta lalata Sanam tuntana k'arama bata ganin Mutuncin kowa sai nata ,  kuma itace ta rok'eshi Alfarma akan tanason Sanam tasamu ilimin addini ko yaya ne , dan har da rashin ilimi yana d'awainiya da ita , haka Huneed ya shiga kyautatawa Mumyn Sanam duk da yasan babu abinda suka nema suka rasa , amman duk k'arfin mutum kuma duk kud'in sa yana mutuk'ar son yaga ana kyauta ta masa ,  kuma koda wasa bai tab'a gayawa Sanam ba bare ya nuna mata a fuska.......

Babban wajen Shopping Sanam sukaje ita da Diyana , sosai ta d'ibi kaya da turaruka manya tare da sabulai masu tsada , Diyana itama Sanam tace mata ta d'auki duk abinda takeso , haka ta zage ta d'ibi kayan kwalliya da turaruka itama , sai dogayen riguna had'add'u wanda ta d'aukar musu kala biyu ita da Sanam iri d'aya , suna cikin zagaye a wajen suka ci karo da Jaydeen yana tsaye yana duban su , wani tsaki Sanam tayi tare da k'ok'arin canza hanya , da sauri Jaydeen yasha gaban ta yana fad'in " plss ko Minty 5 kibani inason magana dake , Sanam ta galla masa harara tana fad'in " Malam dan Allah kabani waje ina da abubuwan yi , Jaydeen yayi murmushi yace mata " Sanam inasonki sosai araina kuma tunda nake ban tab'a son Abu ban samu ba , kamar yadda Mumyn ki tace mun in kwantar da hankalina tamkar nasameki ne , to kisani kafin Daddyn ki yabar k'asar nan sai da Daddyna yaje sukayi magana dashi , kuma shima Daddyn ki ya tabbatar wa da Daddyna cewar yana dawowa zai d'auramin aure dake , wani kallo Sanam tayi masa wanda yake nuni da baka da hankali , magana yaci gaba dayi yana fad'in " inaso inja kunnen ki akan wannan matsiyacin saurayin naki , daga yau sai yau karki k'ara binsa ko inah dan bazan jure ganin yanamin yawo da Mata a titi ba , wani takaicine ya kama Sanam takasa magana , tsaki tayi kawai ta wuce batare da ta kuma bi takan sa ba ,....

Suna k'arasawa gun biyan kud'i akace musu anbiya musu , Sanam cike da fad'a ta kalli wanda yace anbiya musun tace " to ce muku akayi bani da kud'in da zanbiya ne ? Malam inaso kubashi kud'in sa kufad'amin nawa zanbiya , wani daga ciki yace " haba Hajiya ai ba'a maida hannun kyauta baya , wata harara ta watsa masa sannan tace " to ni na maida sai ayimin hukunci , Diyana ce takamo hannun ta suka fito daga wajen dan inba haka ba yanzu zasuyi b'atacciya ,.......

Fahad shida Maryam tuni suka shedawa Hajiya Nafeesa maganar Diyana , Hajiya Nafeesa tashiga zage zage " nifah wallahi tuntuni na tsani yarinyar nan dama , kowanne aiki intayiwa Sanam ita take rusashi , lallai lokaci yayi da zatayi maganin ta dan wannan karon a shirye take da tayi komai dan burin ta ya cika , take ta shiga shirya yadda zata yi maganin Diyana ta shirin Had'ata fad'a da Sanam.....

Har suka baro wajen Shopping Sanam na ruwan jaraba , babu abinda yafi tsaya mata arai sama da maganar da yace Daddyn ta da nasa sunyi , yaushe wannan abun yafaru batasani ba ? dama taga take taken Mumy bason Huneed take ba , tasan tunda Jaydeen ya kasance d'an gidan k'awar ta dole zata bi duk yadda za'ayi ta cusa mata shi , itakuma wallahi ko ba'abata Huneed ba babu abinda zatayi da Jaydeen , ko maza sun k'are a duniya da ta xauna dashi wanda ta mutu babu aure , Diyana dai babu bakin magana , dan tamkar Sanam zatayi aljanu haka tashiga yi tana zage zage , addu'a Diyana tashiga yi akan Allah yakaisu gida lafiya dan yadda take tuk'in motar ma tashin hankaline , a haka Allah yakawosu gida lafiya tashiga dannan Hon. me rikitar wa , me gadi tamkar zai kifa haka yayi sauri ya nufi gate d'in yana bud'ewa , yana gama bud'ewa motar tana danno kai da mugun gudu cikin gidan , wani uban

tsalle me gadi yayi dan karta take masa k'afa , bin motar yayi da kallo ya tabbatar da lallai yau antab'o 'Yar gwal , tana fita daga motar ta nufi cikin gida kai tsaye tana k'walawa Hajiya Nafeesa kira " Mumy Mumy kina ina inason magana dake , da Hajiya Nafeesa da Fahad da Maryam duk mik'ewa sukayi jikin su na rawa jin irin kiran da Sanam kewa Hajiya Nafeesar , tuni suka shiga jin tsoron kodai Diyana ta je ta nemo labarin abinda yakawo Maryam cikin gidan ? In kuwa hakane to tabbas sai tayi magani Diyana a yau basai gobe ba , Sanam tana shigowa palor tabi su da kallo sannan tace " Mumy inaso kijawa wannan 'Dan gidan k'awartaki kunne wallahi yafita daga sabga ta tunkafin insa ayimin maganin sa , wata ajiyar zuciya Hajiya Nafeesa tasaki tare da hamdala a zuci , Cike da kissa da nuna kulawa tace " wanne d'an k'awar tawa kenan ? Sanam tace " wannan kalar 'Yan daudun dan banason sa ko kad'an ya fita daga sabga ta , tana gama fad'ar haka ta haye sama tabarsu baki bud'e , Hajiya Nafeesa taja tsaki sannan tace" aikin banza kalar d'an daudun kuma shine mijin ki , dan duk yadda zanyi yazama mijinki sainayi banza wawiya , Fahad yasa murmushi yana kallon Hajiya Nafeesar sannan yace "Aunty ai batasan kinayiba dama binta kikayi kika fad'a mata , wata harara ta galla masa sannan sukasa dariya su dukan su , dai dai lokacin Diyana tashigo cikin palor idanun ta akan su , aikuwa su duka suka canza fuska tamkar basu suke wannan dariyar ba , Diyana ta kalli Mumy ta rissina tana fad'in " barka da yamma Mumy , Hajiya Nafeesa tayi tsaki sannan tace " barka shugabar munafukai , Diyana tamkar bataji ba tashige abinta batare da tabi takansu ba , ....

Hajiya Nafeesa tace " inaso asan yadda za'ayi a had'a Sanam fad'a da wannan shegiyar yarinyar , Maryam tace " wannan shirin kibarmin shi a hannuna dan nafi kowa son naga sunyi fad'an da baza ta kuma takowa gidan nan ba , kawai inason inga saurayin da Sanam tafi so dan ta dalilinsa zamu saka su yin fad'a , nan suka saka wata shewar murna dan shima shegen dama so suke yadaina zuwa , dan tun sanda yakawo mata malamin dazai dunga koya mata karatun Hajiya Nafeesa takuma tsanar sa , kuma sosai taga canji yanzu a tare da Sanam , komai inzatayi yanzu tadaina gaya mata sab'anin da , tabbas zataso ace sun rabu dan komai zai fi mata sauk'i........

*Kumin Afuwa Zazzab'i nadamuna😔😕*
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 35.

Koda Diyana ta hau sama ta samu Sanam cike da nutsuwa tace " dan Allah Besty kirage saurin zuciya , wannan halayyar bata dace dake ba , Sai sannan Sanam ta sai ta kanta tafara magana "Diyana inason Huneed fiye da tunanin ki banason duk abinda zai zame mana barazana a cikin soyayyar mu , kinajin abinda Guy d'in nan yafad'a wai Daddyna danasa sunyi magana , duk da nasan Daddyna bazai tab'amin auren dole ba , amman naga kamar Mummy tafison wannan Jaydeen d'in akan Huneed , Diyana ta mik'e ta k'arasa kusa da Sanam sosai tace " ki kwantar da Hankalin ki Besty tunda har kinsan Daddyn ki bazai aura miki wanda bakyaso ba , kawai dai shawarar da zan baki shine kiyi magana da Huneed akan yasami Daddyn ki da maganar auren ki , Sosai Sanam taji dad'in abinda Diyana tace mata , dama Huneed tuntuni yake damun ta da Maganar yanaso yaturo , itace take ce masa yabari tayi nisa a karatu sai ya turo ayi magana , amman tunda abun yana neman zame mata tashin hankali dole tayi masa magana, da haka suka shiga hirar su wacce duk rabi akan soyayyar ta da Huneed ne......

*Washe gari*

Tunda Sanam ta tashi take shirin tarar Huneed , bawani girki ta iya ba bare tace zata shiga kitchen da kanta tayi masa , sai dai kawai tasa angyara d'akin saukar bak'i sannan aka turaresa da turaruka masu dad'in k'amshi , shiga kitchen tayi tasamu me yi musu aiki tace tana so tayi mata girki na musamman tana da bak'o , Alawiya cike da girmamawa tace " ranki ya dad'e me da me kike so a dafa masa ? Sanam tayi shuru na wasu Mintyna tana nazarin me Huneed yafiso , can ta tuna wani lokaci suna hira yake tambayar ta wai ta iya Dambun Shinkafa yaji gyada da zogale , a lokacin tayi wani murmushi tace masa ta iya indai so yake , nan ta kalli Alawiyya tace inaso kimin Dambun shinkafa yaji zogale da gyad'a , sannan sai kiyi min farfesun Kayan ciki , ki d'ebi naman kaji ki soya sai ki yi masa kunun Aya , Alawiya cike da girma mawa tace " angama ranki ya dad'e Sanam ta fita daga kitchen ta nufi d'akin ta.....

Tunda Huneed ya sauka a Abuja yakejin sa cikin wani farin ciki , Hisham ne ya d'aukosa a mota sai hira suke abin su , suna k'arasowa gida Hajiyar su ta taresa cike da farin ciki da so da k'auna , 'Dakin sa ya nufa dan yarage kayan jikin sa yayi wanka , yana fitowa kiran wayar Sanam na shigowa wayar sa , Murmushi yayi sannn ya d'aga yana fad'in " My Wifey sai yanzu kika tuna da mijin naki ? Murmushi Sanam tayi sannan tace " dama koda yaushe ina tunanin sa araina , ina fatan My Husbee na ya dawo lafiya ? Huneed yace " waye yafad'a miki nadawo ? Murmushi tayi sannan tace " a jikina naji cewar Masoyina yana kusa dani , sannan in nasaita Nunfashina tasaitin gidan ku inajin bugun zuciya ta yana k'ara yin yawa , hakan ya tabbatar mun da cewa Sojana yana cikin garin Abuja , Wani dad'ine yakama Huneed yayi murmushi yana lumshe idanu sannan cikin wata kasalalliyar Murya yace " tabbas Matata batayi k'arya ba , yanzu haka ina cikin gidan mu a d'akin ina shirin tahowa inga Matata , Sanam tamkar tayi tsalle saboda murna kawai murmushi take baki yak'i rufuwa , ahaka wayar ta katse tuni tafad'a toilet danyin wanka.....

K'arfe biyar dai dai Huneed ya iso gidan su Sanam , tunda yashigo masu aikin gidan suke girmama shi , indai Huneed yazo to suma ranar sai sunsamu rabon su , dan hannuwan sa a bud'e yake akwai shi da kyauta , dan haka kowa keson zuwan sa kuma suke girma mashi ......

Sanam tuni ta shirya cikin wani Material me tsadar gaske , d'in riga da siket sun zauna a jikinta das , sabon takalmi kalar jikin adon less d'in tasa tasa kuma mayafi kalar takalmin , fad'in irin kyan da Sanam tayi b'ata lokacine , inbanda K'amshi babu abinda ke tashi ajikinta , tuni Huneed ya sheda mata zuwan sa , nan tace masa ya shiga d'akin saukar bak'i gatanan zuwa.......

Sai da akayi kusan minty 5 sannan Sanam ta sakko cikin takunta na isa , tana gama sakkowa tasamu bakowa a palor sai Maryam , Maryam tana ganin Sanam ta zuba mata idanu , turaren da Sanam ta fesa Maryam na shak'ar sa taji Amai ya taso mata , da gudu ta nufi toilet d'in dake cikin palor tana kakarin Amai , Sanam tuni ranta yayi mugun b'aci me wannan 'Yar iskar take nufi da har zata hau Amai dan taganta ? kamar ta je gurin Maryam amman sai tafasa ta fita daga cikin palor , sai dai tabbas indai Huneed yatafi dole zata sameta taji dalilin ta nayi mata hakan , duk b'acin da ranta yayi tana tozali da Huneed taji duk yatafi , murmushi yakar mata itama ta maida masa da nata Murmushin , Huneed ji yayi kamar yatashi ya rungumeta amman yasan hakan bazai yuwu yanzu ba , zama tayi kusa dashi tana fad'in " sannu da zuwa My Sojana, Huneed ya rik'o Hannun ta yana fad'in " Matar Soja itama Sojan ce My Wifey irin wannan kyau haka ? tamkar an canzamin ke komai naki yakuma k'arayin kyau , nan yashiga yabon kyan datayi da fad'in dole yasiyi wannan kwalliya , wayar sa ya d'auko yashiga d'aukar ta pic , duk yadda ta motsa sai yayi mata kuma ko wanne yayi sai tayi kyau , sai da yagama yi mata sannan ya matso kusa da ita yayi musu tare batare da ta kulaba , tana gani tayi saurin rufe fuska tana murmushi , nan suka shiga hirar su wacce rabin ta akan yadda sukayi Missing d'in juna , anan Huneed yashiga shedawa Sanam anyi masa k'arin girma nan da kwana biyu za'ayi bikin karramashi , Murna Sanam tashiga yi tana godiya ga Allah , tuni ta bud'e masa Abincin datasa akayi masa tafara seving d'insa.....

Bayan Sallar Magriba Huneed yace ta tashi suje wata Unguwa su dawo , batare da musu ba ko tambayar inda zasu Sanam ta mik'e suka jera har jikin Motar , suna zuwa suka shiga sannan suka fice daga cikin gidan.....

Sun shagaltu da hira shiyasa Sanam bata fahimci inda suka nufa ba , sai da suka shiga cikin Estate d'in sannan tagane Gidan Mummyn Twins zasuje , kallon Huneed tayi yasakar mata murmushi sannan yace " Mummy tanason ganin kyakkyawar 'Yar ta , Sanam ta turo baki tana fad'in "Haka tace maka kenan kawai dai kanaso kadatsemin farin cikin danakeyi yau , tsayawa yayi dai dai k'ofar gate d'in gidan yana hon. Sannan yace mata " kintab'a ganin Uwar dazata datsewa 'Yar ta farin ciki ? Sanam ta yi shuru bata bashi amsa ba , kuma dai dai lokacin Megadin gidan ya bud'e musu gate , Huneed yace "to kidaina cewa haka dan duk wata Uwa da kike gani tafison Farin cikin 'Yayan ta fiye ma danata farin cikin , haka suka fito daga cikin Motar ya rik'o mata hannu suka nufi cikin Palor gidan .....

Koda shigar su wani k'amshin turaren wuta ne yadaki Hancin su , Sai kuma sukayi ido biyu da Hajiya Maimuna tana zaune tana bawa Twins d'in ta nono , sallama sukayi mata a tare Sanam tamkar wacce k'wai yafashewa a cikin ciki take tafiya har ta isa kan kujera ta zauna , shima Huneed xama yayi sannan yashiga gaida Mummyn cikin girmamawa , ga Mamakin Sanam sai taga Mummyn nata ta amsa masa cike da sakin fuska dakuma nuna so da k'auna , harji tayi tana tambayar sa ya Hajiyar sa da kuma Hisham , bayan ya amsa mata da duk lafiya suke sannan takumaji tace masa " ya hanya dafatan kadawo lafiya , ina tayaka murnar samun k'arin girman dakayi , Allah yatsareka yakuma kareka a duk inda kake , Sanam tamkar mutum mutumi tazama agun , dan abun yabata mamaki sosai cikin ranta tashiga tambayar " Yaushe Huneed da Mummy suka san juna haka ? Duk tayaya tasan yayi tafiya harda k'arin girman da yasamu ? bamai amsa mata wanannan tambayoyin sai Huneed , wasan da Huneed yake da Twins d'in shiya dawo da ita daga tunanin datakeyi.........
[9/27, 10:06] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 36.

A hankali Sanam tacewa Hajiya Maimuna " Mummy ina yini , sosai Hajiya Maimuna taji abun kamar almara yau ita Sanam ta kira da sunan Mummy ? wani dad'i taji har cikin ranta tare da sakawa Huneed albarka dan tasan shine yabata wannan tarbiyar , amsawa tayi tare da cewa " lafiya k'alau muke dafatan kuma kuna nan lafiya keda Mummyn taki ? Sanam tace lafiya lau , Mummyn Twins kallon Huneed tayi tana me jinjina masa ta sigar lumshe idanuwa , murmushi Huneed yayi sannan yacewa Sanam " Aunty Sanam ga Twins suna mik'o gaisuwa , kunya ce ta kama Sanam ganin ko k'annan nata bata tab'a gani ba , da sauri ta matsa ta anshe macen wacce suke ce mata Amrah , tsayawa tayi tana kallon ta sai taga kamar su d'aya ita da Amrah , har dimple d'in da take dashi itama Amrah tana wangale mata baki taga ya lotsa , wata iriyar k'aunar 'Yar k'anwar ta ta taji ta kama ta , sumbatar ta tashiga yi tare da yi mata wasa , cike da so da K'auna Hajiya Maimuna ke duban Sanam d'in , cikin zuciyar ta tana fad'in " dama ace zasu dauwama a haka batare da Sanam tayi nisa dasu ba , ta shagala da kallon Sanam d'in wacce ta ware take ta wasa da Amrah har da mata wak'a , shima Huneed d'in kallon ta yake cike da jin dad'in yadda Sanam ta bashi had'in kai wajen faran ta ran Mummyn nata , wayar ta ta d'auko a jaka tashiga d'aukar Amrah video tana mata wasa , Hajiya Maimuna tana ganin haka ta tashi ta nufi sama dan ta d'an basu waje , bakin ta har kunne sai saka wa Huneed albarka takeyi ,...

Aikuwa tamkar jira Huneed yake ta tashi ya matso kusa da Sanam shima yafara d'aukar su a waya , Namijin shi kuma ana kiran sa da Ameeer , tuni Sanam ta ajiye Amrah tana fad'in " My Sojana bani Ameeer d'in shima , mik'a mata shi yayi tashiga kallon sa shima , sosai yafisu kyau ita da Amrah dan yaron ya had'u , bai kaisu haske ba amma kyansa abin kallo ne ya had'u , Sanam ta had'asu duka ta rumgume tana cewa yimana pic in d'ora a social media nima aga k'anne na , murmushi yayi yana duban ta sannan yace " ai baza a yadda k'annan ki bane , duban sa tayi da alamar tambaya ? ea mana ai sai dai ace 'Ya'yanki ne tunda ai kin isa haifar su , dariya tasa tana duban su Suma tamkar sunji me akace suka fara wangale mata baki , tuni Huneed ya shagala da kallon su yafara musu video , bayan kamar minty 20 Hajiya Maimuna tadawo hannun ta d'auke da tire , dambun naman kaji ne aciki tazo ta ajiye musu , ta kalli Sanam tace " in kuna buk'atar wani abun ki shiga kitchen ki dafa muku , ni yau tuwon semo nayi miyar yauk'i kuma nasan ba lallai kuci ba , Sanam tace " a k'oshe muke Mummy dambun

naman ma ya isa , dama Mummy tasan Sanam din tana son damun nama , dan wani lokacin tanaji in suna waya da Daddyn ta zatace ya siyomata dambun nama , duk abinda Sanam ke so Hajiya Maimuna tagama sanin shi , tuni tafara cin dambun naman hannu baka hannu k'warya.....

Huneed duban ta yayi yana dariya yana fad'in " ci a hankali mana Madam , murmushi tayi sannan a hankali tace masa " bantab'a cin dambun nama me dad'in wannan ba shiyasa , sai wajen k'arfe goma suka bar gidan Mummyn Twins , Sanam cike da kewar Twins itama Hajiya Maimuna cike da kewar Sanam d'in .....

Hajiya Maimuna bayan ta dawo daga raka su Sanan jikin mota tad'au waya tashiga kiran Hajiyar ta , tana d'agawa tashiga bata labarin zuwan su Sanan d'in da komai da komai daya faru , Hajiya tashiga hamdala tare da cewa " lallai wannan yaron d'an Albarka ne , kuma shine wanda ya cancan ta yazama miji agare ta , nidama tun farkon ganina dashi naji ya kwantamin arai , ashe shine sanadin da zai dawo miki da farin cikin ki har gida , inaso kici gaba da addu'a tare da janyo yarinyar ki jikin ki a hankali , duk abinda kikasan tanason shi to ki dunga aika mata da shi da haka zaki jawota jikin ki , sosai Hajiya Maimuna tayi na'am da shawarwarin Hajiyar tata , nan sukayi sallama tana saka mata albarka.....

Sanam tun da suka taho baki yak'i rufuwa sai murmushi take , duban ta Huneed yayi sannan yace " Madam gaskiya indai mukayi aure kifara haifo mana Twins masu kama da su Amrah , Sanam tayi murmushi sannan tace " tamkar in dauwama ina tare dasu nakeji , gaskiya yaran sun shiga raina mutuk'a My Sojana , wlh da Mummy zata bani su tas zanyi mata rainon su , Murmushin dad'i Huneed yaji a zuciyar sa yace " anzo gurin , a fili kuma yace " taya Mummy zata baki su ko kin manta k'ananu ne basu isa abada su ba , in rainon su kikeso me zai hana bazaki dawo gidan Mummyn Twins d'in da zama ba , Sanam ta kalli Huneed sannan tayi shuru na wasu lokutan kafin tace " ai Mummy bazata bari nadawo ba , kasan ba shiri take da Mummyn Twins ba shiyasa , Huneed yace " in dai kinason rainon su kawai ki shirya ki koma gidan su , in kuma bazaki koma ba to kidunga zuwa kina musu kwana biyu biyu , ahaka zasu shak'u dake har sudunga ganeki inkinje , Nan Huneed yashiga yiwa Sanam dabara tare da cusa mata ra'ayin zuwa gidan Mahaifiyar ta ......

Tuni Sanam tasa pic d'in su ita da Twins ta rungumo su tana dariya , wasu tasa a status sai kuma ta zab'i guda d'aya wanda sukayi da Huneed da Twins d'in duka sunyi kyau ta d'ora a dp....

Hajiya Nafeesa tana chat da k'awayen ta manyan mata taga Sanam tayi status , mamakine ya kamata dan a iya sanin ta Sanam batayin Status , sannan pic d'in dake Dp ta yafi shekara uku tak'i canza shi , sai gashi yau taga tayi status tare da canza Dp , da sauri tashiga Status tafara dubawa k'irjin tane ya buga ganin Sanam rungume da k'annen ta a palor gidan su tana dariya , duk pic d'in data saka bawanda basuyi kyau ba ita da Twins d'in , tana duba dp nan ma sai da gaban ta ya fad'i , yaushe Sanam tafara son Mahaifiyar ta ? yaushe Sanam tafara zuwa inda Uwar ta take ? tasan ba wanda ya had'a wannan munafincin sai wannan

shegen Huneed d'in , tabbas lokaci yayi dazatayi gaba da gaba dashi akan ya fita daga sabgar Sanam ,. Wani huci take tana kuma yin zoom d'in pic din tana gani , wato Hajiya Maimuna tana k'ok'arin yin nasara akan ta , to wallahi bazata sab'u ba dole takoma wajen bokan ta ayo musu farraqu me zafi........

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 37.

Farin cikin dake d'auke a fuskar Sanam tamkar wacce aka yiwa tukuci da Aljannah , d'auke da murmushi a fuskar ta tadubi Huneed tace " My Hero bani da kalmar da zan furta maka wajen godiya , sai dai zanyi maka addu'ar Allah yabiya maka buk'atun ka na Alkairi , tabbas zuwana gidan mu yanzu yasa na fahimci lallai akwai Alaqa me k'arfi tsakanin ka da Mummy Twins , komai naka tasani hakan ya nuna min kazama d'an gida sosai da sosai , tunda na taso yaune karon farko da nafara ganin farin ciki d'auke a fuskar Mummy , Abinda yaban mamaki ko fad'an data saba yimin yau naga bayayi ba , lallai naji dad'in wannan yanayin kuma indai hakane daga yau zan dunga kawo mata ziyara kodan inga K'annena , Huneed cike da jin dad'i yace " ai dama Mummy Twins bata da laifin komai Bby , kece bakya zuwa ki gaida ta shiyasa takejin rashin dad'i , suna tafe suna hira wacce duk akan maganar zuwa gidan Hajiya Maimuna ce har suka k'araso gida......

Suna shigowa harabar gidan basu dad'e ba Huneed yayi mata sallama yatafi......

Sanam sai da taga fitar sa daga cikin gidan sannan ta juya ta nufi ciki , tana shigowa cikin palor tasamu Fahad da Maryam suna ta wasan banza , had'e fuskar ta tayi dan ta tsani wannan k'azamar rayuwar da sukeyi , zata wuce kenan Maryam ta mik'e da gudu tana kakarin Amai a karo na biyu , aikuwa Sanam ranta ya kuma b'aci dama d'azu da zata fita tayi mata haka wato shine yanzu ma zata kuma yi mata , to wallahi ko waye uban ta yau saita bar musu gida , a fusace Sanam tabi bayan Maryam har wajen k'ofar toilet , Maryam na fitowa tayi karo da Sanam ba wata wata Sanam ta shak'i wuyan Maryam d'in , cikin tsananin b'acin rai Sanam tace " meye a jikina da kike rainawa kan ki hankali in kika ganni ? d'azu da zan fita kinyi min haka yanzu ma kuma da nadawo sai ki kuma yimin , Maryam sosai taji shak'ar da tayi mata dan ko magana ta kasayi , gashi turaren sai kuma dukan hancin nata yake wani Aman na sake taso mata , Fahad ne ya k'araso da gudu dan ya kwaci Maryam , sai dai koda yazo Sanam bata cika ta ba sai marin fuskar ta take tana fad'in " wallahi sai kin fad'amin abinda kikewa Amai a jikina , Fahad yacewa Sanam " dallah cikata dan kinga tazo gidan ku shine kikeson tozar ta ta , Sanam da wani mugun kallo ta bishi sannan taci gaba da tambayar Maryam akan lallai sai tafad'a mata me tagani ajikin ta da take amai , hayaniya tayi yawa har Hajiya Nafeesa taji ta sauko , koda tazo da k'yar ta kwaci Maryam daga hannun Sanam , Maryam ana kwatar ta takuma shiga toilet da gudu tana shara amai , Hajiya Nafeesa ta kalli Fahad tace " meye ya had'asu haka ? Sanam ta ja tsaki tare da barin gurin dan bata da abin fad'awa Mummy ........

Fahad yabita da harara tare da kallon Hajiya Nafeesa yace " a gaskiya wannan yarinyar bata da mutunci , kawai dan Marry ta nufi toilet tana amai shine ta nufo ta tahau duka wai da ita take , Hajiya Nafeesa ta dubesa tace " tabbas akwai abinda Sanam take shirin yi , dan nima yanzu tagama bani mamaki wai itace yau harda zuwa gidan Uwar ta , yanzu nake shirin sakkowa na fad'a maka har status tayi ita da Twins d'in su , Fahad yace " tabb lallai kina Ruwa Aunty kina nufin kicemin Yanzu Sanam tafara son Mahaifiyarta kenan ? Hajiya Nafeesa tace " ga alama nafara gani kuwa , ba wanda yake had'a wannan muna funcin kamar shegen yaron nan , Fahad yace" kawai kibamu aiki akan sa wallahi zamu rabasu nida Maryam , fitowar Maryam daga Toilet yasa dukan su suka fara duban ta , Hajiya Nafeesa tace mata " sannu kinji kiyi hak'uri da abinda tayi miki , Maryam tace " babu komai Hajiya koni ce abinda zanyi kenan , kuma wallahi turaren data sane bayamin dad'i , inajin sa sai naji Amai yatahomin shiyasa , Hajiya Nafeesa tace " cikin jikin kine bayaso tunda kinga masu ciki sunajin irin hakan , abinda nakeso dake kawai kidaina zama a palor gudun irin haka , kuma indai kina yin haka to lallai shirin mu zai lalace , dan Sanam tana da hankali dole zata gano akwai wani abu a k'asa , Maryam tace " zankiya ye dama ba sosai muke had'uwa da ita ba , Dawowa cikin palor suka zauna sannan Hajiya Nafeesa ta dubesu tace " Maryam inaso kiyimin wani aiki , Maryam ta dube ta sannan tace " fad'i ko wanne irin aiki kikeso zanyi miki , Hajiya Nafeesa tace " tunda kinsan wannan k'awar Sanam d'in inaso kiyi min aiki akansu , zan samo number Huneed da ita Diyana a wayar Sanam zaki had'amun su , Maryam ta dubi Hajiya Nafeesa tace " ki fahimtar dani ban gane me kike nufi ba ? Hajiya Nafeesa tace " inaso Kisan yadda za'ayi Huneed yaje k'ofar gidan su Diyana , sannan itama Diyana ta fito wajen sa ayi musu hotuna a turawa Sanam yadda zamu saka mata tsanar su , nasan wace ce Sanam akan kishi mutuk'ar taga wannan pic d'in zata d'auka gaske ne , Maryam tayi wani shu'umin Murmushi tace " ki kwantar da hankalin ki wannan aikin ai me sauk'ine kisa aranki kamar anyi angama , murmushi Hajiya Nafeesa tayi

sannan tace " yau Jarumata shiyasa nake yinki saboda kaifin basirar ki , Fahad yace " shiyasa kika ga na zab'o ta akan tayi mana wannan aiki dan ita kad'ai ce zata iya , nan wayar Hajiya Nafeesa tashiga k'ara ta mik'e tana barin gurin dan tayi waya da Alhaji Abba , .......

Sanam tana hawa sama toilet ta fad'a tayi wanka sannan b'acin ran nata yaragu , amman cikin ranta ta shirya ciwa Maryam mutuncin da har sai tabar musu gida , kayan baccin ta tasa ta haye gado tana me d'aukar wayar ta ,......

Hajiya Nafeesa tana d'aga waya tafara yiwa Alhaji Abba shagwab'a , tuni ya rud'e yana fad'in " kodai nadawo muyi rainon cikin tare ? murmushi tayi cike da kissa sannan tace " basai kadawo ba yallabai na , nafiso kadawo kaga bby boy kawai an haifosa , Alhaji Abba yace " haba Mummyn Sanam ayimin afuwa dai nadawo naganki da ciki , dan inaso naga yadda ciki zaiyi a jikin ki nasan zakiyi kyau sosai , Hajiya Nafeesa tuni tsoro ya cika mata ciki , cikin zuciyat ta tashiga fad'in "ina zanso kadawo ai asirina ne zai tonu mutuk'ar kadawo , maganar sace ta katse mata tunanin datakeyi " yanaji kinyi shuru ko da matsala ne ? da sauri tace " babu matsalar komai Dear kayi zaman ka indai cikine zanyi maka video sa da kuma hotuna in turo maka , murmushi Alhaji Abba yayi sannan yace " shikenan ai daman cikin bayaso nagansa tunda saida ya koreni sannan yazo , haka suka ci gaba da hirar su kafin daga k'arshe suyi sallama.......

*Bayan kwana biyu*
Maryam bata k'ara yadda sun had'u da Sanam ba , itama kuma Sanam d'in bata bin takan su saboda karatun dayasha mata kai , kuma a wannan lokacin Hajiya Nafeesa tayi nasarar samo number Huneed da ta Diyana a wayar Sanam , tana samowa tasamu Maryam ta tura mata tare da ce mata tana jiran ta da kyakkywan result , ....

Maryam tuni ta shiya yadda zatayi aikin batare da tasamu matsala , unguwar su ta nufa sanye da nik'af tana zuwa tasamu wani me shago dake kallon gidan su Diyana , tana zuwa ta d'age nikaf d'in tana duban sa , Deeni yana ganin ta ya washe baki yana fad'in " Hajjaju Maryam ashe kina nan kwana biyu bakya lek'omu , murmushi Maryam tayi sannan tace " Ina nan Malam Deeni yagari ya yan gari inason muyi wata magana in badamuwa , Deeni ya washe baki yana fad'in " ina sauraron ki hajjaju , Maryam ta kalli gefe da gefen Unguwar tasu taga babu kowa sannan tace masa " Diyana tana siyayya agurin kane ? Deeni yayi d'an dum sannan yace " Diyana kullum tana siyayyan Fresh yo guda biyu , wani lokacin ma in bata zo ba da kaina nakan aika mata , wani murmushi Maryam tayi sannan tace " dan Allah inaso kamin wani aiki kafad'i nawa zan biyaka , Deeni yace " wanne irin aiki kenan Hajjaju ? nan Maryam ta d'auko wata k'waya ta bawa Deeni tace " wannan kawai nakeso ka sawa Diyana a cikin lemon datake siya , Deeni ya zare ido kad'a yana fad'in " kinaso nayi kisan kai fa kenan ? Maryam tace " bawani kisan kai da zakayi kawai dai zata d'an bugu na wani lokacin kai kuma zan baka dubu hamsin , Deeni mayen kud'ine shiyasa Maryam tazo wajen sa , dan tasha wucewa tagansa shi da Diyana suna hira ko kuma taga Diyana ta siyo lemo a wajen sa , da wannan tayi amfani da

kuma son kud'in Deeni , take ta curo Dubu Hamsin tabawa Deeni sannan sukayi sallama akan anjima zata dawo inyayi mata aikin , .......

Acan gidan su Sanam itama ansa mata k'wayar bacci a cikin lemon ta , kuma tana dawo wa daga sch taci abinci tasha lemon ba 'ajima ba bacci yayi awon gaba da ita , tuni Hajiya Nafeesa tazo ta kashe wayar Sanam d'in tare da ajiye ta a k'asan filow......

Diyana kamar kullum ta nufo wajen Deeni domin ansar Fresh Yo d'in ta , tana zuwa sukayi wasa da dariya sannan ya d'auko ya mik'a mata , nan tace masa " yanzu kud'in ka sun kai nawa kenan ? yayi murmushi yana fad'in " zan duba list hajjaju ai baki ansa dayawa ba , daga haka Diyana ta ansa ta nufi cikin gida.....

Nan Deeni ya kira Maryam a waya ya sheda mata aiki ya kammalu , Maryam tayi murmushi sannan ta d'au waya takira Hajiya Nafeesa tace " ina fatan Sanam taui baccin da mukeso tayi yanzu ? Hajiya Nafeesa tace " tuni tayi bacci kawai ke nake jira kifara aiwatar danaki aikin , nan Maryam takashe waya tashiga neman number Huneed , sai da ta kira kusan sau uku sannan ta ya d'aga yana fad'in waye ? Maryam ta gyara murya tamkar me kuka tace " K'awar Sanam ce dama Sanam ce tazo gidan mu kuma naganta bata cikin hayyacin ta , sai wani sambatu take dan Allah kataimaka kazo ka maida ta gida , cike da tashin hankali Huneed yace " wacce unguwa gidan naku yake ? nan tashiga yi masa kwatance tiryan tiryan , ...

Yana kashe waya Maryam ta fito daga gidan su ta nufi motar da suka zo da ita , take ta shedawa Fahad abinda ake ciki nan ya shedawa me d'aukar hoto ya fito dan yafara aikin sa , bayan kamar minty 13 sai ga Motar Huneed ta shigo cikin unguwar su Diyana , take Maryam ta lab'e tana kiran number Diyana , tana d'agawa Maryam tagane kwayar da tasha tafara aiki dan wata iriyar magana ta shiga yi , Maryam tace " kifito k'ofar gidan ku Sanam ce inaso muyi magana yanzu , Diyana tana cikin maye tace ganinan zuwa shegiyar Besty ta ashe kina gari , Maryam tuni ta kashe shikuma Huneed yashiga kiran wayar Maryam d'in dan ya sheda mata ya iso.........
[9/27, 10:08] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 38.

'Dagawa Maryam tayi tana fad'in ganinan fitowa , Huneed ya fito daga motar yana gyara tsayuwar sa a jikin motar , baifi minty 2 da tsayuwa ba sai ga Diyana ta fito rik'e da gyale a hannu ta tana had'a hanya , kana ganin ta kasan ba a hayyacin ta take ba saboda yanayin yadda take , Huneed ya tsallako batare da ya kula da yanayin da Diyana take ba , tambayar ta yashiga yi yana cewa "ina Sanam d'in take plss ? tuni su Fahad sunfara aikin d'aukar hoto batare da Huneed ya lura ba , Maryam wayar ta ta d'auko tashiga yin video tana murmushi , Diyana kallon Huneed take tana dafe kanta tare da nazarin tambayar da yayi mata akan ina Sanam , duban sa tayi sannan tace " wace Sanam kuma kaima waye ? mamakine ya cika Huneed to ba itace takirasa tagaya masa cewa Sanam na cikin wani hali ba yazo , gashi yanzu kuma tana ce masa wace ce Sanam , kafin Huneed ya dawo daga tunanin dayake yaji Diyana a jikin sa ta fad'o , da sauri ya rik'e ta tare da fad'in " subhanallah yana dube dube ko zai ga wani a shigar da ita gida , hango su Fahad yayi a tsaye duk da Fahad d'in yasa face mark ya rufe fuskar sa , sannan yasa Glass suna ganin ya kallesu suka yi saurin waske wa suna juyar da fuskokin su d'aya gefen , Huneed jiyayi kawai gaban sa ya fad'i kawai yaji yana zargin wad'an da yagani , Da sauri su Fahad suka shige motar suka gudu dan yadda suka fahimta Huneed yaganesu , Maryam ta maida Nikaf d'in ta tare da nufar wajen da Huneed yake rike da Diyana , da saurin ta take fad'in " Subhanallah meyafaru haka Malam ? Huneed yace " yauwa dan Allah shigar da ita cikin gidan nan wlh bansan meyafaru da itaba take hakan , Maryam na rik'e Diyana tana fad'in " wayyo Allah sannu Diyana muje ciki , Huneed tuni ya tsallaka ya shiga motar sa dan so yake ya gano meyasa mutanan nan suka gudu da suka gansa ? sosai yake gudu amman yarasa hanyar da sukayi , tuni zuciyar sa ta yanke masa akan yaje gidan su Sanam dan ya tabbatar da lafiyar ta , .

Maryam tana ganin tafiyar Huneed tayi saurin kiran Fahad a waya , yana d'agawa tace " ku canza hanya wallahi daga ganin Guy d'in nan ku ya biyo , kuma tabbas yakama ku to shirin mu zai lalace nima yanzu zantaho , tana kashe wayar ta shigar da Diyana cikin gidan su tare dace musu ganin ta tayi zata fad'i a waje , Maryam ba b'oyayyiya bace a gidan su Diyana nan suka

mata godiya tafito tabarsu........

Huneed yana zuwa gidan su Sanam me gadi ya bud'e masa ya shigo , tambayar me gadin yayi Sanam na cikin gidan kuwa ?  me gadi yace " tabbas Hajjaju tunda ta shiga gida haryanzu bata sake fitowa ba , Huneed yace " taje Sch ne yau ?  Me gadi yace " taje  shine tunda tadawo bata sake fita ba ,  nan Huneed ya shige tare da yin parking d'in motar sa ya fito ,  kiran wayar ta yashiga yi sai dai haryanzu a kashe yake jin ta , yana tsaye yana ta kai kawo tare da tunanin meyasa Sanam ta kashe waya yasan dai ba rashin caji ne yasa wayar taje a kashe ba ,  me yi musu aiki yagani ta fito da alamar aiken ta akayi , kiran ta yayi ya ce mata ta kira masa Sanam , jim tayi sannan tace " Bacci take tund'azu  , yanzu ma haka daga d'akin ta nake naje shigar mata da kaya ,  Huneed yayi hamdala jin Sanam na gida tana bacci  ya tabbatar da lafiya take , nan ya shiga motar sa yafara nazarin lallai akwai wata a k'asa , tabbas wani abu ake shirya masa wanda akeso a saka shi a rud'ani , amman dole zai bibiyi number da aka kirasa dan gano ko wacece tayi masa hakan  ........

Tuni su Maryam da Fahad sun dawo gidan sun samu Hajiya Nafeesa tare da hotunan da Video , wata shewa suka shigayi suna dariyar mugunta, Hajiya Nafeesa tace " yau zanyi bacci harda minshari  dan nasan k'arshen Halak'ar su tazo ,  babban burina shine naga shegu biyun nan basa tare da Sanam , wannan kad'ai zaisa komai mukayi mata yakama ta ,  yanzu wannan sabon  sim d'in zaki d'auko ki saita whaspp dashi ki turawa Sanam Videon nan da hotunan , tana ganin su komai zai rikice dan nasan Sanam farin sani tana da kishin masifa , musamman aka abinda takeso dan tasha cemin zata iya rabuwa da kowa akan abinda takeso ,  dariya sukayi su dukan su suna fad'in kice muna da ganin game ,  Hajiya Nafeesa tace " Babban game kuwa , dukan su suka tuntsire da dariya sunajin dad'in muguntar da suka k'ullah ........

*Kundaina Comment Ko*😒🤒🤒
_Kushirya amsa tambayoyi a wajen D.P.O_😎😎 *nagaji da halinku🤨🤨*
[9/27, 10:09] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rikon Me Hakuri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 39.

Sanam sai wajen sallar Magriba ta farka daga baccin datake , wanka ta fad'a sannan tana fitowa tayi arwala dan yanzu sallah bata wuce ta , tana idar da sallah ta shirya cikin wasu kaya marasa nauyi sannan ta sauko ƙasa ....

Bawanda da tasu a cikin palor dan haka ta wuce kitchen , tana shiga ta kunna gas ta ɗora indomie tasa kifin gwangwani sannan ta koma palor ta zauna , tunowa tayi da wayar ta dan tasan yanzu haka Huneed ya kira ta , da sauri ta hau sama tanufi ɗakin ta dan ɗauko wayar , tana ɗaukowa taga wayar akashe take mamaki yaka mata cikin zuciyar ta take tunanin yaushe ta kashe waya ? ko bacci zatayi bata kashe waya sai dai tasa ta a silet , kawai taɓe baki tayi sannan ta sauko ta koma kitchen....

tana zuwa tasamu indomie sa ta ɗora ta dahu , sauke wa tayi ta juye a filet sannan ta kashe gas ɗin tafito ,..
zama tayi kan dinning tafara ci tana danna wayar ta , data ta buɗe take saƙonni suka fara tururuwar shigowa , koda tashiga duba saƙonni rabi duk numbobi ne baƙi da bata san dasu ba , wasu maza ne masu nuna suna sonta wasu kuma mata ne ƴan sch ɗin su , wasu tabasu amsa wasu kuma tayi tsaki abinta , a haka tana tafiya har tazo kan number da su Hajiya Nafeesa suka turo mata saƙo , da har zata wuce sai taga ai kamar pic aka turo mata da kuma video take tashiga tafara buɗewa , suna gama buɗuwa Sanam tayi tozali da hotunan masoyinta abin ƙaunar ta wanda take burin yin rayuwa dashi ta har abada tare da ƙawar ta kuma bestyn ta , wata iriyar zabura tayi tana miƙewa tare dayin zoom ɗin pic dan ta tabbatar , tabbas sune Diyana ce rungume a jikin Huneed kuma a ƙofar gidan su , hannun ta har rawa yake wajen buɗe video dan taga me yake ciki shima , nan ma dai sune a rungume da juna , dama da yake su Fahad sunsa me hoton yayi musu edityn har wata murya yasa musu tamkar sune , Huneed na cewa " Diyana kinji yadda jikin ki yake da laushi tamkar auduga , ita kuma Diyana tace " Allah Babyna dani da Sanam wace kafi jin daɗin jikin ta ? Huneed yace " ina da haɗi ai kinfita komai Baby , tamkar da gaske suke maganar amman duk sharrin edityn ne , dan lokacin Huneed salati yake yadda yaga Diyanan nayi , shine suka saka musu murya tamkar sune suke

maganar , Sanam jiri taji yana ɗibar ta take ta zauna daɓas a ƙasan tayel , duk ac. dake aiki a cikin palor bai hana Sanam yin zufa ba , tuno hawaye suka fara mata zarya akan kuncin ta , cikin zuciyar ta tanajin wani irin ɗaci meyasa Huneed zai mata haka ? duk san datake masa wannan shine tukucin da zai bata kenan ? tabbas tayi nadamar da yadda ta saki jiki take nuna masa soyayya , komai yace da ita batayin musu haka zatayi masa , amman sakamakon da zai mata shine soyayya da ƙawar ta wacce tafi yarda da ita akan sauran ƙawayen ta , Lallai Diyana taci amanar ta amman suje dan kansu daga yau babu ita basu har abada , kuka sosai tashiga yi me ratsa zuciya tamkar zatayi ihu , duk abinda ke faruwa da Sanam su Hajiya Nafeesa suna laɓe suna kallon ta , wata dariya suke ƙasa ƙasa gudun kar taji , sai da sukayi me isar su sannan Hajiya Nafeesa ta nufo wajen Sanam ɗin tana faɗin " Innalillahi My luv meyasa meki haka kike kuka ? Sanam tamkar an tunzura ta takuma sakin kukan batare da tace komai ba , da sauri ta ɗauki wayar tana faɗin " me aka turomiki yasamin ke kuka , tana ganin wannan hotunan tafara salati tare da cewa " wannan ba saurayin nan naki bane Huneed shida Diyana ? kai Sanam kawai ta iya ɗagawa tana sharar ƙwallah , Hajiya Nafeesa tace " wato dama haka suke shiyasa tun farkon zuwan sa banyi na'am dashi ba , to tunda naga kina sonsa shiyasa nima nafara son sa dan inason farin cikin ki , amman ko ranar nan sai da Fahad ya gayamin yagansa a wani hotel shi da Diyana , gudun ɓacin ranki yasa nace yabar maganar banaso kiji , to gashinan kingani da idanunki wallahi sunji kunya azzalumai , tuni Sanam ta miƙe ta haye sama tana kuma fashewa da kuka......

tana hayewa sama su Maryam da Fahad suka fito daga inda suka ɓuya suna dariya , nan suka shiga murna na nassarar da suka samu na raba Sanam da Huneed , kuma da wannan damar zasuyi amfani komai suyiwa Sanam tunda me bata kariyar su musu farraƙu , duk makircin da suke ƙullawa Rabi me musu aiki tanaji , kawai sai dai ta gyaɗa kai tana jimami tare dayin Allah wadai da halin Hajiya Nafeesa.....

A ɓangaren Huneed tunda yasamu kira akan zasu tafi jihar Katsina domin kamo ƴan ta'adda , kwata kwata ji yayi bayason zuwa saboda Sanam , tabbas yanason sanin halin da take ciki , kuma zuciyar sa na gaya masa lallai akwai abinda ake shirya masa shida ita , amman bashi da yadda zaiyi dole zai tafi tunda aikin sane haka , kiran wayar ta yayi har lokacin bata buɗe ba , sosai yake mamakin rufe wayar ta datayi yauɗin , dan ma dai yaje gidan kuma ya samu tabbacin lafiyar ta ƙalau bacci kawai takeyi....

Haka ya shirya tsaf yayiwa Hajiyar sa sallama tare da Hisham , su duka fatan Alkairi suka yi masa sannan ya shige ya tafi cike da kewar gida......

Sai Bayan sallar Magriba ya kira wayar Sanam ta shiga , sai dai har tagama ring ɗin ta ba'a ɗaga masa ba , sosai hankalin sa ya tashi dan yayi mata miss call shida amman bata ɗaga ba , tuni zuciyar sa tankarye tabbas akwai abinda ke damun Sanam , jiyayi tamkar ya dawo gida yafasa aikin saboda fargaba da kuma son sanin halin da Sanam ke ciki , tuni ya kira Hisham yace masa yaje gidan su Sanam dan yagano masa lafiyar ta , Hisham yashiga tsokanar sa sannan yace masa yana gama cin abinci zaije yaga lafiyar ta.....

Koda Hisham yaje bai samu ganin Sanam ba saboda ance masa baza ta samu damar fitowa

ba , kiran Huneed yayi ya sheda masa abinda akace masa a gidan su Sanam , sosai hankalin Huneed ya tashi yakira Mummyn Twins wato Hajiya Maimuna , nan ya gaya mata abinda yake faruwa tun farkon kiran da akayi masa har yaje gidan su Diyana dakuma zargin da yake akan akwai shirin da ake yi akan su , nan tayi shuru tana nazari sannan tace " tabbas akwai abinda za'a ƙulla muku , amman ka kwantar da hankalin ka ka tsaya kayi aikin da kaje insha Allah komai aka ƙullah to tabbas xai kwance , nan ta shiga kwantar masa da hankali tare da ƙarfa fa masa gwiuwa da kuma ƙara tunasar dashi akan yayi addu'a , sosai Huneed yaji kaso tara a cikin goma na daga cikin damuwar dayake yaragu , tabbas Mummyn Twins Uwa ce da kowanne Ɗa zaiyi Alfaharin samun ta , sallama sukayi ya kashe wayar ya koma bakin aiki........

Sanam kuka take sosai a haka bacci ya kuma a wan gaba da ita ,

. Washe gari tana farkawa ta tayi wanka wajen shaɗaya ta sauko da mukullin mota a hannu , lokacin Hajiya Nafeesa tana zaune ita da Maryam suna yin break fast , koda Sanam ta sauko Hajiya Nafeesa ta shiga yi mata murmushi tana faɗin " zonan my luv , Sanam taje Hajiya Nafeesa ta rungume ta tana faɗin ' kicire komai a ranki ki rabu dasu , kinga in kikasa damuwa a ranki to tabbas zaki wahalar da kanki a banza ne su kuma ba ruwan su , ni da zaki birgeni ma da kinfara kula Jaydeen kema dan ki nuna musu kema daman da wanda kikeso , nan Hajiya Nafeesa tashiga turawa Sanam Jaydeen ta ƙarfi da yaji wai dan ta ɗauki fansa , Sanam kwata kwata Jaydeen ba birgeta yake ba dan baya ɗaya daga irin mazan datake so , ganin inbata amincewa Mummyn nata ba zatai ta damun ta , dan haka tace tabata kwana biyu inta huta zata yanke yadda zatayi , tana cewa haka ta fice daga palor zuwa harabar gida, ....

Tana fita tahau motar ta ta nufi gidan su Diyana , tabbas zataje tayi mata rashin mutuncin da bazata manta da itaba a rayuwa........

[9/27, 14:26] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*

*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚

( Domin Marubuta Mata )

✨ (W.W.A)✨

https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

_Alhamdulillah Allah yayi min dawo wa , ina mutuk'ar godiya gareku masoyana ta yadda kuka nunamin kauna tare da addu'oin ku gareni , naga yadda kukayi kewata sosai😊😊 nima nayi kewarku dayawa Allah yabarmu tare_ ❤️❤️🙏🏻🤝

Chapter 40.

Hajiya Nafeesa murmushin samun nassarar raba Sanam da mutane biyun data tsana,

Yanzu tasan komai zatace da Sanam zatayi tunda tarabata da masu zugata, burinta guda d'aya yarage a yanzu shine, taraba Sanam da Mahaifinta Alhaji Abba.....

Sanam na isa k'ofar gidan su Diyana tayi parking din motar ta tafito , tsayawa tayi tana kallon k'ofar gidan tare da tariyo video da tagani a idanuwanta, wani kishine yakuma taso Mata tamkar mahaukaciya haka ta nufi cikin gidan su Diyana....

Tana shiga tasamesu suna zaune suna hira su dukansu a cikin palor, Sanam ko sallama batayi musu ba ta tsaya a bakin k'ofa tanawa Diyana wani mugun kallo, Diyana d'auke da murmushi a fuskar ta tace " 'Yar halak yanzu nagama maganarki , Sanam cike da takaici tace "ai dole kiyi maganata maci amana wacce bata gaji arzik'i ba , duk mutanen da suke zaune a wajen suka shiga kallon Sanam tare da mamakin jin abinda ya fito daga bakinta , Diyana jikinta har rawa yake tana duban Sanam, a hankali ta furta " Sanam ni kike kira da maci amana wacce bangaji arzik'i ba? A fusace Sanam tace " nakiraki da hakan kiyi maganin abun , wallahi Diyana kinban mamaki ashe ked'in fuska biyu gareki , Kirasa Wanda zakiyi soyayya dashi sai Huneed, kuma kinfi kowa sanin matsayinsa a wajena , to anyi walk'iya naganku keda shi dan haka babu ni babu Ku munafukai kawai , tana cewa haka ta juya ta fita hawaye cike a idanuwan ta........
Tabbas Sanam ba iya maganar dataje zatayiwa Diyana kenan ba ,sotayi ta gasa mata maganganu Amman ganin idanun Umman Diyana yasa Sanam takasa, tana fitowa ta koma cikin motar ta zauna ta d'ora kanta kan sitiyarin tasaki kuka me cin rai , duk duniya bata da wata k'awa da suka shak'u kamar Diyana , sannan bata da wanda takeso take mafarkin rayuwa dashi kamar Huneed, Amman meyasa sukayi Mata haka ? ta dad'e tana kuka kafin taja motar ta tabar Unguwar su Diyana......

Diyana tunda Sanam ta fita take tsaye tana maimaita kalmomin data kirata dasu, Umman su Diyana ta dubi Diyana wacce kowa ita yake kallo tace " Diyana me kikayiwa Sanam haka tabbas ba haka take ba dole akwai abinda kikayi Mata , kuma koma meye akan saurayine tunda gashi tafad'a , Hawayen da Diyana take ta Rik'ewa sune suka gangaro kan kuncinta, cikin

muryar kuka Diyana tace "Umma wallahi kwata kwata bansan laifin da take tuhuma ta dashi ba , Umma kinfi kowa sanin halina  bazan tab'a cin amanar Sanam., shuru Umman tayi dan tabbas tasan halin Diyana , bazata tab'a kula saurayin Sanam da sunan soyayya ba , inajin dai so ake arabasu Dan anga suna son junan su da gaskiya , Diyana d'aki tashige saboda kukan da ya kufce Mata ....

Sanam tana tafe cikin motar ta kiran Huneed sai shigowa yake amman ko kallon wayar taki yi , daga k'arshema kashe wayar tayi Dan ko kad'an batason ganinsa, jitayi batason komawa gida tasamu kanta da son zuwa gidan Mumyn Twins wato Hajiya Maimuna mahaifiyar ta....
Hanyar Estate d'in su ta nufa dan tanason inda zata samu Hutu nawani lokacin.....

A b'angaren Huneed kuwa hankalin sa tuni yagama tashi , Kwata kwata yakasa aikin da sukaje yi, Gashi kusan shine jigon tafiya Dan shine babba a gurin kowa umarninsa yake bi, jiyayi yana muradin ganin Sanam a yau basai gobe ba, tuni yafara shirin tahowa birnin tarayya wato Abuja.......

Sanam tana isowa tayi parking tafito tashiga cikin gidan nasu, tana bud'e k'ofar palor wani k'amshi ya bugi hancinta ,samun kanta tayi da lumshe idanunta tanajin nauyin da zuciyar ta tayi yana raguwa,  sallama tayi duk da babu kowa a cikin palor, zama tayi a d'aya daga cikin kujerun da suka k'awata palor ,  banda k'arar ac babu abinda ke tashi acikin palor , tafi minty biyar a zaune saiga Hajiya Maimuna suna sakkowa daga step d'in benen cikin palor, ganin Sanam sukayi zaune tayi tagumi hannu bibbiyu tayi nisa cikin tunani , mamakine yakama Mumyn Twins. Yaushe Sanam tashigo cikin gidan har take zaune a haka ? Suna gama sakkowa ta mik'awa murja twins tace mata " kuje wajen motor ganinan , da yake fita zasuyi dubo Hajiyar ta batajin dad'i , har Murja tafice daga palor Sanam batasan anayi ba,  dafa kafad'ar Sanam Hajiya Maimuna tayi , firgigit Sanam tadawo daga dogon tunanin da tatafi , murmushi ta k'ak'alo kan fuskar ta tana fad'in "Mumy ina wuni ya gida , cike da kulawa Mumy ta amsa tare da tambayar ta su Hajiya Nafeesa, Sanam tace lafiya lau suke , shuru sukayi nawani lokacin kafin Mumy Twins tace "meke damunki haka naga kinyi shuru kina tunani ko akwai wani Abun ne ?  Sanam tayi k'asa da kanta tana wasa da yatsun hannun ta , Mummy tana ganin haka tasan akwai damuwa a tare da Sanam kuma tana buk'atar a rarrasheta , kallon idanunta kawai tayi tagano irin Jan da sukayi saboda kuka, sosai Hajiya Maimuna taji tausayin 'yar ta yakamata , cikin sigar kwantar da hankali Mummy tace " ki hau sama kiyi wanka akwai abinci kid'iba kici sai ki kwanta ki huta , nima zani duba Hajiyar mu batajin dad'i , Amman bazan dad'e ba zandawo tunda ba a kwance take sosai ba ,  Sanam ta amsa da to tare da cewa tayiwa Hajiyar sannu..........
[9/27, 14:27] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 41.

Mumyn Twins na fita Sanam ta mik'e ta haye sama , tana shiga cikin d'akin taji wani k'amshi ya daki hancin ta me saka nutsuwa , komai a gyare tsaf tamkar ba mai shiga cikin d'akin , toilet ta shiga wanda yake agyare tsaf sai k'amshi yake fitarwa , had'a ruwan wanka tayi tashiga tafarayi tana lumshe idanu ,

Acikin kashi d'ari na damuwar yanzu babu arba'in , tabbas ta yadda Uwa Uwa ce ita kad'ai tana samarwa da 'Ya'yanta nutsuwa, kawai yanzu abinda ke damunta shine tunanin Huneed wanda yakasa barin zuciyar ta ta huta , tabbas ko mafarki tayi akace mata Huneed zaici amanar ta to tabbas zata k'arya ta wannan mafarkin , amman sai gashi a gaske abin yafaru wai Huneed d'inta wanda take burin rayuwa dashi shine yake bin k'awarta harda rungumo ta jikinsa, runtse idanu tayi tamkar yanzu take ganin hoton abun.....

Ta dad'e acikin ruwan wanka sannan tayi wankan tafito , kitchen d'in cikin d'akin tashiga dan ta had'a ko ruwan lipton ne tasha, don batajin zata iya cin abinci acikin nan nata , tana dubawa taga akwai ruwan tea a flast da kuma Samosa a jiye itama, d'aukowa tayi tafito ta dawo d'akin ta zauna tafara ci......

Tuni Huneed ya sauka a garin Abuja ko gidan su bai nufa ba ya nufi gidan su Sanam, yana zuwa me gadi ya sheda masa Sanam tafice bata gida, juyowa yayi gidan su Hajiyar sa na

Palor suna hira da me musu aiki Huneed yayi sallama, kallo d'aya Hajiya tayi masa tasan ba lafiya ba , gaishe ta yayi sannan suka gaisa da meyi masu aiki, d'akinsa ya nufa batare daya kuma magana ba ,

Hajiya mik'ewa tayi tabi bayansa dan tasan lallai ba lafiya bace tadawo da Huneed , aikuwa tana shiga tasamesa ko takalmin k'afarsa bai cira ba 'ya kwanta akan gado yayi rubda ciki....

Hajiya tasamu waje gefen gadon ta zauna tayi gyaran murya kad'an , cikin nuna kulawa irin ta mahaifiya tace " lokacin dawowar ka baiyiba kuma naga damuwa akan fuskar ka inason insan meye yake damun Babban Soja , Huneed ya mik'e a Hankali ya zauna yana duban Hajiyar tasa , tabbas bashida wanda yafita a duk duniya , kuma komai zaiyi saiya nemi shawarar ta kuma kome yake damunsa itace tafarko a duniya dayake gayawa , nan take ya sheda mata duk abinda yake faruwa tsakanin sa da Sanam tundaga kiran wayar k'awarta har izuwa yanzu ,
Tamkar zaiyi kuka yace "Hajiyar mu yanzu haka Sanam bata d'agamin waya , wani lokacin ma inna kira wayar kashewa take , shuru Hajiya tayi nawani lokacin sannan ta d'ago da kanta tana duban Huneed , akwana biyu duk yarame ya canza tamkar bashi ba , tabbas tasan Huneed yanason Sanam sosai , dan haka itama take k'aunar Yarinyar duk da bata tab'a ganin ta azahiri ba sai a hoto , dafa kafad'ar shi tayi sannan tace " Tabbas wannan shiri ne aka shirya muku kaida ita , duk wannan abun anyini dan arabaku kuma gashi wad'an da sukayi suna neman yin nasara akan ku , abinda nakeso dakai a yanzu shine kabi komai a hankali zaka kamo bakin zaren , kuma ka zama ja jurtacce kar kabawa mak'iyanku k'ofah da zasu samu nasarar rabaku , yanzu katashi kayi wanka kazo palor kaci abinci sai kakoma gidan nasu ko tadawo yanzu , Huneed ya ya mutsa fuska yana cewa " bazan iya cin komai ba Hajiyar mu mutuk'ar ba Sanam nagani ba , Murmushi Hajiya tayi sannan ta mik'e tana fad'in " lallai Sanam zankamata da laifin horon mu da Yarona datayi , Soja guda yana neman zama sullutu , maza kayi wanka kasameni a Palor inyaso ko zancen nema sai naraka ka , sosai Huneed yasamu saukin damuwarsa , dama duk wata damuwa yana zuwa da ita gaban Hajiyarsu take masa maganin ta , tabbas shima ya yadda wannann shirine aka shirya musu shida Sanam dan A rabasu , amman tabbas zaibi duddugi harya gano wanda yayi musu wannan shirin Sai ya d'an d'ana kud'arsa.....

Mik'ewa yayi yashiga toilet dan shima yanaso yaji sanyi ko yayane ajikinsa,.....

Sanam tana gama shan tea da samosa bacci yayi awon gaba sa ita,..

Mumyn Twins tunda taga jikin Hajiyar ta da sauki sosai take shirye shiryen tahowa gida , Hajiyar ta ta kalleta tace " wai Maimunatu naga sai sauri kike ki koma gida ko Alhaji Abba yau zai dawo ne ? Mumyn Twins jitayi tanajin nauyin cewa Hajiyar ta Sanam ce tazo gidan takeso takoma , Murja me kula dasu Twins ce tace " Auntyn su Twins ce tazo muka barota agidan shiyasa , Hajiya ta yi murmushi tace "Sanam ce kenan tazo gidan naku shine kuma kota biyoku taga jikinan nawa , Murmushi Mumyn Twins tayi sannan tace " da'alama ba zuwan dad'i tayi ba , dan yanayinta yanuna akwai abinda ke damunta , Hajiya ta nisa sannan tace " to maza kutashi

kutafi dan kije kiji meyake damunta , tunda har kikaga tataho gidan ki to tabbas tana buk'atar kulawarki , Hajiya takuma nunawa 'Yar ta yadda zata janyo yarinyar ta jikinta har tadunga nuna mata dai dai, hala sukayi wa Hajiya sallama suka kama hanyar dawowa gida....

Sai Bayan sallar Magriba sannan Huneed yakama hanyar zuwa gida su Sanam , kafin 'ya fito sosai Hajiyar sa tayi masa nasiha tare da kuma k'arfa fa masa gwuiwa akan lallai 'ya jajirce kar asamu nasarar rabasu , dan haka da k'arfin gwuiwar sa ya nufi gidan su Sanam,

Koda yaje megadi yakuma sheda masa har wannan lokacin bata dawo ba , sosai Huneed yashiga mamakin inda Sanam taje haka har wannan lokacin ace bata dawo ba , yasan dai yau babu sch bare ace lacca taje kuma ko shopping taje yaci ace tadawo yanzu , tsayawa yayi jikin motar sa yana danna wayar sa , yafi minty 5 a tsaye ya hangi Fahad da Maryam sun nufo gidan hannu cikin hannu suna wasan banza ,
Huneed kafesu yayi da idanuwan sa yana nazarin su tamkar yanaso yagano wani Abu atare dasu , suna hangoshi suma sai da gabansu ya fad'i , dan yadda yake kallon su tamkar yagane sune suka had'a musu wannan shirin ,
Take suka tsaya suna Diri dirin juyawa su koma , Maryam dabara ta fad'o mata tace " kar mujuya yin hakan zai sa ayar tambaya akan mu , juyowa sukayi suka kama hanyar shiga gidan , da sauri Huneed ya dakatar dasu dacewa " dan Allah kutsaya zanyi magana daku , jikin su har rawa yake suka tsaya cak suna kallon sa , yana k'arasowa yabawa Fahad hannu suka gaisa sannan yace " dan Allah Sanam ina taje ance bata nan ? Wata ajiyar zuciya suka saki atare sannan Fahad yace " gaskiya bansan ina taje ba , sai dai koke Maryam kinsan inda taje ne ? Maryam tace " tun wajen sha biyu tafice na rana kuma bansan ona taje ba , nan Huneed yayi musu sallama yashige yahau motar sa yatafi.....

tunda Huneed yabaro k'ofar gidan su Sanam yasamu kansa da son zuwa gidan Mumyn Twins , yanaso suyi magana itama da ita ko zai samu sassauci a zuciyar sa , hanyar gidan ya nufa duk jikin sa a mace tare da tunanin inda Sanam take , gashi kwata kwata wayar ta bata shiga inyakira ce masa akeyi akashe take , har test ya tura mata amman bashi da tabbacin ma yaje tunda wayar akashe take......

Sanam bayan ta tashi daga bacci ta sauko k'asa tazauna tana kallo , bata dad'e da zama ba su Mumyn Twins suka shigo cikin gidan , sosai Mumyn taji dad'in ganin damuwar fuska Sanam ta ragu sosai , amsa musu sallamar tasu tayi tana musu sannu da zuwa , zama Mumy tayi kusa da Sanam tana cewa " ya gidan dafatan kinci abinci , Sanam tana ansar Twins a hannun Murja tana cewa Mummyn " naci amman yajikin Hajiyar dafatan dai da sauk'i ? Sosai Mumyn taji dad'in yadda Sanam d'in ta tambayi jikin Hajiyar ta , cike da fara'a tace " jikin ta da sauk'i sosai tace tana gaidake kuma yaushe zakije kugaisa ? Sanam tace " zanje insha Allah inkwanar mata biyu , nan Mummy ta mik'e tana fad'in " bari nayi wanka nadawo sai muyi magana , ta mik'e ta hau sama tabar su Sanam tana wasa da Twins abinta tamkar babu abinda

ke damunta.......
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 42.

Mummy wanka tayi sannan ta tada sallar magriba , tana cikin yin addu'a taji wayar ta nayin ring. Bayan ta shafa ta duba Dan ganin me kiran nata Huneed tagani , lokacin wani Kiran yakuma shigowa ta d'aga tare da yin sallama , amsawa yayi cike da bata girma tamkar tana ganin sa , gaisheta tare da tambayar ta twins , Nan tace lafiya lau suke tashiga tambayar sa aikin da yakaisu katsina , Huneed yace"Mummy nifa nataho gida Dan yanzu haka ma ina hanyar zuwa wajenki , Mummy bazan iya aikata komai ba mutuk'ar bana sanin halin da Sanam ke ciki , nakira ta Amman kwata kwata bata d'agamin waya duk nadamu dayawa ,. Hajiya Maimuna tayi murmushi sannan tace "haba Soja kana Captain guda kana wasa da aikin ka , yakamata kacire damuwar Sanam aranka katsaya kabawa k'asar mu tsaro , Huneed yace " Mummy nidai ganinan zuwa sai muyi magana , Allah yakawo ka lafiya ta furta tare da kashe wayar......

Saukowa tayi k'asa tasamu Sanam har lokacin tana wasa da twins, zama tayi tana duban ta sannan tace " kinyi sallah kuwa ? Sanam tace " nayi tunkafin kushigo , Mummy ta gyara

zama sannan ta dubi Sanam tace " inason inji abinda yake damunki dan haryanzu hankalina ya kasa kwanciya da yadda Naga yanayinki ,   Sanam tuni idanun ta suka Fara hawaye , batace komai ba illah kunnawa Mummyn nata videon Huneed da Diyana datayi , tana kunna Mata ta tashi da sauri ta hau sama jin kuka na niyar k'wace Mata......

A can b'angaren su Hajiya Nafeesa kuwa , duniya tayi musu sabuwa kowanne sai nishad'i yake , Maryam ta kalli Hajiya Nafeesa tace " Aunty yakamata infara zuwa awo tunda cikin yayi wata biyu ,  Hajiya Nafeesa tace " kibari nayi magana da likitana komai yace  sai kifara zuwa , Maryam ba haka tasoba sotake kawai Hajiya Nafeesa tadunga bata kud'i tana fantamawar ta , bata rasa ci ba Bata rasa sha ba  sai dai gaskiya Hajiya Nafeesa bata sakin kud'i shine babban matsalar ta ,  suna zaune Kiran Alhaji Abba yashigo wayar Hajiya Nafeesa d'agawa tayi tana wani murmushi , Alhaji Abba yace " uwar biyu yakike ya daren ? Hajiya Nafeesa tawani lumshe ido tana shafa cikin tamkar me cikin gasken tace " habadai Alhajina guda d'aya ma ai ya isa tunda Babbar Yaya tayi mana twins ,  murmushi Alhaji Abba yayi sannan yace " kikasani ko kema ki haifo Mana Twins d'in , Kinga shikenan nahad'a garke babba ,   Murmushi Hajiya Nafeesa tayi sannan tace " to Allah yakawo Mana masu albarka , da Ameen ya amsa sannan yace " Ina shalelena take kwana biyu bamuyi waya ba saboda bana samun lokaci , kuma yau nakirata Amman wayar ta akashe take ,. Hajiya Nafeesa ta tab'e baki tamkar Yana ganin ta tace " Sanam Ni kaina yau kwana d'aya bansata a idanuwana ba ,  da sauri Alhaji Abba yace " kwana d'aya kuma to Bata gidan ne ko Yaya ? Cike da k'osawa da maganar Sanam d'in dayake Mata tace " kasan yanzu kullum sai sunfita yawo da wannan yaron Huneed , Dan nayi Mata magana shine take fushi Dani , kuma bawanda ya lalata Sanam yanzu inba wannan yaron ba , kwata kwata batajin magana duk ta canza halinta ,. Alhaji Abba shiru yayi Yana nazarin maganganun Hajiya Nafeesar ,. Amman meyasa Huneed zaiyi Masa haka ? Ya d'auki amanar 'yarsa yabashi saboda yaga tana k'aunar sa shine zai lalata Masa ita ,  A hankali Alhaji Abba yace " idan Kinga tashigo cikin gidan ki kirani a waya ki had'ani da ita ,  Hajiya Nafeesa da sauri tace " karka kuma had'ani da ita  kasan in kayi Mata magana zata tsaneni sosai tunda tafara yimin rashin kunya ,  kawai idan tashigo zance Mata takiraka kaga daganan sai kasan yadda zaka b'illo Mata da maganar , sosai ran Alhaji Abba ya b'aci yakashe wayar  batare da yakuma cewa komai ba , ....

Hajiya Nafeesa tayi wani shu'umin murmushi najin dad'in nasarar data Fara samu , take ta yanke shawarar bama sai ta kashe kud'inta a banza ba gurin malamai , kawai wannan kissar zatayi batare da ta kashe kud'i ba cikin ruwan sanyi taraba Sanam da Mahaifin nata ,. ....

Mummyn Twins tana cikin kallon videon da Sanam ta kunna Mata taji sallamar Huneed , ajiye wayar tayi tana Masa lale da zuwa ,  ko a fuska bata canza Masa ba ko kuma ta nuna Masa tasan abinda yake faruwa , Dan zuciyar ta bata gamsu da cewa Huneed zai aikata abinda tagani ba , durk'usawa Huneed yayi Yana gaidata ta amsa cike da kulawa da sakin fuska , bayan sungama gaisawa ya zauna kan kujera Yana d'aukar abokin sa ,  wasa yashiga yi dasu Nan Mummy tasa Murja ta had'o Masa abin motsa baki....

Bayan murja ta kawo masa tace Mata ta d'auki su Twins su hau sama gurin Auntyn su ,. Kwata kwata Huneed bai kawo Sanam bace tunda baiyi tunanin tazo gidan ba ,

Bayan Murja ta bargun Huneed ya kalli Mummy yace "Mummy Dan Allah ki kiramin Sanam wallahi ni inna kirata Bata amsamin waya ,. Mummy wallahi bazan iya komai ba mutuk'ar Banga Sanam nasan laifin danayi Mata ba , Mummy tace " inaso ka kwantar da hankalinka indai Sanam ce tana cikin gidan Nan , wata irin zabura Huneed yayi Yana mik'ewa tare da cewa " Mummy Ina take plss inason ganin ta ,. Hajiya Maimuna tabbas ta yarda da irin son da Huneed d'in keyiwa 'Yar ta , kuma batajin zai aikata abinda tagani , kallon sa tayi sannan tace inaso ka nutsu ka zauna bara naje nataho da ita Dan inaso ku dukan ku naji abinda yake damunku dan samun mafita , Huneed zama yayi yana maida numfashi tamkar wanda yayi gasar tsere , mik'ewa Mummy tayi ta nufi sama Dan tahowa da Sanam....

Sanam na kwance kan gadon Mummyn sai kuka takeyi , da sallama Mummy tashiga ta zauna bakin gadon , a hankali ta furta " Sanam inaso kitashi kije ki wanko fuskar ki kisameni a k'asa muyi magana , Bata k'ara magana ba tamik'e tabar cikin d'akin....

Bayan kamar minty 5 da dawowar Mummy sai ga Sanam ta sauko daga sama , kwata kwata bata kula da Huneed ba saboda kanta na k'asa saboda kukan datasha , tunda ta taho Huneed yake kallon ta saboda ganin yadda ta koma duk ta rame kana ganin ta kasan tana cikin damuwa kamar yadda shima yake , .

Tana k'arasowa zata zauna idanun ta suka dira kan Huneed dake zaune ya zuba Mata idanuwan sa , k'irjin tane ya buga take taji ranta ya b'aci tamkar ta juya ta koma Amman hakan tasan bazai samu ba , d'auke kanta tayi daga kallon sa tasamu waje ta zauna tafara wasa da yatsun hannun ta , Mummy tayi gyaran Murya sannan tace " Huneed gaka ga Sanam inaso kufad'amin abinda ya had'aku ku dukan ku , shuru sukayi aka rasa me magana daga ciki , Mummy tace " to shikenan tunda bawanda zaiyi magana Bari intashi in baku guri , yunk'urawa tayi zata mik'e da sauri Huneed yace " Mummy karki tafi zanyi magana , komowa tayi ta zauna batare da tace komai ba ,

Huneed yace " Mummy nidai haryanzu bansan laifin danayiwa Sanam ba , tun Randa nataka naje k'ofar gidan k'awar ta wannan abun yafaru , Nan Huneed ya laburtawa Mummy komai Sanam na zaune tanaji , Mummy tace " tabbas wannan shirine aka shirya muku , kuma gashi anyi nassara akan Sanam d'in sosai , Mummy Nan ta kunnawa Huneed videon da aka turowa Sanam a waya tabashi tace yagani ,....

Huneed Yana Fara kallah ya zabura Yana fad'in " tabbas wannan shirine aka shirya Mana , wallahi Mummy yadda nafad'a muku haka abin yafaru , Mummy tace " basai ka rantse ba Huneed wallahi duk me hankali yaga wannan abun yasan shirine , kuma kowaye yayi muku hakan to tabbas na cikin gidane ,. Sanam shuru tayi tana nazari meyasa zasuce shirine wannan ? Wata zuciyar tace Mata " tabbas shirine ki yarda Sanam taya Huneed da Diyana zasu miki haka ? Kinajin duk abinda Huneed yace ankirasa anfad'a Masa a waya , sai kuma tashiga tunanin tabbas da ta tashi daga bacci tayi mamakin ganin wayar ta a kashe , kenan hakan na

nufin ankashe Mata wayar ne saboda Kar Huneed ya kirata , tabbas itama ta yadda shirine to waye yake Shirin ganin sun rabu ?  Huneed ne ya katse mata tunani da cewa " Mummy zanyi bincike sosai akan wannan al'amarin kubani kwana daya rak ,  Mummy tace " kayi komai a nutse Dan kasan shi mak'iyi Koda yaushe shima cikin shiri yake , sannan inaso kununawa mak'iyan sunci galaba akan ku , Kar ku yadda ku nuna musu kunshirya kuci gaba da takun sak'a , gefe d'aya kuma kuci gaba da soyayyar ku , Nan taci gaba dayi musu nasiha me ratsa zuciya har kowannen su ya gamsu da lallai shirine akai musu Dan anaso arabasu, Sanam sosai tayi Nadama akan abinda taje gidan su Diyana tayi , .....

Mummy tunda taga Sanam tasaki jiki ta mik'e tabasu waje Dan su zanta....

Huneed tamkar me jiran tashin Mummyn yayi saurin dawowa kusa da Sanam , jikin sa har Yana gugar nata yace " Haba Bbyna kin wahalar Dani dayawa fa , kinsa naje yak'i Amman nakasa tab'uka komai saboda tunaninki , Sanam ta d'ago da idanuwan ta da suka sha kuka tana hararar sa ,  Huneed ya kama kunnen sa Yana fad'in "ayimin afuwa Dan bazan iya jurewa fushin My Wifey na ba ,. Sanam ta turo baki tana cewa " bawani Matarka meyasa ka saka Diyana a jikin da Ni kad'ai nakeson mallakar sa ? Huneed yace " taimakonta nayi ganin tana neman fad'uwa , Amman da nasan hakan zai ruguzamin farin cikin mata ta Dana barta tafad'i , sosai Sanam ta yadda da Huneed Dan dama sharrin zuciyane yasa ta yadda da abinda tagani batare da tayi bincike ba, Nan Huneed yaci gaba da lallab'a Sanam tare da yi Mata kalaman soyayya masu kwantar da hankali ,

Sai wajen sha d'aya na dare sannan Huneed yace " zanzo natafi gida Naga dare yafarayi , kuma kiksan yau nadawo kuma inaso gobe tunda safe nafara binciken masu son shiga tsakanina da My Wifey d'ina ,.  Sanam tace " Yana da kyau Dan Nima zanso sanin suwaye suka saka ayi Mana hakan , Mummy ce ta sakko Dan haka Huneed ya mik'e Yana cewa Sanam " zantafi Amman Dan Allah karki koma can gidan yanzu kibari sai bayan kwana biyu ,  Sanam tace " band'auko kayana ba da sauran abubuwan buk'ata ta , sai dai ko gobe naje nad'auko inyaso sai nadawo , Nima kaina Ina bukatar yin nesa da gidan na kwana biyu , sosai Mummy taji dad'in kalaman Yarinyar tata , a zuciyar ta tayi Mata addu'a akan Allah yakuma tsareta  yasa daga haka yarinyar ta tadawo gareta,......

Bayan tafiyar Huneed Sanam da Mummy suka ci gaba da tattauna maganar akan abinda yafaru , Kiran wayar Hajiya Nafeesa ne yashigo wayar Sanam , sai da ta kalli Mummyn ta kafin ta d'aga Kiran , Hajiya Nafeesa tace " My luvly Wai Ina kika shigane yau ? Tund'azu nake nemanki a waya Bata shigowa , kuma na Kira wayar k'awarki itama Bata shiga  Daddyn ki ma yakiraki yace min Bata shigowa Anya lafiya kuwa ?  Sanam tace " lafiyalau Mummy Ina gidan Mummyna shiyasa , kuma wayata akashe take shiyasa Bata shigowa sai yanzu na bud'e , Hajiya Nafeesa cike da son jin abinda Sanam d'in tace tace " wacce Mummyn naki kenan ? Sanam tace "Mummyn Twins  Aman zan kwana  , yanzu zankira Daddyn sai muyi magana dashi sai da safe Mummy , Bata jira me Hajiya Nafeesar zatace Mata ba takatse wayar ,. Hajiya Nafeesa rik'e da waya a hannu tayi saroro tana mamakin canzawar Sanam d'in haka........

*Comment* plss

*'Yar Mutan Kanawa*
_Ce_✍🏻
[9/27, 14:27] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 43.

Hajiya Nafeesa rik'e da waya a hannu sai mamakin irin canzawar da Sanam tayi , tabbas akwai wata a k'asa lallai Hajiya Maimuna ta tashi tsaye , gashi lokaci d'aya Sanam na neman komawa wajen mahaifiyarta , Hajiya Nafeesa ji tayi wani Abu ya tsaya Mata aranta Wanda tarasa gane meye , shin murna zatayi da komawar Sanam haka ko kuma bak'in ciki ? Duk irin yadda ta tsani Sanam da kuma yadda takeson rabata da Mahaifin ta sai data samu kanta da jin kewar Sanam d'in , .....

*Washe gari*

Tun asuba Mummyn Twins ta tashi Sanam tayi sallah , bayan sun idar da sallah  Mummy ta d'auko Hisnun Muslum tafara koyawa Sanam yadda zata dunga yin azkar ,. Sannan ta Gaya Mata fa'idar yin Azkar saboda neman kariya daga sharrin Mutum da Aljan , bayan sun kammala Sanam takoma bacci  saboda ba saba tashi tayi a wannan lokacin ba.,.....

Huneed bayan ya idar da sallar asuba Yana  fitowa daga masallaci ya nufi unguwar su Diyana Dan Fara bincike ,.

Yana zuwa yasamu wajen me saida Drinks ya zauna akan banci ,  Yana zaune har gari ya k'arasa wayewa mutane suka Fara wucewa ,   sai wajen takwas me shagon yazo ya bud'e , sallama yayiwa Huneed sannan ya shiga Yana aikin gyare gyare , Huneed wayar sa ya d'auko yafara danne danne a haka har yagama gyara shagon ya fito ya zauna kan Bencin da Huneed yake ,.  Tunda Huneed ya k'arewa Isma'il kallo yasan lallai Yana da mugun son kud'i , Dan haka yayi amfani da wannan Yanayin nasa yace " Malam inason kamin aiki kuma kafad'i ko nawa kakeso zanbaka ,.

Isma'il ya kalli Huneed da sauri sannan yace " Oga wanne irin aiki kenan ? Sannan taya zanyi maka aiki bansan kaba kawai daga ganinka yau sai inyi maka aiki , Huneed yace " sanina bashida amfani kawai aiki nakeso kamin na Rana d'aya , Amman in bazakayi ba zantafi innemi wani , Huneed na Gama magana ya mik'e Yana shirin barin wajen ,.  Da sauri Isma'il yace " Oga kadawo muyi magana zanyi maka kafad'amin wanne irin aiki zanyi ?

Huneed yayi wani murmushi Wanda shi kad'ai yasan ma'anar yinsa yadawo ya zauna ,.

Duban Isma'il yayi yace " inaso kafad'amin ranar Asabar d'in data wuce  wasu masu motar k'irar Vibe fantia sunzo wajen nan suntsaya,  kalar motar Blue ce  misalin k'arfe hud'u da minty 40 na yamma me suka zo yi unguwar Nan ? Isma'il take yagano su Maryam mutumin Nan yake nufi ,  Nan Isma'il yace " Oga gaskiya bangane me kake Nufi ba ,kuma Ni ranar ma banbud'e shagona ba ,. Huneed yayi murmushi yasa hannunsa cikin aljihi ya zato bandir d'in 'yan dubu dubu guda biyu dubu d'ari biyu kenan , da sauri Isma'il ya Kai dubansa kan kud'in Yana wani lashe harshe tamkar yaga abinci ,. Huneed Yana lura dashi sai yayi kamar baigansa ba yace " Bari natafi wajen wani tunda naga Kai baka buk'ata , dasauri Isma'il yace " Wallahi inaso Oga sai dai gaskiya inajin tsoron abinda zaije yadawo , Dan komai dayafaru a ranar da saka hannu na Amman bansan abinda akayi Mata ba , Huneed ya gyara zama Yana duban Isma'il yace " inaso kafad'amin gaskiyar komai da yafaru Babu abinda zaayi maka , Nan

Isma'il yabawa Huneed labarin yadda Maryam tazo tasamesa akan yasawa Diyana k'wayar bacci a lemo da kuma yadda yaga Maryam d'in tazo da wasu maza guda biyu , komai da Isma'il ke fad'i tuni Huneed ya nad'eshi a waya  , daga Nan Huneed ya mik'e Masa sallama tare da ce Masa yabashi number Maryam d'in ,  Bayan yabashi Huneed ya gargad'i Isma'il akan karya kuskura ya shedawa Maryam zuwan sa , in kuma har yayi hakan to lallai zai hukuntashi , Isma'il yace " hakan ma bazata faruba Oga Nan yabashi kud'in da yayi masa alk'awari tare da barin gurin......

Sai wajen sha biyu sannan Sanam ta tashi tashiga wanka , Mummy nashiga d'akin taji alamar wanka take Nan ta bud'e wordrup ta d'auko mata d'aya daga cikin dogayen rigunan ta

sababbi Wanda ko sawa Bata tab'ayi ba , ajiye Mata tayi akan gadon sannan ta had'a Mata da sabon Pant da breazia ta fita daga d'akin , Koda Sanam ta fito taga wannnan kayan abakin gado tasan Mummy ce ta ajiye Mata , Nan ta nufi kan mudubi Wanda ya cika da kayan shafa kala kala da kuma turaruka masu tsadar gaske ,. Nan tashafa Mai tasa kwalli sannan ta shafa kulacca da had'add'un Humra , rigar ta d'auko tasaka tamkar Dan ita aka siyo tayi Mata cif ajiki , gashi tayi Mata kyau sosai ta fesa turare sannan ta yafa d'ankwalin rigar ta fito daga cikin d'akin....

A falor k'asa tasamu Mummy da Twins sai wasan su suke , Tunda ta taho Mummy ta kafeta da ido lallai jininka jininka ne komai na Sanam irin natane lokacin data na budurwa ,. Sanam na k'arasowa tace " Mummy barka da Rana , Mummy Twins tace " sannu da fitowa , lallai kina Shan bacci da yawa. Haka kikeyi kenan a gidan naku bakya taya Auntyn naki aiki ? Sanam tayi Murmushi tana cewa " Mummy to mezanyi akwai 'yan aiki fa , Mummy tayi Murmushi itama sannan tace "duk da haka Yana da kyau kidunga shiga kitchen kina ganin yadda akeyin aikin girki , inkinje gidan ki ai dole kiyiwa Mijinki girki da kanki , Sanam tace " Mummy shi ma sai yaci na 'yan aikin kawai , Daddy ma girkin 'yan aiki yake ci Dan Mummy Bata shiga kitchen sosai ,.

Murmushi Hajiya Maimuna tayi cikin zuciyar ta tana tuno yadda Alhaji Abba keyi " duk ranar girkin Hajiya Nafeesa saiya ci ya k'oshi a gidan ta sannan yake tafiya , Dan akan hakan sunsha fad'a dashi tace Masa yatafi gidan sa yaje yaci abinci tunda ba girkin ta bane , yakance Mata shi bayajin dad'in girkin kowa indai bana taba , ko tafiya yayi yabar k'asar kullum saiya Mata k'orafin baya iya cin abinci sai su cheefs da coffe ,. Tabbas dole ta tashi tsaye wajen koyawa Sanam girke girke , mutuk'ar mace ta iya girki to ta hau mataki casa'in da tara a cikin matakan zama lafiya da miji ,

Kiran wayar ta da akayi yasa tadawo daga tunani data tafi , d'agawa tayi suka gaisa sa Huneed , Nan yake sanar Mata yasamu nasarar Fara gano Wanda suka musu wannan abun , gashinan Yana hanyar zuwa gidan yanzu haka , Mummy tace " to Alhamdulullah sai kazo , kashe wayar tayi sannan ta dubi Sanam tace " ga Huneed Nan yataho Yana hanya kishiga kitchen keda murja kuyi Masa jallof rice akwai komai a Frizer , Sanam tace " to sannan ta mik'e ta nufi cikin kitchen d'in.....

Hajiya Nafeesa ta dubi Fahad sannan tace " nagaji da halinka na d'aukarmin Motar kufita yawo kaida wannan shegiyar mara galihu , duk inda kukabi indai mutanena sunga motar sai sunkira sunce yanzu na wuce , Fahad yace " Aunty Dan na d'auki motar ki na fita shine abin magana ? to kisa Mijinki ya canza Miki wata sai kibarmin wannan Kinga shikenan , Hajiya Nafeesa ta kalleshi da wani mugun kallo tace " lallai Fahad to ko canzamin motar Alhaji yayi kana ganin zanbar maka wannan ne ? Duk maganganun da sukeyi Maryam na lab'e tana jinsu tunda ga farko , k'ara kasa kunne tayi tanaji Fahad yace " ashe akwai abinda zaki iya hanani Aunty ? Hajiya Nafeesa cike da k'osawa da maganar Fahad tace " Dan Allah kafita Ina buk'atar hutu , tana cewa haka tashige can cikin d'akin ta tabar Fahad tsaye bashi da tacewa , ...

Shima fitowa yayi daga d'akin Yana meyin k'wafa , karo sukaci da Maryam ta kafeshi da idanuwa tana kallon sa , shima ita yake kallo da yimata alamar taji duk abinda suke cewa ? Nan

Maryam tayi Murmushi mugunta sannan tace " naji komai kawai ka k'yaleta zamuyi maganinta kabari na haihu , Fahad yace " haba Merry har saikin haihu ma za'ayi maganin ta kawai ki nemo Mana mafita ,.

Maryam tace " kabani Nan da kwan biyu zan tsara Mana yadda zamuyi Mata .......

Huneed Yana zuwa bayan sun gaisa da Mummy ya kunna Mata Muryar Isma'il wacce yayi record a waya , komai sai da Mummy taji Nan tashiga salati tare da jinjina lamarin , tabbas mak'iyi abin gudune , kuma d'an Adam butulune yanzu ita Diyana da Wanda ta amincewa dashi aka had'a baki aka sa Mata k'waya a lemo tayi bacci , Sanam ce ta fito daga cikin kitchen tana turo baki , Huneed ya zuba Mata muyin idanun sa ko k'iftawa Babu , Mummy ta kalli Sanam d'in sannan tace "lafiya ke kuma kike turo baki haka ? Mummy Wallahi girki akwai wuya nidai kawai kicewa Murja ta k'arasa nagaji dayawa , Huneed ji yayi kamar yatashi ya rungumo ta yadunga juyata a cikin palorn , wani kyau yagani tayi na musamman lallai inyasamu Sanam yagama cika burinsa na duniya ,. Kwata kwata ya manta a inda yake ya kafeta da idanuwa sai kallo yake ita kuma tamkar wacce Bata gansa ba sai wani narkewa take tana zabga wa Mummy shagwab'a , sai da Mummy tayi gyara murya sannan Huneed yadawo sai dai Yana sosa k'eya , Mummy tace " wannan budurwar taka zaka sha fama sosai batason aiki ko kad'an yadda na Fahimceta , Murmushi Huneed yayi sannan yace " Mummy sai anemo Mana masu aiki Dan Nima bana so tasha wuya , Nan Sanam ta zauna kusa da Mummy suka shiga gaya Mata abinda yafaru , take Sanam taji jikinta ya kumayin sanyi akan abinda tayiwa Diyana , Nan suka shiga tattaunawa har number Maaryam da ya anso sai daya Gaya musu , take suka yanke cewar yasa sabon layi yakira number Dan asan yadda za'ayi su kamata , ....

Take Huneed yasa sabon layi a wayar sa ya dannan Number Maryam , sai data kashe ya kuma Kira sannan ta d'aga , Babu sallama Babu komai tace " waye ne yake neman damuna da tsakar ranar Nan haka ? Huneed a hands free yasa wayar Nan ya dubi Sanam da Mummy suka Masa alama da yayi magana ,. A hankali ya furta aminci agareki barka da hutawa sarauniyar Mata ,. Kallon Sanam yayi wacce ta runtse idanu tana kauda kanta gefe , tabbas shima ba haka yaso ba Dan dai kawai Mummy tace yaje Mata da sigar soyayya wannan ne kawai zaiyi nasarar sanin inda take ,. Maryam tace " yauwa barka kadai sai dai bangane waye ba , Huneed cike da jin tsanar ta aransa yace " Masoyine Wanda yake mafarkinki a Koda yaushe , inafata Zaki amshi tayina dan ba wasa nazo ba , Maryam tace " haba Oga banganka ba bansan ya kake ba kawai sai na karb'i tayinka , kabari muga juna sai muyi ciniki inka siya da tsada saina sallama maka , Huneed cike da k'osawa da maganar Maryam yace " ok to a inah zamu had'u Ni a shirye nake ? Maryam tace " kazo ka d'aukeni a Area 11 Estate d'in gidan Makama gida me No. 13 anjima bayan sallar Magriba , tuni Sanam ta zabura tana mik'ewa ta dubi Huneed da Mummy tace " gidan mu fa kenan , anya kuwa wannan tasan me take fad'i kodai mistake address tafad'a ? Mummy shuru tayi tana mamaki to wannan wace yarinya ce haka take neman Yarinyar ta da sharri , tabbas wannan address d'in gidan Hajiya Nafeesa ne to wacece wannan d'in ? Huneed ne yayi magana da cewa " ku kwantar da hankalinku koma wacece yau shirinta yazo k'arshe Dan tabbas saina kamata kuma zata gayawa aya zak'in ta ,. Ai abun yazo da

sauk'i tunda har tayi saurin amincewa Dani komai yazo k'arshe ,. Nan  suka shiga zantawa tare da yin al'ajabi akan wannan abin.....

Maryam tana kwance kan katifa tana Danna wayar ta.  Cikin zuciyar ta tana tunani tagaji da rashin kud'in Nan da take fama dashi  , ta fuskanci Hajiya Nafeesa ba ta Bari aci kud'inta , dole tadunga fita tana barikinta Dan tasaba da rik'e kud'ad'e a hannun ta , Fahad d'in ma bawani kud'i yake samu ba Dan ko sigari in zaisha itace ke siya Masa wani lokacin ,  haka za'a ajiyeta ba'a Bata manyan kud'ad'e tabbas baza ta sab'u ba  Dole ta fita ta nema , addu'a tashiga akan Allah yasa wannan da sukayi wayar me kud'ine sosai yadda zai jik'ata da nera , tasowa tayi tafito palor Dan tasamu abinda zataci , tana fitowa tasamu Hajiya Nafeesa da wata k'awar ta suna maganar ta , Hajiya Nafeesa tace " Wallahi Hajiya Harira tana haihuwa zansa a kasheta. , tabbas indai har nabarta a raye to tabbas barazana ce ga rayuwata ,
[9/27, 14:27] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter     44.

Maryam dake lab'e  tana jinsu take jikinta yashiga rawa , lallai rashin Imanin Hajiya

Nafeesa yayi yawa , tsayawa tayi taci gaba dajin su ...
Hajiya Harira ta nisa sannan tace " hakan kawai zakiyi domin wannan yarinyar mutuk'ar kika barta to sai ta tona Miki asiri , Hajiya Nafeesa tace " ai shiyasa na fad'a miki barin ta tamkar tonuwar asirina ne , Nan suka shiga tattaunawa akan yadda zasuyi da Maryam inta haihu ,...

Maryam tana gama ji ta koma cikin d'akin tana Kai kawo , wato tana haihuwa tagama musu amfani kashe ta zasuyi , to kafin akai ga hakan itama zata tona asirin Hajiya Nafeesa , me take k'aruwa dashi a wajen su Daman kawai kwana cikin ac da kuma cin abincin lafiyayya Wanda tana gidan suma shi takeci ,. Tana da samari kuma suna Mata duk abinda takeso Dan haka me zai dameta , gobe zataje a zubar Mata da cikin jikinta Amman kafin lokacin dole sai tasamo number Alhaji Abba Dan ta Gaya Masa duk irin makircin da Matar sa keyi ,.......

Huneed ya d'auko Sanam ya kawota gida , sai dai bai shiga ciki ba saboda Kar Shirin su ya b'aci ,. Ajiye ta yayi ta shiga Dan tanason d'ebo kayan sawar ta ta dawo gidan Mummy , a yanzu haka hankalinta kwata kwata yafita daga gidan Mummy Nafeesa tafison gidan Mummyn ta , tana shiga masu aikin gidan suka shiga gaidata ta amsa ba yabo ba fallasa .....

Tana shigowa palor tasamu Hajiya Nafeesa ita da Hajiya Harira suna hira ,.Hajiya Nafeesa tana ganin Sanam cike da kissa tafara cewa " oyoyo my luvly Dauther nayi missing d'inki , Sanam tayi Murmushi tana k'arasowa kusa da Hajiya Nafeesa tace " Some 2 U my Mummy , Nan ta dubi Hajiya Harira tahad'e ranta , batason ganin Matar Nan a gidan su duk wani Abu itace ke koyawa Hajiya Nafeesa ,. Hajiya Harira ta yak'e baki tana fad'in " Hajiya Sanam 'Yan Mata ya kike ya karatu ? Sanam batare da ta dube ta ba tace " lafiya sannan ta nufi Sama tana cewa " Mummy Bari na fito Bata jira abinda Hajiya Nafeesa zata ce Mata ba ta haye sama abinta...

Tana hayewa sama Hajiya Harira ta dubi Hajiya Nafeesa tace " wannan yarinyar taki kwata kwata bata da mutunci , kidubi kiga wani banzan kallo data keyimin , Hajiya Nafeesa tayi Murmushi sannan tace " a haka ma Wai kura tayi lafiya tunda wannan shegen yaron ya d'an canza ta , da dane wallahi ko kallo baki ishi Sanam ba ke kinsani , Hajiya Harira tace " hakane kam to Allah ya kyauta , Nan suka canza hira wacce duka akan yadda zasuyi da Maryam ne..,...

Sanam rik'e da Trolly d'inta tafara sakkowa daga kan step a hankali tana yin waya , k'arasowa tayi tana cewa Hajiya Nafeesa " Mummy inaso zankoma Gidan Mummyn Twins inyi kwana biyu ,. Hajiya Nafeesa ta kalli Sanam cike da kissa tace " wanne laifin nayi Miki haka kikeson ki gujeni ? Sanam tayi Murmushi sannan tace " Mummy bakimin komai ba kawai dai inason zuwa , Hajiya Nafeesa tace " shikenan My luv duk yadda kikeso hakan za'ayi , ki gaidamin da Mummyn Twins d'in ki kuma ce musu nayi fushi , Sanam ta mik'e tana fad'in " zasuji Mummy sai munyi waya , Nan ta fice abinta suka ci gaba da waya da Huneed har ta

k'arasa wajen da motar sa take.....

Sanam na fita Hajiya Nafeesa ta d'auki waya tashiga Kiran Alhaji Abba, kukan kissa ta sa Masa akan Wai Sanam ta had'a kayanta tabar gidan , a halin yanzu ma batasan Ina zataje ba Dan a buge taganta tashigo , Alhaji Abba hankalinsa tuni yayi mummunan tashi , Me Sanam takeson ta koma ? Angaya Mata gata wasane da zata zama haka , bai ga laifin taba tunfarko shine ya sakar Mata da yawa shiyasa take hakan , kashe wayar yayi yafara tunanin wa zai Kira , indai ya Kira Mummyn Sanam d'in yasan tabbas saita nuna Masa kuskuren sa akan tunfarko shine me laifi , .

Hajiya Nafeesa tayi Murmushi tana duban Hajiya Harira, itama murmushin tayi tana fad'in " gaskiya kin iya tuggu Hajiyata , Kinga kuwa wannan had'in da kikayi Mata a wajen uban nata zaisa ya tsaneta , Hajiya Nafeesa tayi wata dariya sannnan tace " Kinga yanzu baruwana da fargabar Kar Sanam taganni cikina baya girma , kuma yanzu zamuyi yadda mukeso tunda tayi gaba , ....

Bayan Sanam da Huneed suntafi ya biya da ita ta shopping , sai da ta zab'i abuwan da zatayi amfani dasu sannan ya dawo da ita gida.......

Bayan Magriba Huneed ya shirya cikin shigarsa ta babban Captain ya nufi k'ofar gidan su Sanam , Kiran wayar Maryam ya shiga bugu d'aya tamkar jira take ta d'aga , sallama tayi cike da kashe murya tace " Alhajina kardai kace min har ka k'araso ? Huneed yace " Kinga laifina ai ba'a sanya da zuwa wajen irinku , Maryam tayi Murmushi sannan tace " gani Nan fitowa kabani minty 2 kacal ,. Kashe wayar tayi sannan ta d'auki mayafinta ta fesa turare ta fito , aikuwa tayi sa'a palor Babu kowa tasa Kai ta fita daga cikin gidan baki d'aya , nesa kad'an ta hango motar Huneed tana ganin motar tasan tayi kamun Babban Alhaji tuni ta canza tafiya harta k'arasa ta buga murfin motar , bud'e Mata yayi tashiga tamaida murfi ta rufe tana fad'in " Alhajina gani naso gareka..... Cak bakinta ya tsaya ganin Wanda yake cikin motar , take hanjin cikinta ya hautsina wani zawo ya taho Mata babu shiri.......,.....

_Masoyana littafin_ *NI KO ITA* _haryanzu yana jiranku Kar ku Bari abaku labari , kuyi gaggauwar siyan naku akan farashi k'alilan_, 200

Duk meso yayi magana a wannan Number : 09137064556
[9/27, 14:28] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 45.

Da sauri tafara k'ok'arin bud'e motar ta fice , wata Uwar tsawa Huneed ya daka Mata tuni Maryam tasaki fitsarin dake matse jikinta , Huneed yaja motar da wani matsiyacin gudu yabar cikin unguwar , ...

Gidan da Huneed ya tab'a Kai Sanam farkon had'uwar su lokacin da take rashin jin ta Nan yakai Maryam, Yana zuwa ya kashe motar ya fito tare da zagayawa inda Maryam take ya bud'e murfin motar tare da fincikota , Maryam sai kuka take tana cewa " kayi hak'uri Dan Allah wallahi nadaina , Huneed ya bud'e gidan Yana rik'e da Hannun ta ko kallon ta yak'i yi saboda tsanar ta dayayi , Yana zuwa ya jefar da ita a k'asa sannan ya zare belt d'in jikinsa yafara dukanta , Maryam ihu take tana fad'in " kayi min Rai Dan Allah ka yafemin , Huneed ya tsaya da dukanta ya durk'uso wajen fuskar yace " inaso kifad'amin waye yasa ki shiga tsakanina da Sanam ? Maryam ganin irin dukan da tasha a Hannun Huneed gashi daga ganin sa har kisa zai iya yi , batare da ta wahalar da kanta ba tace " Hajiya Nafeesa itace tasani wallahi , Huneed ya tsaya Yana kallon Maryam sannan yace " ke meye had'in ki da Hajiya Nafeesar ? Shuru Maryam tayi batare da tace dashi uffan ba , aikuwa ya d'auko belt ya Fara Shirin zabga Mata dasauri tace " wallahi bani da had'i da ita kawai dai ni budurwar k'anin tane , Huneed ya mik'e yace " hakan yayi yanzu zanbarki anan dasafe zanzo dole ki fad'amin irin Shirin da kukeyi akan mu , Yana Gama fad'a Mata hakan ya fito tare da janyo k'ofar ya rufe , yanajin Maryam na kuka tana bashi

hak'uri Amman ko waiwayen ta bai yiba ,

Yana fitowa ya shiga motar ya kunnah yabar unguwar , ring d'in waya yaji Yana tashi Nan ya kalli kujerar da Maryam ta zauna , jakarta yagani kuma ring d'in daga ciki yake fitowa , tsayawa yayi ya bud'e jakar ya d'auko wayar , lokacin wani Kiran ya kuma shigowa , number da aka kirata dashi ansa My Fahad , tuni Huneed yagane Fahad ne Dan haka yak'i d'agawa har ta katse, kashe wayar yayi baki d'aya yayi jifa da ita yahau titi ya nufi gida....

Sanam d'aki guda Mummy ta ware Mata Nan ta zuba kayanta a wordrup d'in d'akin , tana kwance tana tunanin yadda zata je tabawa Diyana hak'uri sai ga Kiran Huneed , da sauri ta d'aga tana fad'in " My Sojana barka da wannan lokacin , Huneed ya lumshe idanu tare da cewa " barka kadai My Wifey ya Daren ya su Mummy da Twins d'ina ?Sanam tace " lafiyar su k'alau sai dai muna kewar ka nida su Twins ,
Huneed yace " badan dare yayi ba Dana dawo Nima Dan nakuma tozali da kyawawan 'Ya'yan Mummy , Murmushi Sanam tayi sannan tace " ya kukayi da shegiyar yarinyar Nan ? Huneed yace " da safe ki shirya zanzo na tafi dake wajen da na ajiye ta , a yadda na Fahimta ba iya wannan ne shirinsu ba akwai wani abun a k'asa.
Sanam tace " kamar me kenan ? Huneed yace " a yanzu bazan ce Miki ga Shirin su ba sai dai a gobe inaso inyi Mata abinda komai sai ta fad'a Mana , Amman ta sheda min cewa ita ba 'yar Uwar su Hajiya Nafeesa bace , Ni a yadda na Fahimta ma a unguwar su Diyana k'awarki take , take Sanam ta tuno da ranar da zasu fita ita da Diyana sunfito sukayi karo da Maryam , Nan Diyana tashiga tambayar Sanam meye had'in su da Maryam , Ashe Ashe maganar da Diyana tafara Gaya Mata akan Maryam d'in gaskiyane , Huneed ya katse Mata shurun ta da cewa " Ya kikayi shuru ne ko akwai abinda kike tunani ? Sanam tace " ea akwai Nan tashiga sheda Masa farkon had'uwar su da Maryam ita da Diyana , Huneed yace " gud dole gobe mutaho da Diyana Dan itama inason tambayar ta wasu abubuwan , Sanam tace " kana ganin Diyana zata zo kuwa ? Huneed yace " zatazo Amman sai kinje gareta kin Bata hak'uri sannan , Sanam tace " inhar zan Bata hak'uri ta hak'ura me zai Hana zanje kuma itama dole tamin uzuri , nayi Mata komai ne bisa rashin sani kuma ko itace a irin matakin Dana samu kaina zatayi irin hakan,. Huneed yace " gaskiyane Matar Soja Ashe dai ana kishin Sojan Nan haka , dariya Sanam tasa sukayi sallama akan anjima zai Kira inya yi Shirin bacci , Nan sukayi musayar kalaman soyayya sannan kowanne yakashe waya cike da begen junan su .....

*Washe gari*

Wajen k'arfe goma na safe Huneed ya dira a gidan Mummy twins , tare dashi suka yi break fast suna hira , anan Huneed ya shedawa Mummy duk yadda sukayi da Maryam , Nan Mummy ta jinjina lamarin Hajiya Nafeesa , sai dai batayi mamaki abinda Hajiya Nafeesa tayi ba Dan tafi gaban hakan , Bayan sun kammala Break fast Sanam ta mik'e Dan ta d'auko mayafinta , tana fitowa suka yiwa Mummy sallama suka fita......

Unguwar su Diyana suka nufa Sanam duk kunya ta kamata, sai tunanin yadda zata shiga gidan su Diyana ta had'a idanu da Umman Diyana ,  suna tsayawa a k'ofar gidan Diyana na fitowa zata  tafi sch ,  Nan Sanam ta tuna itama tana da lucture   Amman sai Sha biyu , kwata kwata Diyana Bata lura da Motar Huneed ba , da sauri Huneed ya fito Yana fad'in " barka da safiya Diyana , tsayawa tayi cak tana kallon sa cikin zuciyar ta tana tunanin me yakawo shi wajen ta , ko shima yazo ya ci Mata mutuncin ne kamar yadda budurwar sa tayi Mata , Bata gama tunani ba sai ga Sanam ta fito itama daga cikin motar , Diyana d'auke kanta tayi tana k'ok'arin ci gaba da tafiya ,  da sauri Sanam tasha gaban ta tana me rik'e jakar dake hannun Diyana .........

*Plss kumin afuwa*

*Wlh yau Ina fama da ciwon kai*😢😢😢😢
[9/27, 14:28] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ ( W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter     46.

Diyana tasakar Mata jakar tana k'ok'arin wuceta tabar gun , Sanam tayi saurin k'ara Shan gaban Diyana tana cewa " plss My bestyna kitsaya ki saurareni , Nan Diyana ta tsaya cak

tana duban Sanam , Sanam batace komai ba kawai videon dake wayar ta ta kunnawa Diyana tana cewa " Dan Allah ki kalli wannan video sai ki fahimcine , Diyana ta rik'e wayar tana kallon video take idanun ta sukayo waje , a hankali tashiga furta "Innalillahi wa'inna ilaihi raji'un , da sauri ta kalli wajen da Huneed yake tsaye sannan ta kalli Sanam tace " wallahi bansan sanda wannan Abun yafaru ba besty , Nan Huneed yadubi Diyana yashiga bata labarin duk abinda yafaru , Diyana a mugun fusace ta nufi wajen Isma'il me kanti , Huneed ya dakatar da ita yace " ki k'yalesa Nan da kwana biyu zansa azo akamasa , yanzu in kika Masa maganar zai iya guduwa Dan Kar muka Masa , Diyana sosai ranta ya b'aci da irin abinda Isma'il yayi Mata , wato mutum dai ba abin yarda bane , duk yadda take mutunci da Isma'il Ashe za a iya had'a baki da shi Dan acutar da ita , Nan Sanam ta dafa kafad'ar ta tace " Besty Kinga abinda nagani idanuwana suka rufe har nakasa jurewa sai Dana zo gareki nayi Miki wannan Abun , inaso kiyimin afuwa da abinda nayi Miki Dan nasan ko kece kika ga irin hakan matakin da Zaki d'auka kenan , Diyana ta juyo tana kallon Sanam cike da so da k'auna irin na K'awayen asali , take ta rungumeta tana saka kuka tare da cewa " wallahi ko d'aya banrik'e kiba kawai dama nasan had'amu akeson ayi , Sosai suka burge Huneed dan kana ganin su kasan suna k'aunar junan su da gaskiya , ....

Dukansu suka shiga motar suka nufi gidan da Huneed ya ajiye Maryam ,..

Tunda Huneed ya kaita gidan na yabaro ta Bata sake jin motsin kowa ba , ga uban sauro dake cizonta sai kuka take tana yiwa Huneed Allah ya isa , tunda take bata tab'a kwana a k'ask'ancen cen waje ba sai yau , tana zaune tana kuka tare da tarin tsoro da ya mamaye Mata zuciyar ta har bacci yayi gaba da ita , ....

Acan b'angaren Hajiya Nafeesa kuwa tun jiya suke Kiran wayar Maryam Amman akashe , Fahad yadubi Hajiya Nafeesa yace " Wai bata fad'amiki inda zataje bane ? Hajiya Nafeesa tace " Ina tafad'amin kuwa ni bansan ma bata gidan ba inbanda kagayamin ,. Fahad yace " to kodai gidan su ta tafi ? Kuma indai Maryam zataje gida ai tana sanar min , Hajiya Nafeesa ta tab'e baki sannan tace " wayasani ko zuwa tayi ta kwana da wani gardin , kasan halin ta dan wallahi wannan yarinyar kwata kwata batayi ba , kana ganin ta kasan tana da mugun son abin duniya , Fahad ya dubi Hajiya Nafeesa sannan ya tab'e baki yace " kema ai kina da son kud'i Aunty , tunda yarinyar nan tazo gidan nan baki tab'a Bata kud'in kashewa sai dai inzata Miki wani aikin , Kinga kuwa Dan taje ta kula maza a waje ai ba laifi tayi ba , Hajiya Nafeesa ta gallawa Fahad harara sannan tace " to angaya maka banki ce ni da zan dunga bata kud'i , duk irin hutawar datakeyi a gidan Nan bai yi Mata ba , taci abinci me kyau tasha lemuka masu tsada ta kwanta a waje me kyau to metake buk'ata sama da hakan ? Fahad ya kalleta shima cike da takaici yace " duk wannan abubuwan da kika lissafo ai kud'i Yana gaba dasu , Hajiya Nafeesa a fusace tacewa Fahad "bazan Bata kud'in ba kuyi yadda zakuyi dani , ta haye sama tana sababi tamkar zata kifa ....

Fahad haushine ya kamasa ya furta " kiyi kigama wallahi duk kud'in da kika tara saina k'wacesu ko ta halin k'ak'a , mace bata da aiki sai mugunta tana da kud'i Amman bazata Bari aciba , tsaki yaja yafice daga cikin gidan baki d'aya......

Maryam tana kwance kan tayes duk ta takure saboda sanyin da takeji , jitayi an bud'e k'ofar gidan alamar za'ashigo , dasauri ta mik'e tana kallon hanya aikuwa ido biyu tayi da Diyana da Sanam ,. Jitayi tamkar ta nutse dan shikenan tasan asirin ta ya tonu itakam , Diyana ta tab'e baki tace " banyi mamakin irin abinda kikayi ba dan komai akace zakiyi nasan Zaki aikata , Amman ba laifin kiba ne laifina ne Dana d'auki yadda nabawa Isma'il shikuma yasamu damar cin amanata , Sanam tana k'arasowa ta dubi Maryama kuma a dai dai lokacin Huneed yashigo , durk'usowa yayi Yana cewa Malama Maryam ga abin Kari nakawo Miki kici ki k'oshi sai kibamu bayani akan shirye shiryen da kukeyi keda uwar d'akin naki , take away ya ajiye Mata indomi'e ce aciki tare da ruwan shayi a leda , Maryam tabbas tana jin yunwa Dan da badan haka ba bazata iya cin komai ba a halin datake , Amman itama zataso tafad'awa Huneed duk shirin da Hajiya Nafeesa keyi akan Mahaifin Sanam , tunda itama Hajiya Nafeesar ai ba Amana gareta ba , Nan ta janyo take away tafara cin Abinci hannu baka hannu k'warya , ...

Tana kammalawa tasha ruwan tea sannan ta ajiye sauran data rage , Huneed ya dubeta yace " muna sauraranki kuma mutuk'ar kika b'oyemin gaskiya to tabbas zaki ji ajikin ki , Maryam cike da rawar Murya tace " Dan Allah in nafad'a muku gaskiya Dan Allah kasakeni intafi gida , Huneed yace " in har hakan zai yuwu mazai Hana muna jinki , Nan Maryam ta fara bawa su Sanam labari tundaga farkon had'uwar ta da Fahad har ya zo garin Abuja tare da kuma Kiran ta akan aikin da zatayiwa Hajiya Nafeesa , Maryam duk wani Shirin na Hajiya Nafeesa akan Sanam da Mahaifin ta sai data Gaya musu , sannan ta kuma Gaya musu k'udirin Hajiya Nafeesa nasan raba Sanam da Mahaifin ta har maganar da Marayam taji Hajiya Nafeesa nayi ita da k'awar ta akan kashe ita Maryam d'in sai data Gaya musu , Sanam tuni taji wata iriyar zufa na tsatstsafowa ta jikinta baki d'aya , dukan su bawanda bai girgiza dajin irin Shirin Hajiya Nafeesa ba , .......

💃💃💃 *NI KO ITA* _littafine daya Sha bambam da sauran. Kudai kuyi saurin mallakar naku dan kashe k'wark'watar idanuwan ku ,. Anan zakuji yadda Uwa take tarayya da 'Danta na cikinta tamkar Miji da Mata , kudai Kar kubari yabarku kuyi saurin Mallakar naku akan Farashi 200 kacal_✍🏻

*Domin mallakar naku ku tuntub'i Marubuciyar akan wannan Number : 09137064556 sai najiku*🤝🤝😘

_Taku a ko yaushe_

*Zeee MD*

[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*

_Rik'on Me Hak'uri_

🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 47.

Sanam Hawaye ne yashiga zubowa a kuncin ta , Ashe duk irin yadda Mummy Nafeesa ke nuna Mata k'auna ba gaskiya bane ? Duk tana yin hakane Dan kawai ta shiga tsakanin ta da Daddyn ta , shiyasa kwana biyun Nan in takira Daddy a waya baya d'agawa , yanzu inta kirashi ma akashe ake cemata , kuma tanajin yauma da safe ya Kira Mummy twins , Diyana ce ta dafa kafad'ar Sanam tana cewa " Sorry Bestyna nasan da ciwo ace wacce ka d'auka a matsayin uwa itace zata maka hakan , Amman ki godewa Allah da yasa asirin ta ya tonu tunkafin ta kammala Shirin ta , Sanam cikin muryar kuka tace " me nayi Mata haka takeson shiga tsakanina da Mahaifina ? Duk wata soyayya na nuna wa Mummy Nafeesa , zan iya cewa nafison Mummy Nafeesa akan Mummyna data Haifeni , Daddy ba gatan da baya nuna Mata , kafin yayiwa Mummyn Twins Abu sau d'aya yayiwa Mummyn Nafeesa sau goma , Amman kiduba kiji irin abinda takeson aikata Masa , ta d'auki d'an shege a matsayin d'an da zata ce shine jininsa , Iallai duniyar Nan abin tsoro ce , Huneed ya mik'e tare da cewa " ki share hawayen ki duk abinda ta shuka a yanzu zaizo k'arshe , Sanam tayi wani shu'umin Murmushi tare da mik'ewa tsaye itama tana fad'in " banason Shirin ta ya rushe a yanzu , kamar yadda ta shirya hakan ne zai tafi Amman inaso daga k'arshe wasan ya canza salo ,. .
Huneed ya dubi Sanam da mamakin abinda tace , Sanam itama tana duban sa sannan taci gaba da magana " Maryam inaso kifad'amin nawa ta biyaki kike Mata aiki ? Maryam datayi tsuru tana kallon su duk jiki na Mata ciwo tace " lokacin da zanyi mata aiki munyi da ita zata

bani " 2 million Amman Bata bani ba kawai dubu d'ari biyu tabani shima dan kawai zan Mata aikin rabaku da juna , Sanam tace " inaso kituromin account number ki zansa Miki 3 million kiyi min nawa aikin , Maryam sosai ta girgiza dajin hakan to itakuma wane aiki zatayi Mata hakan? Huneed da Diyana su kansu kallon Sanam suke suna son jin wane aiki zata saka Maryam , Sanam tace " inaso kici gaba da zama a gidan mu , sannan karki kuskura ki nunawa Hajiya Nafeesa nasan komai data ke shiryawa , Abu na k'arshe kuma kiyi yadda zakiyi kishiga jikinta sosai Dan ki jiyomin duk wani shiri da take akaina , kuma ban yadda ko Fahad yasan da wannan maganar ba , yanzu za'a sakeki kitafi sai ki nuna musu accident kikayi tunjiya shiyasa baki kwana a gidan ba ,

Diyana ta kalli Sanam sannan tace " Besty meyasa kikeson yin hakan ? Sanam tayi Murmushi sannan tace " inaso Daddy yazo yakamata da hannun sa , tunda yanzu Daddy ta had'ani dashi komai zance bazai yadda ba , kuma yanzu bamu da hujjar tunkarar ta da wannan maganar , zata iya k'arya tawa tare da sake sabon shiri Wanda ba lallai musan irin Shirin da zatayi Nan gaba ba , dukansu sukayi Na'am da maganar da Sanam tayi , Huneed ya kalli Maryam sannan yace " kinji abinda tace Miki ko ? Maryam da sauri ta d'aga kai Dan tana mugun tsoron Huneed , Huneed ya durk'uso wajen fuskar Maryam yace " inaso kisani mutuk'ar kika sake wannan Shirin namu ya lalace to tabbas saina kashe ki da hannuna kafin ita Uwar d'akin naki takashe ki , Maryam cike da tsoro tace " bazan karya alk'awariba , Nan Huneed ya fito suma dukan su suka fito har Maryam datake d'ingishi ,

A jikin motar suka samu Huneed Yana jiransu , kullo gidan yaje yayi sannan yazo ya bud'ewa Sanam murfin motar , shiga tayi itama Diyana tashiga sai Maryam a tsaye sai muzurai take , wata tsawa Huneed ya daka Mata Yana cewa" ko bazaki tafi ba ne in maidake cikin gidan ? Da sauri tashige motar Dan Bata fatan sake taka k'afarta a k'ofar gidan ......

Huneed sai da suka Kai Diyana har cikin makaranta sannan suka taho , tsayawa sukayi nesa da gidan Hajiya Nafeesa suka sauke Maryam tare dayi Mata Manyan worning akan maganar da sukayi , jikinta na rawa ta amsa da to tayi saurin barin gurin......

Huneed da Sanam tunda suka sauke Maryam kowanne yayi shuru , a haka har suka k'araso gidan Mummy twins , suna shiga suka sameta a palor tana kallo twins duk sunyi bacci , sallama sukayi Mata ta amsa tana cewa " sannun ku da dawowa , Huneed yace " sannu da gida Mummy , yauwa sannu Huneed kungaji da yawa daga ganin ku , Sanam tana k'arasowa ta durk'usa wajen k'afar Mummyn Twins tasaka wani kuka me tsuma zuciya .........

Mummyn Twins Bata hanata ba illah zuba Mata idanuwa datayi tana kallonta , cikin muryar kuka Sanam tace " Mummyna Dan Allah kiyafemin duk iri Abubuwan da nayi Miki , tabbas na aikata kuskure Wanda bansan illar hakan ba sai yanzu , na d'auka duk duniya Hajiya Nafeesa tafi kowa Sona saboda yadda take nuna min gata da kuma yadda take barina inayin yadda nakeso , Ashe duk ba haka bane duk duniya ba Wanda yakaiki Sona Mummyna kece kikasan ciwona kece kika fi kowa k'aunata , nayi nadama akan duk abinda na aikata Miki Dan

Allah ki yafemin Mummy ko nasamu sauk'i a zuciyata ,Hajiya Maimuna cike da so da k'auna ta rungumo 'Yar ta jikinta tana bubbuga Mata baya tare da cewa " kiyi shuru kidaina kuka Ni bantab'a rik'eki araina ba , a Koda yaushe Ina Miki addu'a akan Allah yashirya minke , kuma Koda yaushe kina cikin raina bantab'a ganin laifin kiba akan abinda kikeyimin , nasan komai da kikeyi bayin kanki bane irin tarbiyar da aka baki ce tunfarko ,yanzu Alhmdllh tunda Allah ya amshi addu'ata ya shiryamin ke kindawo hanyar danake son kihau , Allah yayi Miki albarka Sanam Allah yakuma tsaremun ke daga sharrin dukkan abin k'i , Huneed ya amsa da Ameen cike da so da k'aunar Mummyn Sanam , cikin zuciyar sa Yana hamdalar samun sirika ta gari abar alfahari , ......

Nan Huneed ya kwashe komai da Maryam tafad'a musu yagayawa Mummyn Twins ,. Sosai ta girgiza dajin maganar  Bata tab'a zatar abin Nafeesar zaikai hakaba , lallai Allah yanason su tunda gashi ba'aje ko'inah ba Allah yatoni asirin ta........

[9/27, 14:29] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 48.

Har irin Shirin da Hajiya Nafeesar take akan raba Sanam da Daddyn ta sai da

Huneed ya gaya Mata , Mummyn Twins tace " insha Allah bazatayi nasarar hakan ba , inaso ki kwantar da hankalin ki k'arshen makircin tane yazo shiyasa tashirya muku wannan Shirin nata , gashi kuma ta dalilin hakan nata Shirin duk zai wargaje , Nan sukaita tattauna akan irin abubuwan da Hajiya Nafeesar ta ke k'ullawa ,

Sai bayan sallar la'asar sannan Huneed ya yiwa su Mummy sallama tare da sheda musu gobe da Asuba zai koma kan aikinsa , Nan Mummy tayi Masa addu'a tare dayi Masa godiya akan yadda ya jajurce akan lamarin Sanam ,. ..

Sanam har jikin Motar ta rako Huneed Nan suka tsaya , duban ta yayi yace " My wifey zan koma kan aikina Ina buk'atar addu'ar ki , Sanam ta dubesa tana kashe idanu cike da kissa tace " My Soja shigowar ka cikin rayuwata Babban Alkairine , Kai d'in agareni Babban jigone Dan haka addu'ata a Koda yaushe na zama mallakin ka , Ina yi maka fatan Alkairi Allah ya tsaremin Kai a duk inda kake , sannan Allah yarabaka da sharrin Matan zamani , Murmushi yayi ya amsa da Ameen Mata ta Allah ya dawo Mana da Daddy lafiya in turo iyayena a mallakamin ke , rufe idanuwa Sanam tayi tana dariya Nan suka rabu tamkar sutafi tare saboda tsananin k'aunar juna .......

Haka akaci gaba da tafiya kwanaki na shud'ewa , watanni na wucewa har Cikin Maryam ya shiga watan haihuwa , duk wani k'ulli da Hajiya Nafeesa take Maryam na Kiran Sanam ta sanar Mata , har Asirin da tazo gidan Mummyn Twins ta barbad'a da niyar zuwa ganin Sanam , Nan ma Maryam ta sanar da Sanam Dan haka Hajiya Nafeesa na tafiya akasa masu gadi suka wanke gidan tass.....

Daddyn Sanam sai turowa Hajiya Nafeesa kud'i yake tana Masa k'aryar siyan kayan barka , shi ason sa ma soyake ta taho inda yake ta haihu , Amman tashiga tsarashi akan dole ya hak'ura , sai dai yace da zarar ta haihu zai taho gida ayi hidimar suna da shi , ....

Wani magani likitan Hajiya Nafeesa yashiga bata duk jikinta yafara kumbura tamkar me cikin gaske , a cikin satin Maryam tafara nak'uda tamkar batayi , asibiti suka kaita da k'yar aka samu ta haihu Amman tasha wuya sosai , cikin ikon Allah ta haifi d'anta bak'ir k'irin dashi , tamkar Hajiya Nafeesa tasa ihu saboda munin d'an data gani , haka suka ja gefe ita da Harira suka shiga magana , Hajiya Nafeesa tace " yanzu wannan jaririn ta inah yake kama da Fahad ? Shegiyar yarinyar bin mazan ta yayi yawa wallahi , wannan yaron duk Wanda yagansa yasan ba d'ana bane , Babu ta inda zance Yana kama dani bare kuma Alhaji , Hajiya Harira tace " a can d'akin Naga wata mata itama ta haihu Amman kamar naji an cewa Bata motsi , me zai Hana muje muga wanne kalar d'a ta Haifa sai musan abinyi , kinga inyaso sai ki jik'a likitocin Asibitin da kud'i suyi Mana musanye , take Hajiya Nafeesa tayi na'am da shawarar Hajiya Harira suka nufi d'akin da Matar take .....

Sukayi sa'a kuwa d'akin Babu kowa Nan suka ga jaririn ta fari kyakkyawa dashi , Nan suka rik'e baki suna duban juna kafin su fito da sauri suna Hamdala , wata nurse ce tazo zata shiga

cikin d'akin , da sauri Hajiya Nafeesa ta tare ta tana fad'in " kece wacce kika amshi haihuwar wannan Matar ? Nurse tace " nice lafiya kuwa Hajiya ? Nan suka ja ta gefe suka shiga kora Mata bayani akan aikin da suke so su sata , tare dayi Mata tayin kud'ad'e masu tsoka inhar tayi musu aikin , tanajin irin kud'in da suka fad'a take ta amince Nan Hajiya Nafeesa tayi Mata transfer na dubu d'ari biyar akan zata ciko Mata sauran , Nan suka koma d'akin Maryam suka d'auko d'anta  batare da sun yi karo da kowa ba suka kawoshi d'akin Matar Nan , sannan suka d'auki na Matar suka dawo dashi d'akin Maryam , Nan Hajiya Nafeesa ta kwanta a gadon mara lafiya likitan ta har lokacin bai k'araso ba , Yana zuwa yayi Mata wata allura wacce ta maida jikin ta tamkar namasu jegon gaske , dayake likitan shima ba Mai kula bane gashi da son kud'in tsiya shiyasa bai San kalar d'an da Maryam d'in ta Haifa ba ......

Tuni aka shiga gayawa 'yan uwa da abokan arzik'i haihuwar Hajiya Nafeesa , Alhaji Abba baki har kunne yakira waya tare da cewa Yana Nan akan hanya , ..

Koda su Sanam da Mummyn ta suka samu labari take suka shiga dariya Dan wasan yazo k'arshe ,. Mummy Twins Koda tayi waya da mijinta tayi Masa murna na samun k'aruwar da akayi batare da ta nuna komai ba , Nan yake sheda Mata gobe Yana hanya shima dan dole yadawo gida dan taya Hajiya Nafeesa murnar samun haihuwa ,Mummyn Twins tace " gaskiya dai yakamata kadawo Dan kuwa wannan abin murna ne sosai yasamu, abinda ake nema shekara da shekaru Allah bai kawo ba sai yanzu ai dole azo ataya murna ,  Nan sukayi sallama tana duban Sanam suna dariya , lokacin tuni Sanam da Mummyn ta sunzama tamkar k'awaye , duk dangin Hajiya Maimuna babu inda Sanam yanzu Bata shiga , gidan Hajiya kuwa Kakar ta kusan kullum tana hanya  saboda akwai sa'anin ta a Family d'insu kusan kullum suna tare.,...

Sanam tuni ta shedawa Huneed Maryam fa ta haihu , kuma dole yadawo dan a yanzu Maryam tana buk'atar kulawarsu sosai , tunda kaga ta haihu nasan a Koda yaushe zata iya sakawa akasheta ,  Huneed tuni ya had'o kayansa shima ya nufo Abuja Dan wannan wasan k'arshen dole yadawo agama wasan dashi ...........
[9/27, 14:29] Muhammad Karim: [9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚

( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Chapter 49.

Hajiya Nafeesa tuni tabiya kud'i akan a kashe Maryam batare da Fahad yasani ba , Maryam tasha wuya sosai shiyasa ake bata kulawa a Asibitin , ita kuwa Hajiya Nafeesa tuni ta d'auki jaririn da sukayi musanye sunyi gida , Koda Maryam ta farka bataga jaririn data Haifa ba sannan Babu Hajiya Nafeesa , take maganar Hajiya Nafeesa ta fad'o Mata na cewa tana haihuwa zasu kashe ta , da sauri tafara yunk'urin tashi sai dai jitayi jikinta duk ciwo yake Mata takasa motsin kirki ,.

Wani zogi taji a k'asanta Wanda ya tabbatar Mata a wajen haihuwa ta k'aru ,. Nan tashiga neman wayar ta Dan ta Kira Sanam akan ta taimaka Mata , sai dai wayam Babu wayar sai sannan ta tuna tunjiya data Fara cin wuya tayi jifa da wayar , a hankali Maryam ta shiga saukowa daga kan gado tana d'ingisawa , a haka har ta k'araso k'ofar fita wacce tazo bud'e k'yaure tajishi arufe gam , gaban ta ne yafad'i Kar dai ace sun rufeta ne ? Da sauri ta nufi window tana k'ok'arin lek'awa , wasu maza tagani masu zubin arnan daji a tsaye jikin window suna Mata muzurai , da sauri tasaki labule tafara zubar da hawayen ta , tabbas Bata da mafita anan dan basai anfad'a Mata ba tasan wannan Shirin nasu Hajiya Nafeesa ne , jingina tayi da jikin gado tafara kuka tana addu'ar Allah yakawo Mata mafita,.....

Huneed tuni ya iso Abuja cikin shigarsa ta babban Captain , Koda ya k'arasa gida wanka yayi sannan yaci abinci ya fito , Kiran Sanam yayi a waya ya sheda Mata isowar sa sannan yace tafad'a Masa Asibitin da Hajiya Nafeesa take zuwa , Nan Sanam ta gaya Masa yakashe waya ya nufi Asibitin ,...

Tuni gidan Hajiya Nafeesa ya cika da 'yan uwa da Abokan arzik'i , kowa Yana zuwa yi Mata barka da murnar samun haihuwa , Jariri kwata kwata tak'i badashi Wai bayason jagwal gwalo , Yana kan gadon sa na jarirai sai dai a lak'a aga fuskar sa kowa sai fad'in " tubarkallah yaro Yana da kyau , ....

Me jego sai washe baki take tana farin ciki tamkar itace ta haihun , Madara ake bashi saboda itadai ba ruwan nono gareta ba bare tabashi , kuma Koda aka fad'a Mata magungunan da zata Sha Dan tasamu ruwan Nono k'i tayi , bataji aranta zata iya shayar da d'an da ba nata ba bare kuma d'an shege , Kullum cikin bashi Madara take tana fad'awa mutane ruwan nonon har yanzu baizoba......

Acan asibiti kuwa Wannan Matar da su Hajiya Nafeesa suka musanya d'an Maryam da nata itace ta farko , tunda ta farko ta had'a ido da jaririn da ke kusa da ita tasan ba jinin ta bane wannan , da sauri ta mik'e zaune tana k'walawa likita Kira , da sauri Nurse dake kula da ita ta shigo tana tambayar ta lafiya ? Kallon Nurse d'in tayi sannan tace " Ina Babban likita yake ? Nurse tace " Yana office kina buk'atar wani abune ? Tuni ta sakko daga kan gadon ta ta fito daga d'akin , Nurse sai binta take tana fad'in " kiyi a hankali baki Gama jin sauk'i ba fa , Likita Yana cikin office d'insa Yana Zaune Yana waya ta banko k'ofar da k'arfin gaske , da sauri ya kalli k'ofar Dan ganin Wanda ya shigo haka , batayi wata wata ba ta shak'o wuyansa tana fad'in " Ina kukai min yarona ? Wallahi wancan bak'in d'an bashi na Haifa , ko ku fitomin da d'ana konayi k'arar ku , take kuma tashiga kuka tana fad'in " wallahi bazan yadda ba d'ana ko d'umin jikina baiji ba ace arrabani dashi , likitan jikinsa tuni yashiga rawa Yana fad'in " waye ya d'auke miki d'an naki muje aduba cikin Asibitin sai aga ku nawa kuka haihu yau , Fitowa sukayi kuma a dai dai lokacin mijin Matar da 'yan uwan ta sukazo , dama mijin nata da yakawo ta Asibitin sai ya manta wayar sa a gida shine ya koma Dan ya d'auko ya Kira 'yan uwan ta ,...

Suna iso ta tare su da maganar musanya Mata d'an ta da akayi , da sauri suka nufi d'akin da take ciki aikuwa suna tozali da wannan d'a kowanne sai yayi baya Yana salati , tabbas wannan ba d'an Bahijja bane , wannan ce haihuwar ta ta uku kuma duk yaranta kamar su d'aya da Babansu , kuma yaranta Fara rene itama kuma Fara ce wannan yaro kuwa bak'ir k'irin haka yake , take cikin Asibitin ya d'auka akan anyiwa wata Mata musayar Jariri , Nurse d'in da aka had'a baki da ita sai Uwar zufa take tana faman zare idanuwa , Nan take 'yan jarida suka iso Asibitin suka Fara neman labarai .....

Huneed ya iso asibiti yasamu wannan labarin na musanyan yaro , wucewa yayi yafara duba inda yake tunanin samun Maryam ,...

Maryam kuwa taci kuka ta k'oshi tarasa ta yadda zata fita daga cikin d'akin , duk wannan Abu da akeyi na batun musayar yaro batasan anayi ba, jefe jefe tana d'an lek'awa ta window Dan ganin wannan mutanen suna Nan. ....

Wasa wasa k'aramar magana tazama gaske , Dan tuni Asibitin ya cika da mutane anata fad'in " dole likitoci sunsan inda d'an wannan Matar yake , Take Babban likitan ya had'a taro na gaggawa daga kan likitoci har Nurse a Babban office d'insa .,....

Har dare Huneed baiga d'akin da aka kwantar da Maryam ba , Kiran wayar Sanam yayi yace " My Wifey nayi neman duniya Amman bansamu Maryam ba , ko Zaki tuntub'a Mana kiji tana Asibitin ko tana gidan ? Sanam tace " yanzu nazo gidan kuma duk inda na duba Banga

Maryama ba , Amman Dana zagaya baya ta wajen tagar palor naji K'awar Hajiya Nafeesa wato Hajiya Harira tana waya , Koda na kasa kunne naji tana cewa kusan duk yadda zakuyi ku d'auketa daga cikin Asibitin sai kutafi da ita , sannan naji tace " in sun kashe ta su jefar da gawar a wajen gari , tabbas nasan ba kowa za'ayiwa haka ba face Maryam Dan haka tana Nan cikin Asibitin Nima ganinan zuwa , tana gama cewa haka ta fito daga gidan ta hau motar ta ta nufi Asibitin......

Alhaji Abba tuni ya taho tare da tarin siyayyar da yayiwa yaro da me jego , farin ciki yake tamkar ba atab'a Masa haihuwa , tunda yataho ya shedawa Hajiya Nafeesa Nan tashiga gyara jiki da kuma k'ara maida kanta kalar masu jego ka rantse itace ta haihu , ...

Acan Asibiti Sanam na shiga itama ta tadda wannan hatsaniya ta musanyan yaro da akayi , sosai tashiga mamaki tare da ayyanawa a ranta watak'ila ma Hajiya Nafeesa ce suka aikata hakan , haka tashiga cikin Asibitin sanye da face mark tana dube dube , baya ta zagayo aikuwa ta hango wannan k'artin masu kama da arnan daji itama , tana ganin su tayi saurin komawa da baya batare da sun ganta ba , wayar Huneed tashiga Kira tana magana a hankali , Nan ta sheda Masa tana cikin Asibitin daga baya , yazo taga wasu mutane kuma i tadai Bata yadda dasu ba , Nan ya tambaye ta daga wajen Ina kenan ? Nan tashiga Gaya Masa tiryan tiryan har ya k'araso , Yana zuwa shima ya lek'a ya hangosu Nan ya tabbatar da duk yanda akayi sune wad'an da zasu kashe Maryam , Nan take ya Kira yaransa ya sheda musu maza suzo Asibitin Royal hospital su same shi yanzu , Nan yashiga kaiwa da komawa Yana jiran zuwan su , Sanam tace " My Sojana ina shigo naji wata Hayaniya Wai anyiwa wata Mata musanyan yaron data Haifa , Huneed yace " Nima naji wannan Asibitin ai komai akace zasuyi Babu musu zasuyi shi , Sanam tace " wallahi jikina yabani Hajiya Nafeesa ce tayi wannan aikin , Huneed ya dubeta da sauri ta d'aga Masa Kai alamar ea ,. duban ta yasakeyi Yana nazari sannan yace " bazan yi Miki musu ba Dan wanda yasa akashe wani babu abinda bazai iya ba , Kiran yaransa ne ya katseshi suka sheda Masa sun iso , Nan yashiga kwatanta musu ta b'angaren da yake , Nan take suka zagawo suna k'amewa tare da Sara Masa , Dan dukansu shine ogan su cike da girma mawa suke bashi girman sa , Nan Huneed yabasu Umarnin kamo Masa wannan mutanen da aka saka sukashe Maryam , tare suka nufesu har dashi suka kamasu batare da sun ankare dasu ba , Sanam ta lek'a window Nan ta hango Maryam zaune sai sharar hawaye take , Kiran sunan ta tayi da sauri ta jiyo tare da mik'ewa tana jin wani dad'i ya ziyarce ta , zagayowa Sanam tayi suka bud'e k'ofar tare da shigowa d'akin da Maryam d'in take , Sanam ce ta rik'o Hannun Maryam suka fito daga cikin d'akin , Nan taga wannan mugayen mutanen ansaita su da bindugu kowanne Yana durk'ushe akan gwuiwarsa ,.....

Take cikin Asibitin yakuma d'auka ankama wasu 'yan fashi sun shigo zasu kashe wata , nanfa 'Yan jarida suka samu abinda sukeso sukayo caa.. dason jin labari , sai dai kwata kwata Huneed ya Hana ayi magana dasu dan basaso a haska a social media har Hajiya Nafeesa tagani , Koda suka zo wucewa ta wajen Matar dake kuka akan canza Mata yaron da akayi Maryam ta hangi yaron ana ta kallonsa , da sauri ta anshe hannun ta daga na Sanam ta nufi wajen jaririn , tana zuwa ta anshe shi a hannun wata Mata tana fad'in " wannan ai shine d'ana

Wanda na Haifa , aikuwa kallo yadawo kanta yayin da Uwar waccan yaron ta mik'e tana fad'in " to Ina kika kaimin yarona ? Sanam tace ki kwantar da hankalin ki yaron ki nanan kizo muje daga ciki zamuyi magana , take suka shiga wani d'aki suka keb'e Nan Sanam tashiga bawa Matar labarin komai game da Hajiya Nafeesa , takuma shada Mata yanzu zasu d'auki hanya su nufi gidan Hajiya Nafeesa Nan zata anso d'anta , ba'ayi wata wata ba Sanam da Huneed da Maryam tare da wannan Mata suka nufi gidan Hajiya Nafeesa......

Akan Hanyar su ta zuwa suka Kira Mummyn Twins suka sheda Mata komai , Nan itama ta sheda musu Alhaji yadawo dan tund'azu ya sauka kuma yanzu haka Yana gidan Hajiya Nafeesa shima , itama gatana zuwa zasu taho da Hajiya Babba wato Mahaifiyar ta. .....

Diyana tuni ta bayyana itama a gidan Hajiya Nafeesa , tunda suka taho daga asibiti 'yan sandan da mijin Bahijja ya d'auko suma suke biye dasu har suka shigo cikin estate d'in area 11 ......

Hajiya Nafeesa ana zaune a palor sai wani yauk'i take ita ala dole ga me jego , Alhaji Abba na rungume da yaro sai kallonsa yake Yana Murmushi , duban ta yayi sannan yace " nifa haryanzu narasa da wa wannan yaron yake kama , Hajiya Nafeesa jitayi gabanta ya fad'i Amman sai ta dake tace " haba Alhajina wannan yaron ai kana ganin sa anganka , Murmushi kawai yayi Dan bai ga ta inda suke kama da yaron ba , duk yadda yataho Yana d'okin yaron Yana ganin sa yaji bai kwanta Masa Rai ba sab'anin sauran yaran sa , Hajiya Harira ce ta sauko daga sama tana fad'in" kaga iyayen yaro kunsa shi agaba tamkar za'a k'wace muku shi , zama tayi kusa da Hajiya Nafeesa tana fad'in " sonake nazo na wuce gida tunda na kammala Miki komai , Hajiya Nafeesa ta dubi Hajiya Harira tana yi Mata alama da ido ya sukayi da su Goga ? Ta bud'e baki zatayi magana sai ga su Sanam da Mummyn ta da Hajiya Babba da Diyana sun shigo , Bayan su kuma Maryam ce da Bahijja da kuma Mahaifiyar Bahijjar , a zabure Hajiya Nafeesa ta mik'e ita da Hajiya Harira suna kallon juna .........
[9/26, 21:04] Muhammad Karim: *'YAR KISHIYA*
_Rik'on Me Hak'uri_
🤦🏻‍♀️🤦🏻‍♀️

*NA*
*Zee MD*

*WOMEN WRITERS ASSOCIATION*📚
( Domin Marubuta Mata )
✨ (W.W.A) ✨
https://www.facebook.com/106752595253176/posts/107924965135939/

*Bisimillahir Rahamanir Rahim*

Alhamdulillah ! Alhamdulillah !! Alhamdulillah !!!

Chapter 50.

Da sauri Bahijja ta nufi wajen da Alhaji Abba ke zaune rik'e da jariri a hannu , tana zuwa tace " bani d'ana mugaye azzalumai , Alhaji Abba cike da mamaki ya dubi Bahijja sannan ya Kai duban sa ga Hajiya Nafeesa wacce zufa ke tsatstsafo Mata , duk irin yadda na'urar ac. Ke aiki Amman Hajiya Nafeesa gumi take, kafin yayi magana 'yar sanda mace ta shigo tare da nufo Hajiya Nafeesa da ankwa tana fad'in your onder arrest , sai a lokacin bakin Alhaji Abba ya bud'e yafara magana " Wai meye yake faruwa zaku shigo min cikin gida batare da izini na ba kuma kuna neman tafiya da iyalina , 'yar sanda ta dubi Alhaji Abba tace " kabiyomu office duk sai kasamu wannan amsar tambayoyin naka , take suka ingiza Hajiya Nafeesa a gaba zuka nufi fita da ita , Hajiya Harira na k'ok'arin guduwa Huneed ya rik'eta tare da mik'awa 'Yan sanda ita yace itama suje da ita , ...

Koda Hajiya Nafeesa tazo wucewa ta gefen da Maryam da sauri Maryam ta tare ta tace " Allah ya tsareni daga sharrin ki tun lokacin da kika shirya kasheni nake harkance dake , duk wani motsin ki akan idanuwa na kike shiyasa Nima na shirya Miki nawa Shirin , inaso kuma inyi Miki albishir akan duk wani Shirin ki da kikeyi akan Sanam tasan komai , zare idanu Hajiya Nafeesa tayi Maryam tayi wani murmushin takaici sannan tace " ki k'arewa gidan Nan kallo Dan da alama ba lallai ki dawo ba , tuni akayi gaba da Hajiya Nafeesa wacce tuni tafara zubar da hawaye.....

Alhaji Abba har yanzu ganin abin yake kamar al 'amara , Nan su Huneed suka zaunar dashi sannan Huneed ya umarci Maryam data fad'i duk irin Shirin Hajiya Nafeesa da yadda ta kawo ta gidan , Nan Maryam tashiga karantawa Alhaji Abba komai da dukkan irin makircin da

Hajiya Nafeesa ta shirya Masa , Banda kalmar Innalillahi Babu abinda Alhaji Abba ke Mai maitawa ,   Nan aka Kira Fahad a waya akan anasan ganin , dayake baisan komai ba haka ya nufo gidan kansa tsaye...

Sai da ya shigo sannan yaga abinda yake faruwa agidan , Nan Alhaji Abba yasa shi agaba akan shima yanaso yaji komai daga bakinsa ,   Fahad ba yadda ya iya tunda akan kamasu da laifi dumu dumu haka ya gayawa Alhaji komai da Yayar tashi take k'ullawa , wani abun da Maryam d'in ma Bata fad'a ba shi Fahad sai daya fad'awa Alhaji Abba ,   wani jiri Alhaji Abba yaji Yana d'ibarsa daga zaune , da sauri Sanam ta k'arasa tana rik'eshi da sauri , duban ta yayi cike da so da k'auna ya rungumeta Yana kuka , cikin zuciyar sa Yana tirr da halin Hajiya Nafeesa wacce yaji yanzu a duniya ba wanda ya tsana sama da ita , ....

Kukan Maryam ne yadawo dasu daga shurun da akayi , rok'on Alhaji Abba gafara tashiga yi tare da Sanam da kuma Huneed shima ,. Jaririn ta na hannun ta tana rik'e dashi , Alhaji Abba yace " ta tashi taje ya yafe Mata , Nan ta mik'e ta fice Fahad shima yabi bayanta , ....

Suna fita Fahad yadubi Maryam yace " yanzu shikenan haka zamu tafi Babu komai da muka samu ?  Maryam ta kallesa cike da tsana tace " Dan kaga ka Sha shine kake wannan maganar ,  wallahi nayi danasanin had'uwar mu dakai , gakuma d'anka Nan kasan yadda zakayi dashi , Fahad ya kalleta shek'e k'e yace " wannan shegen d'an zan karb'a Abu mummuna dashi ,  Maryam tace " koma dai meye ai jinin kane kuma dole ka anshe shi , wani mari ya sakar Mata tare da Fara zaginta , Huneed Wanda tun fitowar su ya biyo bayan su Yana jin komai da suke fad'a take ya kama Fahad ,  dama Yana so ya hukuntashi shima akan abinda sukayi Masa shida Sanam ,   take yasa aka tafi da Fahad Dan shima abashi horo me tsanani .....
Maryam kuma ta nufi gidan su tare da jaririn ta a hannu.....

*Bayan kwana biyu*
Alhaji Abba yanzu ya d'an samu sauk'in abinda Hajiya Nafeesa tayi Masa ,  ya tattara komai nata da yasani yayi sadarsu , komai na cikin gidan tuni yasa aka kwashe su dan ko kad'an baya k'aunar abinda zai sa yasake tunawa da Hajiya Nafeesa a rayuwar sa , tuni ya rubuta Mata takardar sakin ta kawai so yake yaje police station yakai Mata ,. ...

Tuni anbawa Bahijja d'an ta tare da tsare Hajiya Nafeesa da Hajiya Harira a gurin 'yan sanda ,  nurse d'in da suka had'a baki da ita aka canza Yaron itama ankamota tare da tufe Asibitin gaba d'ayanshi , ...

A can b'angaren su Sanam ransu fess sun rabu da annoba , Mummyn Twins sai k'ara kwantar wa da Alhaji Abba hankali take , ranar da zai kaiwa Hajiya Nafeesa takardar sakin ta Sanam tace zata bishi ,  aikuwa tare suka taho dashi da  Sanam da Twins wad'an da sukayi wayo ,   suna zuwa aka fito da Hajiya Nafeesa wacce saboda dukan datasha har ta canza kamanni ,  Alhaji Yana ganin ta ya kauda kansa cike da wata iriyar tsanar ta ,   Hajiya Nafeesa

tana k'arasowa ta zube kan gwuiwo winta tana fad'in " Alhaji dan Allah ka yafemin wallahi na tuba nadaina komai , Alhaji Abba ya mik'o Mata takardar ta Yana rungume da da Twins , kasa ansa tayi jikinta sai rawa yake tana fad'uwar gaba , tana dubawa kuwa taga dakinta yayi saki kuma har uku Babu batun komowa , rushewa tayi da kuka tana fad'in kayimin Rai Alhaji natuba , ta juya wajen Sanam tana fad'in " Dan Allah kisa baki Daddyn ki ya yafemin , Sanam tayi Murmushi sannan tace " Nafeesa kenan , ke aganin ki Yana da kyau a zauna da wacce zuciyar ta Babu Allah acikin ta ? Har kisan Kai fa kikasa ayi Allah yasa asirin ki ya tonu , duk irin abinda kikayi Daddyna ya yafe Miki sai dai bamason ki k'ara dawowa cikin rayuwar mu , mik'ewa sukayi Alhaji ya dubeta yace " Ina son in Gaya Miki daga yau ko me kama dake bana son k'ara gani acikin rayuwar mu nida iyalina , nagode wa Allah da baisa na had'a zuri'a dake ba , Yana fad'in haka yashige ya tafi shida 'Yayan sa suka bar Hajiya Nafeesa da tarin Dana sani.........

Tuni Aka tura su Hajiya Nafeesa da Hajiya Harira da Nurse virson zaman shekara uku da horo me tsanani ,.....

*Bayan shekara d'aya*

Tuni an saka ranar Huneed da Sanam wata Uku masu zuwa , Diyana itama lokacin aka saka Ranar ta da wani saurayin ta Umar , Soyayya ake zabgawa tsakanin Huneed da Sanam tamkar sukai junan d'aki , lokacin saura wata biyu da sati biyu su Sanam su kammala digree d'in su , kuma a lokacin Huneed yasamu k'arin girma yazama Babban Major ,

Mummyn Twins sai aikin gyara 'yar ta take da kayan Mata , duk wata kunya yanzu ta cire ta janyo 'yar ta jikinta tamkar k'awaye.....

Mummyn Twins yanzu ta ko'inah kulawa take bawa mijinta , dan Bata son Koda minty d'aya tabada k'ofar dazai yi tunanin wata mace bare kuma ya Kai ga aurowa , ...

Alhaji Abba kuwa kwata kwata baya tunanin k'ara wani aure ma , Dan duk wata kula Yana samu a wajen Hajiya Maimunar sa , ....

Koda Sanam tabawa Maryam kud'in da tayi Mata alk'awari k'in karb'a Maryam d'in tayi , sai da Sanam ta takurawa Maryam sannan ta nuna Mata ai ba komai ko jari taja dan ta rik'e kanta , Dan tunda Maryam ta haihu tasamu lalura saboda irin wuyar da taci , tuni Maryam ta tuba tasamu waje d'aya ta zauna tana kula da yaron ta ....

Akwana atashi yau saura kwana biyar bikin Sanam da Huneed Diyana da Umar , tun ranar talata aka fara biki domin biki ne na 'yar gata gaba da baya , Sosai kayi b'arin kud'i Amarya Sanam tasha kyau tamkar ita ta tsara kanta.

Duk Wanda ya d'ora idanuwa akan Sanam bazai so ya d'auke ba , gyara iya gyara tasha shi duk inda ta gifta sai dai kaji k'amshi na tashi ,. Haka sukasha Dinner kala kala da Reception , nera tayi kuka Dan tsayawa fad'in irin kud'in da aka kashe da kuma kyan Ango da Amarya sukai

b'ata baki ne , ....

An d'aura auren aranar lahadi a masallaci dake cikin unguwar Asokoro Abuja , daga Nan Sojoji suka shiryawa Ango da Amarya Babban Reception , anci ansha sannan Sojoji sukayi wasa da bindiga tare da gwangwajewa , ....

Diyana ma a Nan gidan su Sanam akayi komai nata kuma komai tare suke , yamma nayi aka kawo motocin d'aukar Amare , Nan Aka Kai Sanam da Diyana wajen Alhaji Abba yashiga yi musu nasiha me ratsa zuciya , Mummy itama shigowa tayi Nan itama tayi musu nata fad'an tare dayi musu fatan Zaman lafiya da mazajen su , Alhaji Abba ya d'auki mukullayen mota kowacce yabata kyauta , Nan aka fito dasu kowacce aka nufi gidan ta da ita.......

Gidan Sanam dake Unguwar Maitama yagaji da had'uwa , ga Uwar dukiya da ka narka Mata tamkar basa son kud'in ,

Bayan kowa ya watse sai Sanam a bakin gado tana kukan rabuwa da gida , Ango Huneed ne ya shigo cikin d'akin d'auke da Manyan ledoji a hannun sa , Yana zuwa ya bud'e fuskar Sanam Yana fad'in "My wifey wannan kukan ya isa haka Kar ki janyomin ciwon Kai , shagwab'e Masa tayi sannan tace " My Sojana nifah gaskiya komawa gida zanyi dan Ina missing d'in Twins , rungumota yayi jikinsa Yana fad'in " indai Twins ne Nima Ina missing d'insu Amman Wanda Zaki haifomin a wannan cikin naki , shafo cikin yayi Yana Murmushi Sanam ta ture hannunsa tana mejin kunya......

Wanka Huneed ya shiga bayan ya fito itama tashiga tare da d'auro arwala , Bayan sunyi sallah ya gabatar Mata da tambayoyi akan karatun addini tabashi amsar abinda tasani , ledojin da yashigo dasu ya bud'e musu suka Fara cin kajin da yashigo dasu , da k'yar Sanam taci Dan kawai iya su Madarorin kwali ta dunga Sha , suna kammalawa ya d'ebe sauran ya nufi cikin frize da su ....

Brush Sanam tayo sannan tasa wata rigar bacci tare da feshe jiki da turaruka masu k'amshi tabi lafiyar gado , Huneed shima dashi sai boxer da singlet ya nufo gadon ya kwanta , Nan zance ya canza salo Dan tuni Su Ango Huneed aka Lula duniyar da ba'atab'a zuwanta ba , sosai Huneed yayi mamakin samun Sanam a virgin d'inta , Dan ganin irin yadda ta taso idanuwa a bud'e ga tsantsar wayewa da rashin ji sayake tuni ta bayar da jikinta , sai yasamu sab'anin hakan , Dan haka ya shiga Samata albarka tamkar ya had'iyeta ......

*Bayan shekara d'aya*

Tuni su Sanam anzama Manyan Mata , wata irin soyayya suke itada mijin ta Huneed tamkar Laila da Majnun , kullum suna tare ko dama tuni yadaina zuwa ko Ina saboda yanzu yaxam Babba , Koda yaushe Yana tare da Matar sa musamman yanzu da take laulayin ciki .....

A can b'angaren Hajiya Nafeesa kuwa ansako su duk ta rame ta lalace saboda bak'ar wuyar da suka Sha ,  tun a cikin virson suka rabu da Hajiya Harira baram baram , Dan haka suna fitowa kowacce ta kama gabanta , Hajiya Nafeesa da k'yar tasamu kud'in motar da ta koma can garinsu meduguri ,  Koda ta koma tuni sun samu labarin komai akanta a wajen Fahad Wanda ya dad'e da komowa gida ,.

Tunda ta koma take fama da cutar tari , daga k'arshe aka gane ta kamu da tarin tv Dan haka 'yan uwa kowa ya gujeta , dama data na gidan Alhaji Abba bawani zumunci take ba ko ganin su ba zuwa takeyi ba bare ta tallafa ,shiyasa kowa ya gujeta da k'yar take samun abinci so d'aya a Rana  ,........

Cikin Sanam Yana isa haihuwa ta haifi Santalelen yaron ta me kama da Babansa , ranar suna yaci sunanan Mahaifin Huneed suke Kiran da da Abeeh , sosai aka Sha hidima lokacin itama Diyana ta haifi yarinyar ta data saka Mata sunan Besty ta Sanam , suke ce Mata Uktee , Hajiya Maimuna tuni suka  koma can k'asar Paris ita da Alhaji Abba da Twins , lokacin tana mak'ale da cikin ta k'arami Wanda keta tsokanar ta da cewa " 'Ya na haihuwa uwa nayi , ....

Zaman lafiya da kwanciyar Hankali tsakanin Sanam da Mijin ta Huneed sai abinda ya k'aru , Koda yaushe in suna zaune sai Huneed ya tsokani Sanam farkon Had'uwar su shida ita data fesa Masa ruwan tab'o , Nan zasuyi dariya yace " aini ruwan tab'o Yayimin Rana tunda ya mallakamin wacce ba kowanne namiji ne zai sameta ba sai me sa'a , Nan Sanam tayi Murmushi tace " Nima Ina godiya da samun gwarzon Namiji jajurtacce Wanda ko wacce mace take burun samu ,  Alhamdulillah Allah ya kuma tsaremin Kai mijina Abin k'auna ta Uban 'Yayana kuma My Sojana,.......

*Alhamdulillah*

*Anan nakawo k'arshen wannan littafin ina rok'on Allah kuskuren danayi a cikin sa ya yafemin🙏🏻🙏🏻🙏🏻🙏🏻 Allah yasa ya amfani al'umma baki d'aya*

_Nagode sosai Masoyana da yadda kuka dunga bibiyata🥰🥰🥰 har nakawo k'arshen wannan labari_

✍🏻✍🏻✍🏻✍🏻 *Kubiyoni a sabon Book Dina me suna*
_Bazawara CE_